# Magana Jari Ce



Littafi Na Biyu

# Magana Jari Ce 2

# Magana Jari Ce 2

Alhaji Abubakar Imam, C.O.N., O.B.E.

NNPC

NORTHERN NIGERIAN PUBLISHING COMPANY
ZARIA

***Mallaka*** Ⓜ Kamfanin Gaskiya Zaria 1945

Ba a yarda a kwafi wannan littafi ba, dukkansa ko sashinsa don bugawa ko sa wa a ko wace irin na'ura, sai an sami iazini a rubuce.

*An fara bugawa 1937*

*An sake bugawa sau 17 daga 1954 - 1985*

*An sabunta 1993, 1999*

***AN SHIRYA A***

Kamfanin Litattafai Na Nijeriya Ta Arewa

Lambar Gidan Waya 412,

Kamfanin Gaskiya, Zaria.

**ISBN: 978 — 169 — 058**

*An Buga A*

Kamfanin Gaskiya, Zaria.

# Labarun Da Ke Ciki


| | *Shafi* |
|---|---|
| Magana Jari Ce | 1 |
| Yaro, Tsaya Matsayinka, Kada Zancen 'Yan Duniya Ya Ruɗe Ka | 6 |
| Ba Ruwan Arziki Da Mugun Gashi, Wanda Allah Ya Ba Haƙuri Ya Fi a Zage Shi | 9 |
| Labarin Kalala Da Kalalatu | 15 |
| Labarin Yusha'u Na-Narimi-Dutse-Ba-Ka Fargaba | 18 |
| Mara Gaskiya Ko Cikin Ruwa Ya Yi Jiɓi | 23 |
| Ba Gaskiya Ba Ce A Bar Biɗa Ga Shari'a, Kai Dai A Samo Sa'a | 26 |
| Labarin Sarkin Noma Da 'Ya'yansa | 30 |
| Da Muguwar Rawa Gwamma Kin Tashi | 36 |
| Labarin Jimrau Ɗan Sarkin Noma Na Biyu | 41 |
| Labarin Wani Makaho | 45 |
| Labarin Kosau Ɗan Sarkin Noma Na Fari | 50 |
| An Ki Cin Biri, An Ci Dila | 56 |
| Gamuwar Kosau Da Jimrau Da Nomau | 60 |
| Jarrabawar Da Aka Yi Wa Sarkin Ɓarayi Nomau | 66 |
| Labarin Waɗansu Maɗinka Guda Uku | 75 |

Kuda Wajen Kwaɗayi A Kan Mutu 79

Yaro Bari Murna Karenka Ya Kama Zaki 83

Kukan Kurciya Ma Jawabi Ne, Mai Hankali Ke Ganewa 90

Labarin Wani Sarki Da Yaronsa 92

Zatin Nema Ba Ya Kawo Samu 96

Allah Na Taimakon Wanda Ya Taimaki Kansa 100

Labarin Ja'iru Ɗan Sama Jannati 104

Labarin Waɗansu 'Yan Kama Da 'Yan Sama Jannati 113

Labarin Sarkin Farisa Da Wani Bahindi 121

Labarin Waɗansu Samari Su Uku 128

Kama Da Wane Ba Wane Ba Ne 132

Labarin Kamaruzzaman Ɗan Sarki Shahruz-zaman 138

Labarin Amjadu Da Asadu 150

Kyale Maƙetaci Ya Yi Ta Halinsa, Kome Ya Jima Zamani Na Nan 168

In Maye Na Da Hankali Ba Ya Fid Da Maitarsa A Fili 175

Iya Gani Iya Kyalewa 179

Rana Ta Karshe 184

## GABATARWA

Wannan littafi, 'Magana Jari Ce, 2', yana cikin littattafai guda uku da Alhaji Abubakar Imam ya rubuta a cikin wata shida na zamansa a Zariya a shekarar 1936. Dalilin zaɓo shi kuwa ya rubuta waɗannan littattafai shi ne ya shiga wata gasa ta rubutun littafi a shekarar 1933 ya kuma ci nasara da littafinsa na farko 'Ruwan Bagaja'.

An haifi Alhaji Dr. Abubakar Imam, O.B.E; C.O.N.; LL.D (Hon.) N.N.M.C. a shekarar 1911 a cikin garin Kagara sa'an nan tana cikin lardin Kwantagora, yanzu kuwa Jihar Neja. Ya yi makarahta a *Katsina Training College* kuma ya kama aikin malanta a Makarantar Midil ta Katsina a shekarar 1932. Yana da shekara 22 ya rubuta 'Ruwan Bagaja'. Ganin ƙwazonsa wajen ƙaga labari mai ma'ana ya sa Dr. R.M. East shugaban Offishin Talifi na Zariya ya roƙi a ba da shi aro daga Katsina ya yi aikin rubuce rubuce a Zariya.

Bayan ya koma Katsina aka bi shi da roƙon ya ƙara rubuta wasu littattafan. A can ya rubuta 'Karamin Sani ƙuƙumi' cikin 1937. A cikin shekara 1938 sai Gwamnan Kaduna ya roƙa a dawo da Imam Zariya a koya mashi aikin edita ya zama editan jaridar farko ta Arewa. Shi ne ma ya raɗa mata suna 'Gaskiya Ta Fi Kwabo' aka fara bugawa a watan Janairu na shekara 1939.

Ya yi shekara 12 yana wannan aiki na edita har ma ya rubuta wani littafi a lokacin 'Yaƙin Duniya Na Biyu' watau 'Yaƙin Hitila' da ya ba suna 'Tafiya Mabuɗin Ilmi'. Wannan littafi ya ba da labarin tafiyarsa tare da wasu editoci na jaridun Africa ta Yamma zuwa Ingila a jirgin ruwa a shekara 1943.

Wani mashahurin littafi kuma da ya rubuta shi ne 'Tarihin Annabi da na Halifofi' wanda aka fara buga shi a shekara 1957 lokacin nan yana shugaban Hukumar Ɗaukar Ma'aikata ta Nijeriya ta Arewa.

Alhaji Dr. Abubakar Imam shi aka fara naɗawa Kwamishinan Jin Kararakin Jama'a a shekara 1974 a Jihar Kaduna, lokacin ana kiranta Arewa ta Tsakiya. Ya rasu yana da shekara 70 a duniya ranar Juma'a 19 ga watan Yuni, 1981.

Alhaji Abubakar Imam ya riƙa cewa wannan aiki da ya yi, na talifin 'Magana Jari Ce' ya yi masa amfani ainun. Ya kan ce wannan aiki shi ne ya ba shi damar zama tare da mashahurin Baturen nan na talifin Hausa, Dr. R.M. East, O.B.E. Ya ce daga gare shi ne ya koyi duk ɗan abin da ya koya na game da talifi.

Abin mamaki, shi kuma wannan Bature, Dr. East O.B.E., a wajen 'Muƙaddamar' da ya yi da Turanci tun farkon buga 'Magana Jari Ce', ga abin da ya ce: 'Muna godiya ga En'e ta Katsina, saboda taimakonsu, da hangen nesa da suka yi, har suka yarda,

suka ba mu aron Malam Abubakar Imam. Suka yarda, ya bar aikinsa, na koyad da Turanci a Midil ta Katsina, ya zo nan Zariya, ya yi wata shida domin ya taimake mu, mu sami wadannan littattafai a cikin harshensa.

'Iyakar abin da mu ma'aikatan wannan ofis muka yi, na game da talifin wadannan littattafai, shi ne aiki irin na ofis, na shirya al'amuran, yadda suka kai har aka buga su. Ban da wannan sai su kuma taimakonsa da muka yi na tattara masa littattafai iri iri, don ko zai kwaikwayi wani samfur. Sai fa kuma wajen shiryawa bayan da ya rubuta.

'Kai, in dai har muna da wani abin da za mu yi kirari mun yi, game da talifin waɗannan littattafai, to, babban abin kirarimmu kawai, shi ne yadda muka yi har muka binciko wannan malamin talifi'.

1982 N.N.P.C.

# Magana Jari Ce

A cikin littafi na ɗaya mun bar Sarki Abdurrahman ɗan Alhaji da Wazirinsa Aku suna cin duniyarsu.

Ana nan, labarin Waziri Aku ya bazu cikin ƙasashe, ko ina ka raɓa sai ka ji ana zunɗen Sarki Abdurrahman kan wautar da ya yi ta naɗa tsuntsu Waziri. In mutanen wata ƙasa suka gamu da na ƙasar Sarki Abdurrahman, sai ka ji suna yi musu ba'a, suna cewa, "Yanzu fa a ƙasarku mutum ba shi da ikon ya ce aku ƙuturu, da mutum ya ce haka sai a yanka shi ko?"

Mutanen ƙasar kuwa in sun ji ana yi da Sarkinsu kan haka sai su ce, "Mu muka san abin da Wazirimmu ke ciki, ku labarinsa ku ke ji kawai. Mu mun haƙiƙance, bari ta Wazirci ko Sarki in an yi masa ba laifi ba ne. Mu da Sarki ba shi da ɗa, aradu, in ya mutu akun nan za mu zaɓa mu naɗa. Liman kaɗai ne ba mu iya yi masa, don tsuntsu ba ya yi wa mutane salla ba. Ba ƙarfi ba ne Sarki ko? Kun san don ƙarfi dai mutum guda ba ya iya mulkin mutane dubbai. Abin da a ke so ga Sarki dai na ce ko hikima da fasaha da adalci? To, Wazirimmu ya shafe kowa nan kusa kusa." In sun tsaya da faɗa haka sai a ƙyale su.

To, yamma da ƙasar Sarki Abdurrahman akwai wata ƙatuwar ƙasa ta wani Sarki wai shi Jama'anu, Sarkin Sirika, watau wanda Alhaji Imam ya ba da labarinsa a cikin wani littafi da a ke kira Ruwan Bagaja. To, wannan Sarki na Sirika babban amini ne ga Sarki Abdurrahman. Ana nan, da labari ya kai masa na yadda abokin nan nasa ya naɗa Aku.

Wazirinsa, ya tambayi dalili, aka ce wai don akun ya ba shi labari masu daɗi.

Sarkin Sirika ya ce, "Labarai! Haba, ko kuwa dai wani abu?"

Masu ba shi labarin suka ce, "Labarai fa kaɗai suka sa ya yi masa Wazirci, har ya sa nasa Wazirin cikin jaka ya jefa cikin kogi, don shi bai iya ba da labari ba.

Da Sarkin Sirika ya ji hakanan sai ya yi salati yana tafa hannu, ya rasa ma abin da zai ce don haushi, sai ya ɗauki alkalami ya sami takarda ya rubuta haka:

"Daga Sarkin Sirika Jama'anu, zuwa ga aminina, masoyina Sarki Abdurrahman ɗan Alhaji. Gaisuwa mai yawa da so da yarda.

"Amma bayan haka na ji wani labari wanda ya ɓata mani rai matuƙa. Ina shakka ko gaskiya ne, ko kuwa shakiyancin mutane dai ne. Na ji wai ka fid da Wazirinka, ka naɗa aku. In gaskiya ne ka fid da shi yau, ka murɗe wuyansa tun duniya duka ba su ƙare da ji ba. Yanzu yaya muna cikin hankalimmu, duk duniyan nan, kudu da arewa, gabas da yamma, mu a ke shayi, sa'an nan a ji wai don son jin daɗaɗan labaru har mun naɗa Aku Waziri! To, me aka yi aka yi aku, balle labarinsa? In don labari ne, bari ta nan ƙasar, duniyan nan ma duk akwai wani akun da ya fi wanda na ke kiwo iya ba da labarai? Aku kome iya ba da labaransa, ai iyakar abin da za a nuna masa shi ne a sa bawa guda ya riƙa lura da shi kada kyanwa ta murƙushe shi. Amma a yi wa aku Wazirci! Haba, wasa hauka ne? In dai don nishaɗi ne irin namu na Sarakuna ya sa ka yi wannan abu to, wannan nishaɗi bai yi ba. A sake tun da wuri.

"Kuma ma, in don ba da labarai ka naɗa aku Waziri, amaryar wata ina nan tafe da akuna, mu zo a gwada su, ya kunyata Wazirin naka cikin taro, sa'an nan mu ga shi kuma abin da za ka naɗa shi. Na san sai ka yi murabus, ka ba shi sarautar ya ci, watau ya zama da Sarki da Waziri duk tsuntsaye, kai kuwa ka zauna su riƙa ba ka labari kana dariya! Wannan abu naka na ba ni mamaki. Mutum dai in da ransa kome yana gani.

Wassalamu."

Da aka kawo wa Sarki takardan nan ya karanta, sai ya yi murmushi, ya miƙa wa Wazirinsa Aku, shi kuma ya sa tabarau ya karanta, sai ya bushe da dariya, ya ce, "Allah Sarki! Ashe Sarkin Sirika, duk tsufan nan nasa, har yanzu bai san ƙarfe duka ƙarfe a ke kiransa ba, amma ko cikin ƙarafa akwai zinari da azurfa? Rubuta masa, Allah ya kai mu amaryar watan. Amma ka ce na ce a gaya masa



in zai zo ya karɓe mabuɗan taskar kuɗinsa da ya ke ba uwargidansa ajiya, ya ƙulle taskar, ya zo da mabuɗan. Kuma ya hawo danda ya zo da shi, kada ya bar wa ɗan, kome nacewar da ya yi. Kuma da zai bi shawarata, baƙon nan Dogon Yaro, wanda ya kawo caffa gare shi watan jiya, ya sallame shi tun da wuri, kada ya yarda ya ja shi a jika, har ya san asirinsa.'' Sarki ya rubuta, aka aika wa Sarkin Sirika duk abin nan da aku ya faɗi.

Da aka karanta wa Sarkin Sirika takardar, sai ya fashe da dariya, ya yi tsaki, Mts., ya ce, ''A'a! Ka ji ɗan neman tsuntsu da rigima, ƙaryace-ƙaryacen nan da ya ke wa Sarki Abdurrahman yana cin nasara, tsammani ya ke kowa sakarai ne kamarsa? Ka ji ya sami labarin Dogon Yaro da danda, ka ji zai yi rigima wai shi mai duba. To, in mutu ma, ina ruwansa? Na ce ko dai iyakar abin da a ke gudu ke nan duniya, ko da ya ke an san duka za a ne?''

Sai ya kekketa takardar ya yar, ya zauna yana zage-zage, wai aku ya raina shi. Ya kira akunsa, wannan da ya ke taƙama, ''Haziƙ, Haziƙ!'' don haka ya sa masa suna. Aku ya taso ya zo, Sarki ya kwashe labarin Waziri Aku ya gaya masa. Kuma ya ce ya yi ta tunanin daɗaɗan labarai, in ya ƙure shi zai ƙara sawa a lura da shi, kuma zai murɗe wuyan wancan akun mai rigima cikin mutane kowa na kallo.

Haziƙ ya yi dariya, ya ce, ''Waɗansu aku rigimarsu ta fi su, in sun sami wuri. Amma abokin nan naka dai ya saɓa al'ada. To, me tsuntsu zai ce cikin mutane? Amma bar su, Allah ya ba ka nasara; ba kome. In dai ni ɗan halas ne sai ka san ba kiwon banza ka yi ba. Akun Sarki Abdurrahman sai ya kwashi kunya a hannun rigarsa, in yana da ita.''

Sarkin Sirika ya ce, ''Kai, rufa wa kanka asiri. Ba a ce masa aku yanzu, sai Waziri.''

Haziƙ ya fashe da dariya, ya wuce yana cewa, ''Allah dai ya kai mu lokacin.'' Mutane suka ce, amin.

Aka shiga sha'anin mulki. Kullum aka zauna ba abin da a ke yi sai labarin Waziri Aku.

Ranar sab'a wa ashirin Sarkin Sirika ya yi shiri ya hau, da shi da manyan Sarakunansa duka, ya sa aka ɗauki Haziƙ bisa doki, suka ɗunguma da kaɗe-kaɗe, da bushe-bushe, har suka isa garin Sarki Abdurrahman. Aka tarye su, aka kai su masauki, suka sauka.

Da suka huta, dare ya yi. Sarki Abdurrahman ya tafi wajen abokinsa Sarkin Sirika, suka raba dare suna taɗin Waziri Aku, da abubuwan da ya yi har aka ba shi Wazirin Sarkin Sirika ya ce, ''Na ji. Amma duk da haka iyaka ka sa a riƙa ba shi ruwa da

sukar, amma ba a ce a yi masa Wazirci ba. A yi wa aku wazircin mutane? Haba, wannan abu ma ko daɗin ji yana da shi? Ni duk abin da ka gaya mini, na ga babban abin da ya sa ka yi masa wazirci dai don daɗin labari kawai ne, ba kome ba. To, in don ya gaya maka inda za ku taryi mutanen Sinari ne, wannan wani abin mamaki ne ga tsuntsu? Ko cikin dare ba ya iya tashi ya nufi wajen rundunar Sinari, ya ga ta inda za su ɓullo, ya zo ya gaya maka da safe ba? To, don ya yi haka sai a naɗa shi Waziri a ce yana da fasaha? In dai don irin wannan fasaha ce ka ke taƙama da shi a kanta, gobe na ga abin da za ka naɗa Haziƙ, in ya ƙure Wazirin naka."



Sarki Abdurrahman ya ce, "Na ji jawabinka. Amma sai a sa wani abu kan wannan gardama, akun da ya ci nasara a ba shi."

Sarkin Sirika ya ce, "Na sa jaka guda, in akunka ya ƙure nawa a ba shi."

Sarki Abdurrahman ya ce, "Ni kuma na sa jaka, in naka ya ci nasara a ba shi. Kuma in sa Wazirina ya zama bawan Haziƙ ɗin naka."



Sarkin Sirika ya ce shi ma ya yarda da wannan. Ya ce, "Gobe ka ji fasaha wajen Haziƙ."

Sarki Abdurrahman ya ce, "Allah ya kai mu." Suka yi ban kwana, suka watse.

Gari na wayewa, ko da azahar ta yi sai Sarakuna suka taru maƙil a ƙofar fada. Can Sarkin Sirika ya taho da mutanensa, dogarawa na tafe na "Takawarka lafiya, masu abu! Masgaye! Sunkuye! Gyara dai, zaki." Aka kafa masa karaga kusa da ta Sarki Abdurrahman, ya harɗe.

Jim kaɗan kuma sai ga Waziri tafe, ana ɗauke da shi, wa ɗansu na yi masa fita. Da ya sauka ya tafi wurin Sarkin Sirika ya yi gaisuwa. Ko da dubansa Sarkin Sirika sai ya fashe da dariya.

Waziri ya yi kamar bai kula ba, ya tashi ya tafi gaban Sarkinsa ya yi gaisuwa, sa'an nan ya zauna.

Hazik, akun Sarkin Sirika, ya kura wa Waziri Aku ido yana mamaki. Da aka natsa, Sarki Abdurrahman ya dubi Wazirinsa, ya ce, "To, bismilla."

Sarkin Sirika ya ce, "Sai a sami allo a rika rubuta wa kowa abin da ya ci a labarin da ya bayar, don in an kare a tara. Sai a ba da adadin daga ɗari, abin-da ya yiwo baya, kome dadin labari, kada ya wuce ɗari. Kuma kada a faɗi darajar sai kowa ya kare bayyana sukar da ya ke da ita game da labarin."

Sarki Abdurrahman ya ce, "Ai kuwa gaskiyarka. To, su wa za su rika faɗin darajar labaran?"

Sarkin Sirika ya ce, "Alkalina da na nan garin."

Sarki Abdurrahman ya ce, "To." Aka ɗauko allo da tawwada, aka rubuta a wannan shafi WAZIRI, a gudan kuma HAZIK.

Waziri ya dubi Hazik, ya ce, "Sai ka fara, don kai ne yaro." Hazik ya fara da habaici:

# Yaro Tsaya Matsayinka, Kada Zancen 'Yan Duniya Ya Ruɗe Ka

An yi waɗansu samari su uku a wani gari wai shi Kona, guda ana kiransa Halilu Wayo, guda Abdu Lura, ƙaramin kuwa Nahi'u Hankali. Ba banza ba aka laƙaba musu waɗannan sunannakin, sai don ko wanne halinsa ya dace da a kira shi hakanan.

Suna nan sai ran nan Halilu Wayo ya ce, "Ya kamata mu shiga duniya, mu gwada waɗannan baiwa da Allah ya yi mana. Mu ga wanda ya fi, don saura su sakam masa. Amma yanzu ina amfanin muna zaune kurum, kullum sai gardama ta fatar baki?"

Saura suka ce, "Halilu, ai ko gaskiyarka. Da ma an ce maza-dangin gujiya ne, sai an fasa a kan san bidi." Suka shirya, suka ɗunguma zuwa Bila.

Da suka isa suka nemi su ga Sarki, aka yi musu iso. Suka tafi, suka faɗi suka yi gaisuwa. Dogarawa suka amsa, Sarkin Zagi ya tambaye su sunayensu da sana'arsu, da inda suka fito da kuma inda za su. Suka faɗi sunayensu ɗai ɗai, suka gaya masa kuma sun fito daga Kona ne, za su yawon duniya, don ko Allah ya sa su sami inda za su raba gardamar da ke tsakaninsu.

Sarki ya yi dariya da ya ji sunayensu, sa'an nan ya dube su, ya ce, "Wace gardama ta rabo ku da gida?"

Halilu ya ce, "Ni da Allah ya ba wayo, tsammani na ke duk ba abin da ya fi wayo amfani cikin zaman duniya. Wannan kuwa Abdu tsammani ya ke ba abin da ya fi lura amfani ga mutum. Ɗan saurayin nan kuwa Nahi'u shi cewa ya ke ba a gama hankali da kome. Saboda haka muka fito dai, mu sami inda za mu raba wannan gardama mu huta."

Sarki ya ce, "I, ai ko lalle wannan gardama ta isa a rabo da gida, a shiga duniya neman inda za a raba ta."

To, Sarkin nan kuwa na kiwon balbelu kamar ɗari. Ka san yadda balbelu su ke, duk kamarsu ɗaya ce, amma duk da haka a cikin balbelun nan akwai wata wadda Sarki ya ke so. Ba don kome ba kuwa, sai don ita ta fi amincewa da mutane. Kullum da ta ga azahar ta yi an taru wurin fadanci, sai ta rabo da 'yan'uwa ta zo kusa da Sarki, ta tsaya yana wasa da ita. Ko da ya ke an saba

da ganinta, duk da haka da tashi ta shiga cikin 'yan'uwa ba mai sake fid da ita, don yawansu da kuma kamanninsu da ya ke ɗaya. To, samarin nan sun gama gaya wa Sarki labarinsu ke nan, sai ga balbelan nan ta taso fir, ta sauka bisa kan karagar Sarki.

Da Sarki ya dube ta sai ya ce, "Alhamdu lillahi, ga ma inda za ku raba gardamarku, ku huta da wahalar shiga duniya." Ya kamo balbela ya miƙa musu, ya ce, "To, kowa ya yi amfani da baiwar da Allah ya yi masa, ya san yadda zai yi ya gane balbelan nan, ko ta shiga cikin dubun balbelu."



Abdu ya lura da irin siffarta da kyau, tun daga ƙafafunta har ya zuwa bisa kai. Nahi'u Hankali kuwa bai ko dube ta ba. Ashe kuma sa'ad da Abdu ke lura da irinta, Halilu Wayo ya kaikaici idanunsu ya zuba mata ruwan goro a fiffike. Da suka jima da ita a hannu, Sarki ya ce su sake ta. Suka sake ta, ta tashi.

Sarki ya ce, "Na sa fam biyar, da dawaki biyar, da raƙuma biyar, da shanu biyar, da bayi biyar, duk wanda ya gane ta zan ba shi. Bayan haka kuma in gina masa gida, in naɗa shi Sarkin Fadana."

Samarin suka ce, "To, mun ji, mun ko gode, Allah ya kai mu gobe."

Gari na wayewa, balbelu suka taru maƙil a ƙofar gidan Sarki inda a ke ba su abinci. Wani bawa mai lura da su ya fita ya ba su abinci. Sarki ya kira samarin, ya ce, "To, ga su can waje, wa zai fara zuwa?" Halilu Wayo ya ce shi zai fara. Daren nan kuwa an kwana ana ruwa, saboda haka ɗan yawun goron da ya zuba ya wanke. Ya nema, bai gane ta ba, ya dawo, ya ce ya kasa, wani ya tafi.

Sarki ya dubi saura, ya ce, "Wa zai bi?" Sai Abdu Lura ya ce za shi. Ya tashi ya tafi, sai ya iske ashe abubuwan da ya lura da su a jikinta, duk galibinsu ko wacce na da waɗannan abubuwa.

Da ya ga ya rude, ya kasa gane ta, sai ya ce, "Kai, ƴace ce ke son Sarki cikinku?"

Su duka suka amsa, "Ni, ni!" To, ganinka wa zai ce ba ya son ubangijinsa, mai lura da shi ƙwarai?

Da ya ga dai bai samu abin kamawa ba, sai ya koma, ya ce ya kasa. Sarki ya yi murmushi, ya dubi Nahi'u Hankali, ya ce, "In ta bi daga daga na ƙurya ka sha kashi." Sai Nahi'u ya tashi ya tafi.

Da isarsa sai ya dube su, ya riƙe baki wai shi al'ajibi, ya ce, "Kai, ai ko jiya kun kwana kuna waƙa, amma wannan da ta je wurin Sarki jiya da azahar, ya nuna su da baki, ya ce, "ta fi kowa murya."

Ko da balbelan nan ta ji an yabe ta, sai ta ce, "Haba samari, don ma ka tarad da ni na tsufa. Da sa'ad da na ke yarinya ce, in na fara waƙa ai kowa sai kallo."

Nahi'u ya ce, "Ai lalle da alama." Ya sa hannu ya kama ta, ya ɗauka ya kai wa Sarki. Da Sarki ya gan ta, ya yi mamakin yadda saurayin nan ya gane ta. Ya kawo duk abin da ya ce, ya ba shi, ya kuma naɗa shi Sarkin Fada. Saura kuma suka shiga cikin fadawan Sarki. Sarkin Fada Nahi'u ya yi musu kyauta daga cikin abin da ya samu. Suka yi aurarraki, suka zauna nan, su da garinsu sai saƙo ko yaushe wurin iyayensu.

Ran nan da dare suna zaune da Sarki, sai wani maroƙi ya zo yana ta bunƙasa Sarki da kirari, har Sarki ya shiga cikin abin da ya ke faɗi, sai Sarkin Fada ya ce, "Allah ya ba ka nasara, ka ga fa da irin wannan bunƙasarwa ne har na yaudari balbelarka ta tona kanta." Sai Sarki ya yi sanyi da bin zancen maroƙa da na makaɗa.

Mutanen Sirika da suka ji akunsu Haziƙ ya ba da wannan labari, duk sai suka buɗe haƙora suna murmushi na wajensu ya fara da mai daɗi.

Da aka natsa, Warizi ya lura da labarin da Haziƙ ya bayar duk habaici ne ya ke yi masa, shi kuma sai ya karɓa:

# Ba Ruwan Arziki Da Mugun Gashi, Wanda Allah Ya Ba Haƙuri Ya Fi a Zage Shi

Da, an yi wani mutum mai arziki, wanda ba a taɓa samun irinsa ba, sunansa Isa Lamiri. Saboda yawan arzikinsa har duk sa'ad da aka ɗaɗi sunansa sai ka ji wani ya amsa da kirari ya ce, "Na-Asabe-ƙarfe-gari." Babban abin da ya rage masa jin daɗin duniya, shi ne ba shi da ɗa, ba shi da jika. Saboda haka ya ke cewa shi ba shi da burin tsibe kuɗinsa da Allah ya ba shi. Kullum ba abin da ya tsare sai kece raini, ya ci goro, ya busa taba sigari. Mutum ne baduniyi, mai son nishaɗi, kyauta kuma sai ka ce ruwan sama. 'Yan danginsa kullum su kan nemi su hana masa alherin da ya ke yi, suna cewa, "Isa, kuɗi ba sa son ƙazamar bukata." Shi kuwa ya kan ce musu, "Su kuwa ba su son a samu a ƙulle."

Da ya ga 'yan'uwansa sun dame shi haka, sai ran nan ya mila ya sha iska, ya tuna kuɗin nan dai Allah ne ya ba shi su ba don tanadinsa ba. Ya sa aka tara masa dukan musakai, da makafi, da matsiyatan ƙasar, ya rarraba musu kuɗinsa sadaka don Allah, bai rage wa kansa kome ba sai sisi. Ko wannensu ya yi masa addu'a, suka ce yadda ya ji ƙansu haka Allah ya ji ƙansa shi kuma, ya saka masa da fiye da abin da ya ba su. Suka watse. Duk gari aka ɗauki labarinsa. 'Yan'uwa suka yi kamar su kashe kansu don haushi. Da su burinsu, tun da ba shi da ɗa, ba shi da jika, in ya mutu su kwashe kuɗin.

To, duk wannan abu kuwa ya auku ɗaya ga watan Rabi'ul Awwal ne, watau watan Mauludi. Goma ga watan nan bai cika ba, sai da Isa ya komo abin da zai ci ma sai maƙwabta sun ba shi. 'Yan'uwansa suka yi ta yi masa dariya, suna cewa, "Ai mun gaya maka kuɗi ba su son ƙazamar bukata. Ga shi nan yau kwana goma kaɗai da rabuwa da dukiya, har ka soma bara. Allah ya ƙara."

Shi kuwa Isa duk wannan aiki na zamani bai motsa ransa ba. Duk sa'ad da ya sami kwabo sai ya ba da sisin kwabo, sisin kwabo kuwa ya sayi abinci ya kira wani kasasshe su ci, in ma bai sami kowa ba har ma ya kan kira karnuka ko kaji ya ba su.

Ran goma sha biyu ga wannan wata, watau daren Mauludi, yana barci sai ya yi mafarki, ya ji ana ce masa, "Gobe zuwa azahar wani zai zo wurinka a cikin shigar Buzaye, ya tsaya. Da ka ga ya tsaya, sai ka ɗauki kulki ka yi ta bugunsa, za ka ga ya koma kuɗi tsaba. Ka yi ta kwasa, Allah ne ya fara saka maka bisa ga alherinka. Kuma kafin baɗi war haka, matarka za ta yi ciki, za ta haifi namiji, ka sa masa suna Sa'idu."

Daga nan sai ya yi firgigi, ya tashi zaune, ya yi ta juyayin abin da ya ji. Ya ce, "Wannan abu mafarki ne ko kuwa mene ne? Ba abin da ya fi, sai gobe da azahar in lura, in na ga wani Buzu ya zo ya tsaya wurina sai in yi ta kwaɗa masa kulki. In ya koma kuɗi, to, sa'an nan ba mafarki ba ne, gaskiya ce. In kuwa ya ƙi, ko ina zai kai ni sai ya kai ni, a yi abin da za a yi."

Ya duba waje sai ya ga ashe gari ya waye. Ya tashi ya yi salla, ya sami wata ƙotar fartanya ya ajiye, bai faɗa wa kowa labarin mafarkinsa ba. Can kusan azahar sai wani wanzami, wanda a ke ce masa Shu'aibu, ɗan wanzam, Maikayan-kaifi, ya zo zaurensa ya yi masa aski, don tun yana da arziki shi ne wanzaminsa.

Ɗan wanzam ya zauna ya fara. Yana cikin yi ya duba dama ga Isa ya ga ƙota, ya ce, Wannan fa, gyara za a kai?"

Isa Lamiri ya ce, "I, ai ka san in lela ta ƙiya sai a koma basha." Can an kusa gama masa aski, sai ga wani Buzu ya shigo zaure, bai ce kanzil ba sai ya tsaya bisa kan Isa. Da ganinsa sai Isa ya tuna da mafarkin jiya, ya ce wa wanzami, "Dakata." Wanzami ya tsaya. Isa ya tashi, ya ɗauki ƙotan nan ya yi ta bugun Buzu har ya faɗi ƙasa. Buzun dai bai ce i ba balle a'a. Ya bi shi ƙasa, ya yi ta bugu da ƙota.

Ɗan wanzam zai riƙe shi, ya ce, "Ba ruwanka, ba ka san abin da ke tsakanimmu ba."

Da faɗuwarsa sai suka ga ya rikiɗa, ya koma tsabar ƙarfe tsibe. Shu'aibu ɗan wanzam ya riƙe baki don mamaki, ya ce a ransa, "Ashe idan aka yi ta bugun Buzaye kuɗi su ke zama!" Isa Lamiri ya ɗebar masa 'yan sule goma, ya sallame shi. Ya yi ta kwasar sauran yana kai wa gida. Da ya ƙulle su wuri guda sai ya zauna, ya yi godiya ga Allah bisa ga wannan baiwa da ya yi masa.

Fitar Shu'aibu Mai-kayan-kaifi ke da wuya, sai ya nufi kasuwa, ya sai wata kokara ya sulle, ya nufi rumfar da Buzaye ke zama in sun kawo dabino. Ya iske sun cika rumfar fal suna shan fura. Da isowarsa sai ya faɗa tsakiyarsu, ya cira kokaran nan ya yi ta bugunsu, duk suka yi waje da gudu. Shi kuwa ya danne ɗaya, ya yi ta bugu. Da suka ji ɗan'uwansu na ƙara, duk sai suka juyo suka tasar wa Shu'aibu gaba ɗaya, suka kama shi, suka ɗunguma zuwa wurin Sarkin Kasuwa. Sarkin Kasuwa ya miƙa da su har wurin

Sarki. Suka ce, "Ga wani mahaukaci ya yi wa ɗan'uwammu rotse."

Sarki ya dubi wanda aka yi wa rauni, ya ce, "Garin me wannan abu ya faru haka?"

Buzaye suka ce, "Galla muna zaune a rumfa muna shan fura, daga nan galla sai ya shigo ya same mu, ya yi ta duka. Ko da muka ga zai kashe mana ɗan'uwa, sai muka ce kai namiji, galla maza bisa kanka. Muka kammai, muka zo da shi nan." Mutane kuwa suka shaida hakanan ne. Sarki ya dubi Buzaye, ya ce, "Motsuwa ya yi, sai ku yi haƙuri, zan sa a sa shi a turu."

Da ɗan wanzam ya ji batun turu sai ya dubi Sarki, ya ce "a'a! Yaya za a sa ni turu lafiyata lau?"

Sarki ya yi murmushi, ya ce, "To, in lafiyarka lau ne, me ya sa ka yi wannan aiki?"

Ɗan wanzam ya ce, "Akwai kuwa, ina da dalili, ranka ya daɗe. Yau da azaharin nan ina yi wa Isa Lamiri aski sai wani Buzu ya shigo zaurensa. Da ganinsa Isa ya tashi ya yi ta bugunsa, sai na ga nan take ya koma kuɗi tsaba. Cikin kuɗin nan ma har ya ba ni sule goma, ga su."

Da fadawa suka ji haka sai suka fashe da dariya, suka ce "Lalle ɗan wanzam ya motsu, amma a kira Isa Lamiri a ji." Nan da nan aka kira Isa ya zo.

Sarki ya tambaye shi. Isa ya ce, "Karya ya ke yi. Ina wannan zai yiwu? Tun da na kira shi ma ya yi mini aski, na ga lalle dai yau kansa ba ɗaya ba ne." Ya cire rawani, ya ce, "Kun ga ma bai gama mini askin ba, ya zabura da gudu ya bar ni."

Shu'aibu, Ɗan wanzam, ya dubi Isa Lamiri, ya ce, "Haba Isa, faɗi gaskiya dai. Watau don ka yi ta bugunsu ka riƙa samu kai kaɗai ko? Ba ka son kowa ya gane asirinka. In ƙarya na ke yi, ku bari in ƙara bugun wannan ku gani mana in bai zama ba. Da ma sauran kaɗan ya koma kuɗi, ƙetarmu ta 'yan kasuwa ta sa suka ɓata mini nama."

Da Sarki ya ji haka sai ya ce, "Lalle dai motsuwa ya yi. Sai a kai shi kurkuku."

Za a fita da shi sai Isa Lamiri ya durƙusa gaban Sarki, ya ce, "Cikin albarkacinka, ranka ya daɗe, in ka yarda ina son ka ba ni shi in tafi gida in sa a yi masa 'yan rubuce-rubuce. Kafin kwana uku in ya yi sauƙi, to, in kuwa ya faskare mu sa'an nan zan mayad da shi gare ka, ka taimake mu."

Sarki ya ce, "To, shi ke nan, ku tafi. Allah ya sawwaƙa."

Lamiri ya kama hannunsa za su fita, sai ya dubi Buzaye, ya ce, "Mhm. Kai! Ga kuɗi a fili, wauta ta sa ku bar su su wuce." Duk aka fashe da dariya. Aka watse.

Isa Lamiri ya kai shi gida, ya yi ta rarrashinsa yana cewa, "Wallahi kada ka biye wa mafarki, ya sa a ɗaure ka ba ka ci ba, ba ka sha ba. Ko da ka zo nan zaurena da alamar barci-barci ka zo, har kana yi kana tsayawa, sa'ad da ka ke yi mini aski. Shin, in ma ba mafarki ba, ka taɓa ganin an bugi mutum ya zama kuɗi? Lura fa cikin hankalinka." Ya yi ta kawo masa misalai dai, har ya yarda abin nan dai mafarki ne ya tashi juyad da hankalinsa.

Da Isa ya ga ya ciwo kansa, ya raka shi gida ya dawo. Ko yaushe ya zo ya yi masa aski sai ya tuna masa da wautar da ya yi, su yi ta dariya.

Bayan kamar kwanan wata matar Isa ta yi ciki. Watan nan bai dawo ba sai da ta haifi ɗa namiji. Bai manta da abin da aka gaya masa ba, ya sa masa suna Sa'idu. Aka yi biki da shagali mai yawa.

Ɗan wanzam kuwa duk inda ya kewaya gari sai mutane su yi ta yi masa ba'a, suna cewa "Dan wanzam mai Buzaye!"

Mutanen Sirika da suka ji wannan labari sai suka ƙura wa Waziri Aku ido suna mamaki. Sarkin Sirika ya dubi Sarki Abdurrahman, ya kaɗa kai. Haziƙ zai fara wani, Sarkin Sirika ya ce, "Sai mu tafi mu yi la'asar, sai gobe kuma a ci gaba. Abin da a ke yi don nishaɗi ya zama kamar cin ƙwan makauniya?"

Alƙalai suka yi shawarar darajar da za su ba kowane labari. Da suka gama hankalinsu suka ce, 'Labarin Haziƙ talatin, Waziri hamsin." Mutane suka watse. Sarkin Sirika ya ce wa alƙalai, "Ya kamata a riƙa shari'ar gaskiya dai."

Sa'an nan alƙalan kuma suka ce wa Haziƙ da Waziri, "Labari kaɗai a ke so, ban da habaici. Ku kun sani da kayan Sarki Abdurrahaman da na Sarkin Sirika duk ɗaya ne."

Waziri ya ce, "Hakanan ne. Haziƙ ne da ma ƙuruciya ta tashi ɗibarsa, amma ba kome."

Da aka isa gida Sarkin Sirika ya kira Haziƙ, ya ce, "Labarin da ka yi yana da daɗi, sai ka yi ƙoƙari kuma yau, ka tuna da wanda ya fi shi. Don an ba shi hamsin, ka san wannan ba kome ba ne. Sai mun yi kwana wajen goma sha biyu nan ana labari, tun yana masu daɗi har su ƙare a bar maka fage."

Haziƙ ya ce, "Don ban san irin kamun ludayinsa ba ne da ma. Gobe ma gamu."

Can zuwa magariba sai Waziri ya aiko Haziƙ ya tafi su ci abinci tare. Aka ɗauke shi aka kai, aka kawo musu abinci iri iri suka yi ta ci, waɗansu ma Haziƙ bai taɓa ko jin sunansu ba.

Da suka gama Waziri ya sa aka kawo goro aka ɓara musu, ya

cika bakinsa, ya miƙa wa Haziƙ ɓari. Haziƙ ya ce ai shi bai taɓa cin goro ba, yaya zai yi ya tauna shi ma? Waziri ya yi murmushi, ya sa aka mai da Haziƙ gida, yą tafi yana ta mamakin wannan irin daula da Waziri Aku ke ci haka.

Da gari ya waye, azanar ta yi kuma aka sake taruwa, Haziƙ ya fara:

# Labarin Kalala Da Kalalatu

Akwai wani mutum wai shi Kalala, yana da matarsa wadda a ke kira Kalalatu. Kalala Allah ya yi shi wani irin mutumin da ne, ba abin da ya fi da ƙi illa a yi masa abinci ya ci shi kaɗai. Da suna ci tare da wani maƙwabcinsa, sai maƙwabcin ya zama wani iri ne mai mita. Ya kan riƙa cewa Kalalatu ba ta iya miya ba, wai kullum miyarta daga ta cika gishiri sai ta cika ruwa.

Da Kalala ya ga tsegumin ya faye yawa sai ya bar kai abincinsa wurin maƙwabcin. Ya riƙa fita karauka yana nemo baƙi, yana kawowa gidansa suna ci tare.

To, Kalalatu ba ta ƙaunar wannan ɗabi'a ta mijinta, domin bisa ga misali, ran da Kalala ya yanka kaji biyu, iyaka Kalalatu ta sami cinya, domin duk Kalala zai kai wurin baƙin da ya jawo ne su cinye. Ta yi, ta yi ta hana shi wannan tabi'a, ya ƙi hanuwa. Saboda haka sau da yawa in ya ba ta dahuwa sai ta tsame rabi ta cinye, in Kalala ya yi magana ta ce ya ƙone ne, ko kuwa ta ce ta sauke ta shiga ɗaki ɗauko kwano, kafin ta fito ta tarar kyanwa ta cinya rabi. Dalilai dai irin waɗannan marasa kan gado ga su nan kullum Kalala na ta sha, amma saboda haƙurin da Allah ya zuba masa ba ya cewa kome.

Ran nan, ko ina Kalala ya sami kuɗi sai ya tafi kasuwa ya nemo daƙwalen kaji guda biyu ya sawo. Ya yiwo cefane ya kawo gida, ya ce wa Kalalatu ta soye kajin nan gaba ɗaya. Ta tashi, bayan ya fige ya gyara mata, ta sa tukunya ta shiga suya. Abu ga daƙwalen kaji, duk kitse ya cika tukunya, sai wani abu su ke coi, coi, coi, in tana juya su. Duk kuwa kwaɗayi ya kama ta, da ma ga ta idonta idon nama sai ka ce kura sai yawu ke zuba dalala. Ta sa ɗan yatsa ta ɗanɗana ta ji ko gishiri ya yi daidai, sai ta ji abin daɗi ya kamo ta har ga ƙeya, ta ce, "Kai, waɗannan kaji yau suna shirin ganin wata irin gajerar suya. Amma dubi duk yawan kajin nan, rabona bai fi cinya ba daga cikinsu. Ka san dai halin mai gidan nan ya miskile ni."

Ta ci gaba da suya ƙanshi na jifarta, ta yi kamar ta jure ta kasa, sai ta fara tsame tana ci, wai ta kau da mugun yawu. Kafin su

soyu ta kusa cinye rabin kaza. Da ta sauke sai ta je ta gaya wa mijin sun soyu.

Kalala ya ce, "To, sai ki cire cinya guda, taki ke nan. Saura kuwa a ajiye, har in je in samo abokan ci."

Kalalatu ta ce, "To." Ta tafi ta cinye 'yar cinyar da aka ce ita ce tata, ta tsuguna tana kallon saura, sai mai ke zuba nash, nash. Ta ruga wajen ƙofar zaure ta leƙa ko ta hango mijin tafe da baƙin, ba ta ga kowa ba, ta komo wajen kaji ta ƙura musu ido. Sai ta ce, "Af, ashe ma fikafikai guda biyu sun ƙone tun ɗazun, bari in cinye na ɗayar kuma don su zo daidai, kada mai gida ya gane." Sai ta kama fikafikai ta fiffizge ta laƙwame. Ta sake rugawa bakin zaure ta gani ko mijin na tafe, ba ta ga kowa ba. Ta dawo, ta tsaya bisa kwanon da kaji su ke, ta ce, "Shin mai gidan nan zai zo dai? Ga kaji har sun fara yin sanyi. To, ni Kalalatu, yanzu in ya zo ya tarar wannan kazar duk na fiffige ta, ya tambaye ni, in ce me? Ba abin da ya fi sai in cinye ta gaba ɗaya, in ya zo in ce kyanwar gidan nan ta sace ta." Sai ta tsuguna ta cinye ta sarai, ta kwashi ƙasussuwa ta kai masai ta zuba.

Ta koma ƙofar zaure ta hanga, ba ta ga mai gida ba. Da ta ga haka sai ta dawo, ta ce, "A bari ya huce shi ya kawo rabon wani. Bari in ƙarƙare cinya guda, kowa ya huta, in ya so in ya dawo kome ta tafasa ta ƙone." Sai ta kama kazar guda kuma ta laƙume. Ta nufi randa ta ɗebi ruwa ta kora, ta yi gyatsa, ta ce, "Madalla, kome ta ke zama ta zama."

Ta zauna ke nan, sai ga mai gida ya shigo. Ya ce wa Kalalatu, "Yi maza ki niƙa yaji ki barbaɗa musu, kin san yanzu lokacin sanyi ne, ba abin da ya fi yaji amfani. Na manta ne in gaya miki ki niƙa yaji ɗazun. Yi hakuri, yau dai kin sha aiki."

Kalalatu ta ce, "Ai ba kome, ku dakata mini dai kaɗan." Ta shiga ɗaki tana ta shawarwarin abin da za ta ce wa mijin ya faru ga kaji. Tana can cikin ɗaki, sai Kalala ya ɗauki wuƙa ya nufi maniƙa yana wasawa ƙararas, ƙararas, wai don ta yi kaifi ya sami ta yanka kaji ƙanana ƙanana, in an kawo.

Kalala na can na ta fama da washin wuƙa, sai Kalalatu ta ji ana sallama. Ta yi farat ta fita bakin zaure wajen mai sallama, ta dube shi ta riƙe baki, ta ce, "Kai baƙo, kai ne mai gidan nan ya kirawo, wai ku zo ku ci abinci?"

Baƙo ya ce, "I, Allah ya saka muku da alheri."

Kalalatu ta ce, "Kai, tafi can, sakarai, ba ka san abin da a ke ciki ba. Kana tsammani mutum mai hankali ya sa a yi masa abinci ya fita karauka neman abokin ci? In kana kama gabanka ka ruga, tun da wuri ka ruga. Ka ji shi can yana washin wuƙa, kunnenka guda zai yanke. Kullum haka ya ke yi, motsattse ne."

Baƙon nan, ko da ya saurara ya ji Kalala na washin wuka sai ya dafe ƙeya ya zura a guje. Kalalatu kuma ta ruga wajen Kalala, ta ce, "Ga irin jaye-jayen naka nan, ba ka san irin mutanen da ka ke jawowa gida ba."

Kalala ya ce, "E? Mahaukaci ne?"

Kalalatu ta ce, "Mahaukaci mana, ko ba mahaukaci ba ne ai ɓarawo ne, da ɓarawo ko da mahaukaci ai duk tafiyarsu ke nan. Kajin da na barkaɗa wa yaji, ko da ya gan su sai na ga ya yi wuf ya fizge, ya shafa a guje da su. Ga shi can ya miƙa, ya tasar wa kasuwa."

Kalala ya fusata, ya ce, "Allah wadan ɗan banza! Mutanen duniya ba wanda ke iya musu. Da ma ya bar mini ko da guda ɗaya, ai da na sami ta kalaci. Daƙwalen kajin nan duk ya cinye shi kaɗai? Bari in leƙa ko na hango shi, mu raba." Sai ya ruga wajen zaure ya hanga, sai ga baƙon nan can ya tattake da gudu kaca kaca kaca yana korar iska. Kalala ya ce, "Kai abokina! Kai tsaya, don Allah ko guda ɗaya ka ba ni! Wallahi su ke nan, mai ɗakina ko lasawa ba ta yi ba, ka ɗauke." Baƙo ya yi kamar bai ji ba.

Kalalatu ta ce wa mijin, "Bi shi mana, a guje dai na san ba ya tsere maka. Duk wahalan nan da na sha ta zama a banza, ko lasawa ban yi ba, ai ka san ka ɗauki alhakina."

Sai Kalala ya runtuma a guje da wuƙarsa a hannu, ya bi baƙo yana kira, "Tsaya don Allah, ɗaya kaɗai na ke so, na bar maka ɗaya!"

Baƙo tsammani ya ke Kalala na nufin kunnensa ɗaya kaɗai ya ke so ya yanka. Ya waiwaya sai ya ga ya taso masa da wuƙa tsirara a hannu.

Saboda haka ya ƙara mai, ya dai yi wa Kalala fintinkau yana ji yana gani.

Da Kalala ya ga abin ba girma, sai ya juyo ya nufo gida da wuƙarsa a hannu, yana ƙutawa, yana Allah ya isa. Da matar ta gan shi ya dawo yana zage-zage sai ta tarye shi, ta ce, "Ya ba ka? Ka ga irin abin da na ke gaya maka nan tuni."

Kalala ya ce, "Ko tarad da shi na yi? Wannan akwai ɗan banza da gudu! Ga shi kamar tsoho, amma da ya zura sai ganinsa a ke kamar ba ya taka ƙasa. Bar shi ya je ya ci, ban dai yarda masa ba duniya da lahira. Allah ya isa. Daga yau ko sai yau, ba na sake kiran ɗan kowa ya ci abincina, tun da duniya ta sake. Mts, Allah wadai! Talaka dai ba aboki ne ba, ko ka so shi ran biki kwa ɓata."

Mutane da suka ji wannan labari suka fashe da dariya. Da suka yi shiru Waziri ya soma:



## Labarin Yusha'u Na-Narimi Dutse-Ba-Ka-Fargaba

Da, an yi wani yaro wanda Allah ya nufa da wata irin zuciya sai ka ce dutse, don rashin fargaba. Saboda ganin haka sai ya riƙa alfahari, yana cewa shi duk duniyan nan bai ga wani abin da zai ba shi tsoro ba har ya kaɗu. 'Yan'uwansa yara su kan ƙulla abubuwa da yawa yadda za su sa ya kaɗu, amma duk a banza. Saboda haka har suka sa masa suna 'Dutse.' Da sun gan shi sai su riƙa yi masa kirari suna cewa, "Yusha'u Na-Narimi, dutse-ba-ka-fargaba."

Da kakansa ya ji haka, sai ya ce shi lalle sai ya ba shi tsoro har ya kaɗu. Yusha'u kuwa duk bai san abin da a ke ciki ba. Ran nan da tsakad dare sai ya tafi hira wata unguwa, ya raba dare bai dawo ba. Da kakan nan nasa ya ji haka sai ya tashi, ya sami karare, ya ɗaura wani mutum-mutumi dogo, ya sa masa farar riga, shi kuma ya sa wa kansa fara. Sai ya tashi ya ɗauki mutum-mutumin nan ya ɗora bisa kansa, ya tafi hanyar da yaron nan zai biyo, ya maƙe.

Can zuwa tsakad dare, duk ba wani mahaluki mai motsi, sai ya ji yaron nan tafe yana waƙa. Da jinsa sai ya fito daga inda ya ke ɓoye, ya tasam masa haiƙan. Da Yusha'u ya ga ya nufo shi sai ya ce, "Kai tsololo, in aljani ne kai, lalle Allah bai halicce ka da tsari ba, ga ka tsololo, amma ɗan kai sai ka ce ƙodago. Ko kuwa fatalwa ce? In kuwa fatalwa ce, na so in gan ta sa'ad da ta ke da rai. Zotori!"

Kakansa dai bai ce uffan ba, ya dai nufo shi har ya taka wa yaron nan ƙafa. Sai yaron ya tsaya, ya ce, "A'a! Shakiyancin nan na aljannu da fatale har ya kawo gare ni? Kai tsololo, mene ne na taka ni? To, ko da ya ke tsawona bai kai in mar ka ba, ai ka sha kulki!" Sai ya dunƙula hannu, ya kai wa kakan bugu, tim!

Ya sake ɗagawa zai ƙara, sai kakan ya yad da karan, ya ce, "Kai, kai, kai, ni ne kakanka Narimi, kada ka buge ni."

Yaron ya yi murmushi ya ce, "Kaka, me ya sa ka yi mini haka, ga shi har ka sa na buge ka?"

Narimi ya ce, "Mutane na ke ji suna cewa, ni ba wani abin da

za a yi maka har ka kaɗu, shi ya sa na yi wannan dabara wai ko na sa ka ji tsoro. Ashe dai gaskiyarsu. Gobe kuwa sai na tafi na gaya wa Sarki jaruntakan nan taka."

Yaro ya ce, "Shin kaka, mene ne tsoro ne? Ni ban san abin da a ke kira hakanan ba. Ashe yanzu nan duniya har akwai abin da zai sa In kaɗu?" Kakan ya yi murmushi, ya koma gida.

Gari na wayewa sai kakan ya tafi ya gaya wa Sarki, ya ce yana da jika wanda ba abin da za a yi masa ya kaɗu. In Sarki yana so ya gani, ya kirawo shi ya gwada shi. Fadawa suka ce, "Allah ya ja zamaninka, wannan yaron ai sananne ne a kan rashin tsoro, ai tun da ya ke babu abin da ya taɓa sa shi ya kaɗu."

Sarki ya ce, "To, madalla, gobe ku zo da shi mu gani. Ai inda ba ƙasa a ke gardamar kokawa."

Da gari ya waye kakan ya kira yaro, ya gaya masa abin da suka yi da Sarki; Yaro ya ce, "To, sai mu tafi, in shakka ya ke yi."

Da aka yi sallar azahar, da yaron da kakansa suka tafi gidan Sarki. Suka tarad da fada ta cika, kowa na faɗin albarkacin bakinsa. Suka faɗi suka yi gaisuwa. Dogarawa suka ce, "An gaishe ku."

Sarki ya dube su, ya ce, "Kun taho?"

Kakan ya ce, "I, Allah ya ba ka nasara, ga yaron."

Sarki ya dubi jama'a ya ce, "Kun ga yaron da aka ce bai taɓa kaɗuwa ba don tsoro. Ina so in gwada shi, amma ku shaida, in aljannu suka halaka shi, ko kuwa suka zauta shi, kada a zarge ni. Zan sa shi ya kwana cikin ɗakin gindin tsamiyan nan ta gunki. In ya tashi lafiya gobe, ba a ji ya yi kuwwa ba, ko wata firgita, zan ba shi 'yata aure."

Dan kakan yaron nan ya ji haka sai idonsa suka yi ƙwal-ƙwal. Fadawa kuma duk suka dube su, suka yi dariya. Kowa ya san tsamiyan nan a kan ƙwanƙwamai. Nan ne kuwa fadar Sarkin aljannu. In mutum ya bari magariba ta yi masa, ko kuwa rana ta take yana kusa da wurin, sai wani ba shi ba. Wannan abu ba ko camfi ba ne, an ga haka ba ɗaya ba, ba biyu ba. Saboda yawan aljannu har a ke kiranta "Mutuwa kusa."

Da kakan yaro ya ji haka sai ya ce, "Ranka ya daɗe in da wannan za a gwada shi, ba ya iyawa, ƙwarinsa bai kai haka ba."

Yusha'u ya yi wuf ya ce, "Me ya sa ka ce haka? Cikin duniyan nan ashe har akwai wani abin da zai sa ni in kaɗu ma, balle har a ce in yi ihu? Haba, ranka ya daɗe, ko ba ka san labarina ba ne? Ni ne fa Dutse Na—Narimi ba ka fargaba. Allah ya kai mu magariba."

Kakansa ya yi, ya yi, ya hana shi, ya tsaya shi sai ya kwana. Narimi ya gaji, ya ce, "Je ka, ai mai rabon shan duka ba ya jin

kwaɓo, sai ya sha." Suka sallami Sarki, suka tafi gida, duk Narimi na zulumin abin, yana cewa, "Lalle baki dai shi ke yanka wuya."

Magariba na yi sai yaron nan ya ɗauki 'yar tabarmarsa, ya tafi gindin tsamiyan nan, ya shige ɗakin ya yi shimfiɗa, ya kunna fitila, ya kwanta, ya bar ta tana ci. Aka zo aka gaya wa Sarki. Sai ya sa waɗansu malamai su huɗu, suka sami wani wuri can nesa da gindin tsamiyar, suka ɓuya. Suka tsaya daidai da inda za su iya hangen duhun yaron nan cikin ɗaki; don ƙada ya fito.

Yana nan kwance sai ya ga wani aljanni ya keto bangon ɗakin ya fito, duk tsawonsa bai fi kamu guda ba. Amma kansa, duk inda tulu ya kai da girma ya fi hakanan. Da fitowarsa sai ya zauna gindin fitila tare da yaron, ya yi masa ƙuri da ido. Sai Yusha'u ya ce masa, "Me ka ba ni ajiya ne, har ka dame ni da kallo haka? Ko kuwa kana da wani ɗa ne kamata wanda ya ɓace?" Aljannin nan dai bai ce masa uffan ba, sai lashe-lashen bakinsa ya ke yi. Yaro ya ce, "Kurwata kur, ka ci kanka, ka sha baƙin ruwa!" Aljanni dai bai ce masa kome ba.

Suna nan zaune, sai ga cinyar mutum ta faɗo ƙasa tim, har da jini. Yusha'u ya dubi cinyar, ya ce, "Kai, mai wannan cinya lalle kafin ya mutu an yi ƙato! Shinkici! Amma irin ƙattan nan galibi ba su kan yi ƙarfi ba. Bari in jinjina cinyar, in ji in ɗa alamar ƙarfi." Ya tashi ya cicciɓi cinyan nan ya ji ta sakwat, ba nauyi. Sai ya ce, "Allah wadai, yau ga ƙaton kwabo! Ashe duk ƙatancin nan ta gina ne ba ta shiga ba." Sai ya yar da ita waraf, ya koma kusa da gajeren nan na tsugune. Ya zauna ke nan, kuma sai wata cinyar ta faɗo kusa da ta fari. Kafin a yi haka kuma sai ga hannuwa sun faɗo. Yaro dai bai ce kome ba sai dariya ya ke yi musu. Can kuma sai ga gangar jiki ta faɗo tirim. Ko wace gaɓa ta liƙe ga 'yar'uwarta, sai ga mutum ya tashi ya nufo su, amma ba kai. Yaron nan ya ce, "Kai, wannan huhun ma'ahu ya faye ɗoki! Tsaya mana tukun kanka ya faɗo sa'an nan ka zo, in hira za mu yi."

Aljani dai bai ce kome ba, sai ya zo wurin wancan ɗan gajeren nan da ya fara zuwa, ya danne shi, ya kama hannunsa guda ya kakkarya shi rugu-rugu, ya bar shi nan yana kuka. Ya zabura zai gudu sai ga waɗansu aljannu guda biyar sun tsago ƙasa sun fito. Da ganin abin nan da ya faru, sai suka yi cacukwi da wannan da ya karye ɗan'uwansu, suka ce, "A'a, a, a! Kai Kururrumi, kai ka karye Ɗandagizge? Wallahi yau in Sarkin Aljannu ya zo, bari ta kai, ko da mutumin nan mai fitala da ke nan aka yi abin, kashinsa ya bushe!"

Sai yaron nan ya ce, "Kai, in kuna shiriritarku ku bar gamawa

da ni. Ka ga 'yan nema masu manyan kunnuwa! Kashina ya bushe! Halama ni na kashe shi?"

Kai, in gajarce muku labari dai, aljannun nan suka yi ta ba shi tsoro iri iri har gari ya waye, amma Yusha'u bai razana ba, balle ya kaɗu.

Da rana ta fito ya ɗauki 'yar tabarmarsa, ya nufi gidan Sarki, ya ce ya dawo. Mutane za su yi musun bai kwana ba, sai malaman nan huɗu suka shaida ya kwana. Sarki ya rasa abin da ke masa daɗi, ga shi ya yi alkawari ba damar warwarewa. Mutane suka yi ta mamakin yaron nan, kakansa kuwa ya yi ta farin ciki da ya kuɓuta.

Sarki ya tashi, ya shige gida duk rai a ɓace, ya kira 'yar da uwarta, ya gaya musu wannan al'amari duka. Yarinyan nan ta ga ran iyayenta ya ɓaci, sai ta ce, "Kada ku ɓata rayukanku a banza, na ce ko kaɗuwa ce ya ce bai ga abin da zai sa shi ya yi ba?"

Uban ya ce, "I, lalle ko gaskiyarsa, duk duniyan nan kuwa babu."

Yarinya ta ce, "To, na ce ko kun gama naku na manya? Saura kuma mu mu yi ƙoƙarimmu na yara, mu gani."

Uban ya yi dariya ya ce, "Wane ƙoƙari gare ku na yara ban da wauta?"

Yarinyar ta ce, "Ina so, in ka yarda, baba, ka je yanzu cikin taro, ka ce ka ba shi ni, amma da sharaɗi guda, shi ne daga yau har kafin rana wa ta yau, in wani abu ya sa shi ya kaɗu, baiko ya tashi."

Uwar ta yi dariya ta ce, "Ka ji wautar tamu ta mata! Wanda ya kwanta ɗakin gunki bai ji tsoro ba, to, me zai tsorata shi a cikin gidansa?"

Uban ya ce, "Bari in je in faɗi, kada mu rage mata hanzari." Sai ya koma zaure ya faɗa wa mutane haka, duk suka shaida. Yusha'u ya yi dariya, ya sallami Sarki ya tafi gida, iyayensa suka yi ta yi masa guɗa don murna. Yarinyan nan kuwa ta san tun da ya kwana ɗakin gunki jiya, lalle aljannu ba su bar shi ya runtsa ba, tun da abin ya ke haka kuwa, daren yau lalle in ya fara barci sai Allah. To, lokacin nan kuwa cikin tsakiyar ɗari ne mukumuku. Saboda haka da asuba sai yarinya ta tashi ta faɗa wa ubanta, ta sa ya aike aka tado Waziri da Alƙali, da manyan malaman gari guda huɗu waɗanda Sarki ya sa su tsaron nan jiya da dare. Da suka taru, sai yarinyar ta ɗebo ruwa mai sanyi ƙwarai daga wani sabon tulu, ta ba Sarkin Zagi ya ɗauka, duk suka ɗunguma zuwa gidan.

Da suka isa ƙofar gida, ta ce kada kowa ya yi magana, ko wani babban motsi. Ta sa aka tafi sululu aka tado kakan yaron nan, ya

fito waje ya tarad da su, kowa dai ya zuba wa 'yar yarinya ido ya ga abin da za ta yi. Sai ta ce kakan yaron ya shiga gaba ya nuna musu ɗakin jikansa, amma fa ba a ce in ya je ya ta da shi ba, ko motsi mai ƙarfi ma kada kowa ya yi.

Suka isa, ta tarad da ɗakin rufe da asabari, ta sa hannu sannu a kan hankali ta cire, sai ga yaro kwance tim, daga shi sai durwar bante, barci ya sa har ya ture ɗan bargonsa bai sani ba. Sai ta karɓi ruwan nan ta shiga cikin ɗakin saɗaɗaf, saɗaɗaf, ta watsa masa a jiki. Ko da ruwan nan ya zuba masa sai ya kaɗu, ya yi firgigi ya tashi, ya ce, "Wai!" Duk mutanen nan suka yi tafi baki ɗaya, suka bushe da dariya, suka ce, "A' ya kaɗu, ya kaɗu!"

Da Yusha'u ya buɗe idonsa, ya gane makirci ne aka yi masa, sai kunya ta rufe shi. Don gudun jin kunya bai bari gari ya waye masa ba, sai da ya gudu ya bar garin. Mutane suka yi ta mamakin wannan fasaha ta 'yar yarinya.

Da Sarki ya komo gida ya gaya wa uwar yarinyar abin da ya faru, duk sai suka rungume ta don murna. Da gari ya waye Sarki ya nemi yaro, aka ce ai ya gudu. Sai ya sa mutane su bi shi. Kafin azahar aka komo da shi. Sarki ya naɗa shi Sarkin Yaƙi. Aka ba shi ƙaton gida. Sarki ya aura masa 'yam mata biyu daga cikin 'ya'yan bayinsa. Da ma abin da ya tsana ya ba shi 'yar cikinsa, ga shi talaka. Sarki kuma ya yi wa kakan yaron nan kyauta mai yawa don jaruntakar jikansa. Suka yi ta cin duniyarsu a tsanaki. Kullum idan Sarkin Yaƙi ya tafi fada Sarki ya ce masa, "Yusha'u, Sarkin Yaƙi, Na-Narimi, dutse ba ka ƙargaba." Shi kuma sai ya ce, "Lalle ba na ƙargaba sai na ruwa, Allah ya ba ka nasara." Duk sai a yi ta dariya.

Mutane suka ce, "Ba Sarki ne kaɗai ba, kowa ya ji wannan labari ai lalle ya yi dariya."

Alƙalai suka ce, "Haziƙ ashirin, Waziri saba'in."

Sarkin Sirika ya ɓata fuska, ya ce, "Kaliyani fin nari wa ƙali filjannati."

Ana komawa gida kuma Waziri ya sa aka tafi aka kira Haziƙ suka sake yin dina tare. Da suka gama ya sa aka ɗauke shi; aka mai da shi gida.

Gari na wayewa kuma, da aka yi sallar azahar sai aka sake taruwa. Mutane har daga ƙauyuka suka yi ta zuwa, don sun ji labarin wannan babban taro. Aka sa mutane suka yi tsit, sa'an nan Haziƙ ya shiga aikinsa.

## Mara Gaskiya Ko Cikin Ruwa Ya Yi Jiɓi

Wata rana waɗansu Filani su bakwai suka tashi daga rugarsu za su yawon sharo. Suna cikin tafiya sai suka kai wani gari, suka ga in sun wuce dare zai yi musu ba su kai gari na gaba ba. Saboda haka suka sami wani ƙaton zaure a gidan Sarkin Fawa, suka sauka. Ashe guda na da kuɗi, bai gaya wa kowa ba cikin 'yan'uwan nan. Sai can da dare suna hira, ya ɗauko kuɗin nan ya ƙidaya su sule goma sha biyar, ya mayar ya ƙulle a warki, ya ce, "Na she im mun je ni sai na samo aure."

'Yan'uwansa suka ce, "Mun she mu ma ko da ba mu jo da kuɗi ba, da danshe na she ma samo."

Can da dare ashe guda duk haushi ya kama shi, don shi ba shi da ko anini. Sai ya tashi ya sace kuɗin nan, ya kai ya binne, ya komo ya kwanta.

Da gari ya waye za su tashi, mai kuɗin nan ya kwance warki wai ya ɗauko kuɗi ya ƙidaya, kuɗi suka ce ɗauke mu inda ka ajiye. Ya fa tashi da zage-zage, ya ce 'yan'uwansa suka sace don baƙin ciki.

Da Sarkin Fawa ya ji zage-zage a zaure, ya fito ya tambaye su. Mai kuɗin nan ya mai da jawabi duka. Da Sarkin Fawa ya ji haka, ya yi ƙoƙari ya sami wanda ya ɗauka, ya rasa. Sai ya ce wa mai kuɗin, "Ka yarda, ko kuwa in kai ku ga Alƙali?"

Mai kuɗi ya ce, "A'a? Sai a kai mu ga Alƙali, na she kuɗin nagge guda in yad da shi, ai ba shi yiwuwa."

Sarkin Fawa ya sa su gaba har Majalisar Alƙali. Alƙali ya tambayi mai kuɗin nan, ya bayyana masa yadda aka yi. Da Alƙali ya ji haka sai ya ce wa sauran Filani, "Ashe da ma abin ba sacewa kuka yi ba? Don Allah ku ba shi kuɗinsa, ku tafi abinku. Da ya ke da wasa kuka ɗauka ai ba ku bari a zo gaban magabata ba."

Sai duk baki ɗaya suka ce, "Renki shi daɗe, ai mu ba mu ɗaukar masa kuɗi ba."

Alƙali ya ce, "Haba, ku kun faye son wasa, na ce ko kun gwada shi ne ku gani ko ya karaya. To, ya yi raki, ku ba shi abinsa, ku tafi ku ba ni wuri."

Filani suka tsaya tsakani da Allah su ba su ɗaukar masa kuɗi ba. Da Alƙali dai ya yi waɗannan 'yan dabarunsa na mahukunta ya ga abin ya ƙi, sai ya samo dogwayen sanduna guda shida, ya auna tsawonsu, kowa na kallo, ya yanke su dai dai da juna. Ya ɗauka ya rarraba musu, ya ce wa Sarkin Dogarai, "Tafi da su gidan waƙafi sai gobe. An ce in wasa ku ke yi, ku faɗi gaskiya ku tafi, kun ƙi. To, in ni Alƙali ne ba ƙarya ba, na kuwa gaji abin nan, kaka da kakanni, gobe in kun zo a ga sandan ɓarawon nan ta fi ta saura da rabin taƙa. Ku jama'a, duk kun ga tsawonsu ɗaya ko?"

Mutane suka ce, "I, Allah ya gafarta malam."

Ya dubi Filani, ya ce, "Ku kuma kun gani hakanan ne ko?"

Filanin suka ce, "I, Allah shi daɗe da renki." Alƙali ya ce, "To, Sarkin Dogarai, tafi da su. Kai kuwa Sarkin Fawa tafi da wannan mai kuɗin gidanka sai gobe." Suka tafi. Da dare ya yi tsaka, kowa ya yi barci, sai ɓarawon nan ya rasa abin da ke masa daɗi a duniya, ya tabbata gobe Alƙali ɗaure shi zai yi in an sami sandansa ya ƙaru da rabin taƙa. Saboda haka sai ya gwada rabin



taƙa, ya zaro wuƙar da ke gindinsa ya yanke, ya ce watau gobe in sandansa ya ƙaru da rabin taƙa, sai ya yi daidai da na saura.

Da gari ya waye Alƙali ya zo gidan shari'a, sai ya aika Sarkin Fawa ya zo da baƙonsa. Sarkin Dogarai kuma ya taso ƙeyar waɗancan, kowa da dogon sandansa a hannu. Da suka taru Alƙali ya ce, "To, jama'a, kowa ya matso ya gani." Da suka matso duk Filani suka zaro ido su ga ikon Allah. Sai ya karɓi sandunan ya gwada su, sai ga sandan ɓarawon ya kasa na saura da rabin taƙa. Alƙali ya fashe da dariya ya sa dogarawa su tambaye shi sai ya nuna inda ya ɓoye su.

Da Bafillacen nan ya ji abin ba ɗama sai ya ce, "Wayyo Allah, she ma Alƙali ya sa a bi ni in kawo."

Alƙali ya ce wa dogarai su ƙyale shi. Ya sa Sarkin Dogarai ya bi shi inda ya binne, ya tono ya kawo. Aka ba mai kuɗi abinsa. Alƙali ya sa aka yi wa ɓarawon nan bulala shida, aka ɗaure shi wata uku. Saura kuwa ya sallame su, suka koma rugarsu suka ba da labari. Da aka sake shi sai 'yan'uwansa suka yi ta yi masa ba'a, suna kiransa "Dogo mai gajeren sanda."

Da Haziƙ ya kai ƙarshen wannan labari sai Waziri ya ce, "Ka taɓa karanta wani littafi na Larabci da a ke ce masa Bahrul'adab ne?"

Haziƙ ya ce, "Me ka gani?"

Waziri ya ce, "Wannan labari naka na san can ya ke."

Haziƙ ya ce, "A'a, ni na ƙago abina."

Waziri ya ce, "Kada ka ja wata gardama da ba ka da gaskiya cikinta. Abin da ka sake cikin suna biyu ne kaɗai. Na farko, ka ce Filani ne, na biyu, ka sa wa mai gidan da suka sauka suna Sarkin Fawa. Ban da waɗannan ba abin da ka sake. Ka dai yi koƙari da ka hardace da kyau haka."

Haziƙ da ya ji ba ya da gaskiya sai ya yi shiru, kada a nemo littafin a buɗa a gani ya ji kunya.

Da aka yi shiru Waziri ya ce wa Haziƙ, "Bari in gaya maka akasin labarin da ka bayar."

## Ba Gaskiya Ba Ce A Bar Biɗa Ga Shari'a, Kai Dai A Samo Sa'a

Wata rana wani baƙauye ya labta wa jakinsa itace, ya nufo gari don ya sayar. Yana yawo, sai wani mutum ya kira shi ya kai icen gidansa. Da zuwan baƙauye aka yi cinikin ice, ya sallama, aka ce ya sauke ya shiga da shi cikin barga.

Baƙauye na kunna kai zaure na biyu, sai ya ji ƙanshin mai ya buge shi. Ya duba haka sai ya ga ashe mai gidan ne aka kawo masa abinci mai mai ya ke ci. Ga miyan nan sai mai ƙundun, da kaza a bisa tuwon.

Baƙauye ya tsaya da kayan ice yana kallon mai gidan nan yana mamaki. Da mai gida ya ga haka sai ya ce, "Kai, je ka ka ajiye icen ka zo mu ci, kada ka sa in ƙware a banza."

Baƙauye ya ajiye kayan icen, ya zo ya zauna, suka fara cin abinci, kafin mai gida ya kai loma guda shi ya kai uku. Da ya ƙoshi ya wanke hannu, ya dubi mai gidan nan, ya ce, "Dan'uwa, don Allah wace sana'a ka ke yi da ka sami wannan arziki haka? Ni yanzu yau shekara talatin ke nan na ke ice, amma da rana ɗaya ban taɓa cin abinci mai daɗi irin wannan ba."

Mai gida ya ce, "Ni? Duba na ke yi."

Baƙauyen nan ya ce, "Ni in ina so in koyi duba, na iya?"

Mai gida ya ce, "Ka iya mana, ai ba wuya."

Baƙauye ya ce, "Don Allah gaya mini yadda zan yi."

Mai gida ya ce, "Sai ka sayad da jakan nan naka duka, ka sayi riga baƙa da fara, ka sa. Ka sayi rawani ɗan kura da wando buje, ka sa. Sa'an nan ka sayi wani littafin Larabci da a ke kira Alfu laila. Ka kuma sami wani katako ka sa a rubuta maka a bisansa 'Nine Sarkin Duba Malam Lamiri, Mai-gani-har-hanji, ka kafa a ƙofar gidanka."

Da baƙauyen nan ya ji haka, sai ya yi tsammani gaskiya ne. Yana komawa gida sai ya aikata duk yadda mai gidan nan ya gaya masa. Mutanen ɗan kauyensu da suka ga haka sai suka yi ta yi masa dariya, suna yi masa ba'a a kan wannan wautar da ya yi. Gogan naka kuwa shi bai kula ba, kullum da yamma sai ya ɗauko Alfu lailan nan ya riƙa buɗawa, yana mui mui da baki. Yau da

gobe har ya sami wani shafi da ya fi ƙaunar ya buɗa kullum, wanda ke da waɗansu zane-zane masu kyau.

Ana nan, ran nan wani maƙwabcinsa ya aza wa jakansa ice, ya nufi gari. Yana isa, sai ya tarar ana ta jaje an yi wa wani attajiri satar jaka uku. Da mutumin nan ya ji haka wai shi ba'a sai ya tafi wurin attajirin nan, ya ce, "Akwai, wani mai duba a ƙauyemmu wanda a ke wa kirari, Malam Lamiri, Mai-gani-har-hanji," in da za ka tafi wajensa na tabbata ya iya nuna maka ɓarawon nan." Sai ya tafi abinsa yana ta dariya.

Attajirin nan da ya ji haka, ya hau motarsa sai ƙauyen da Malam Lamiri ya ke. Da zuwa ƙofar gidan ya ga an rubuta, 'Ni ne Sarkin Duba, Malam Lamiri, Mai-gani-har-hanji.' Sai attajirin nan ya fara mamaki, yayi sallama. Malam Lamiri ya fito, yana riƙe da Alfu laila a hannu yana buɗawa. Attajirin nan ya faɗi ya faɗi abin da ke tafe da shi duka.

Lamiri ya ce, "Sai mu tafi gidan naka mu gani." Ya kira wani ɗan ƙanensa ƙarami, suka shiga motar tajirin, suna zazzare ido, don ba su taɓa shiga mota ba. Jim kaɗan sai ga su garin. Aka kai su wani zaure can kusa da ƙuryar gida, aka ajiye. Suna nan zaune, baƙauye na ta tunanin ƙaryar da zai shara in an tambaye shi, sai ga abinci attajirin nan ya sa wani baransa ya fara kawowa. Ko da ya zo ya ajiye, ya fita, sai baƙauyen nan ya ce wa ƙanensa, "Wannan shi ne na fari." Yana nufin wannan shi ne abinci na fari da aka kawo.

Ashe bawan nan na maƙe na ji. To, yana ko cikin ɓarayin da suka saci jaka ukun. Sai ya yi tsammani Lamiri ya gane shi ne, har ya ke cewa shi ne na ɗaya. Saboda haka ya nufi wajen 'yan' uwansa waɗanda suka gama kai suka yi sata tare, ya ce, "Ai na ga asirimmu zai tonu, malamin nan ya gane ni da na shiga da abinci."

'Yan'uwansa suka ce, "Yaya ke nan?"

Suna cikin shawara, sai attajirin nan ya yi kıran guda ya shiga. Sai ya ba shi ruwan sha a rufe cikin kwano, ya ce ya kai wa Lamiri a zaure. Yana ajiyewa, ya ba da baya, sai Lamiri ya ce wa ɗan ƙanen nan nasa, "Ka ga na biyu." Yana nufin ruwan nan abinci na biyu ne. Ashe shi kuma yana maƙe yana ji, ya je ya gaya wa 'yan'uwansa, duk idonsu ya raina fata.

Suna nan suna shawarar gudu ke nan, sai attajirin ya sake yin kira. Bara na uku ya tafi, aka ba shi ruwan wanke hannu ya kai wa Malam Lamiri. Yana shiga, ko da ya ajiye ya fita, sai Lamiri ya ce wa ƙanensa, "Ka ga na uku ba? Wannan tafiya ta yi sa'a." Watau shi nufinsa, sun yi sa'a tun da suka sami abinci. Baran nan ko na tsammani nufin ya ke, ya yi sa'a tun da ya gane su. Ya koma ga 'yan'uwan sa ya gaya musu haka.

Da suka ji sai suka ce, 'Ko gudu muka yi, ba mu tserewa. Abin da ya fi sai mu je mu kira malamin nan, mu roƙe shi Allah da Ma'aiki ya rufa mana asiri. Mu nuna masa inda muka ɓoye kuɗin, mu roƙe shi ya nuna kuɗin, amma kada ya nuna mu. Kome ya ce mu ba shi mu ba shi." Sai suka tafi suka kira Lamiri waje guda, suka bayyana masa abin da su ke ciki duka. Suka kuma nuna masa inda suka ɓoye kuɗin, suka ce in ya yi alkawari ba zai tona su ba, za su ba shi fam ashirin.

Malam Lamiri ya yarda, suka ba shi kuɗi ya ƙulle, ya koma zaure ya zauna. Da attajiri ya zo, Malam Lamiri ya ɗauki littafi yana buɗawa. Can ya nisa, ya ce, "A je wuri kaza a duba, a gan su, ko anini ba a taɓa ba." Ko da aka je aka tarad da su cif. Sai attajiri ya yi farin ciki matuƙa, ya kawo fam ashirin ya ba Lamiri. Ya sa shi cikin mota ya kai shi gida, ya ce ko yaushe ya riƙa zuwa suna gaisawa.

Da Malam Lamiri ya ga ga shi yanzu-yanzu har ya kai ga fam arba'in tsaba, sai ya tashi ya nufi gidan mutumin nan da ya koya masa yadda a ke duba. Suka gaisa, ya ce, "Ba ka sani ba, ɗan'uwana, ashe dai duba ba shi da wuya. Jiya-jiyan nan sai fam arba'in. Ga sule hamsin kai kuma na kawo maka ka sayi ice. Na gode."

Mutane suka ce, "Wannan lalle ya sami sa'a hakika. Ga shi ya tashi da fam arba'in ris."

Alƙalai suka ce, "Haziƙ goma, waziri—" daga nan sai Sarkin Sirika ya yi farat ya katse wa Alƙalai magana, ya ce "Kai, mu ba mu son irin daraja-darajan nan taku. Ko ba a rubuta ba mu ba mu iya tunawa?" Sai ya tashi, ya karɓe allon ya goge rubutun da ke ciki, ya jefar.

Sarki Abdurrahman ko da ya ga haka, sai ya ce me zai yi ba dariya ba. Aka watse. Da aka isa gida Sarkin Sirika ya ce wa Haziƙ, "Yanzu sai ka saki jikinka, ko nasa sun fi daɗi, in an kare sa'ad da za mu koma gida, in aka zo a faɗi wanda ya fi, ba na yarda a ce kai ne baya. In dai ba a ce kai ka fi ba, sai dai a ce kuna daidai."

Haziƙ ya ce, "Ai don wannan ba kome. Allah dai ya kai, mu gobe. Ai da ma masu karin magana sun ce, "Ta safe ta raggo, in rana ta yi sai mu mutanen Sarki."

Da gari ya waye aka taru, sai Haziƙ ya kama aiki ya ce, "Af, Allah ya ba ka nasara, tun da na ke ba da labari har yau ban taɓa ba da na ɓarayi ba. Ka san ko na yi babbar mantuwa."


Waziri ya ce, "A'a, tsaya, mu ba mu son labarin ɓarayi."

Hazik ya yi burwaya, ya kaɗa fiffike, ya ce, "Ayya! Don me ka ce ba ku son labarin ɓarayi? A cikin labarurrukan nan na duniya har akwai waɗanda suka fi na ɓarayi da 'yam fashi sha'awa da mamaki?"

Waziri ya ce, "Dalilin da ba na sonsu, sa'ad da muna yara iyayemmu kan rika hana tsuntsaye ba mu labarun ɓarayi, wai don kada mu koyi dabarar sata. Ko da na ke ba da labari kada ka yi tsammani zuba su na ke yi tsuu, ban san abin da na ke yi ba. Kafin in ba da labari sai na auna wanda ko bayana ba za a zarge ni ba a kansa. Ko da ya ke dai an ce duniya ba a iya musu, tun da na ke ba mutane labari har yau ban taɓa ba da na mata ba, don tsoron yin mugun baki. Kuma ban da labarin Annabi Sulaimanu da na bayar sau ɗaya, har yau ban taɓa ba da labarin wani Annabi ba, ko da su ke duk ra'asan su ke a gare ni. Tsoron kada waɗanda ba su sani ba su ji su ce saɓo na ke yi, shi ya hana ni takalar labarunsu, ko da ya ke sun fi kome daɗi. In ko kana so ka ba da labarin ɓarayi, sai ka ba da na zamanin jahiliyya, waɗanda ko dabarun da su ke yi suna sata in an gaya wa mutanen yanzu da idonsu ya waye, sai su yi mamakin yadda mutanen da ke yarda a yaudare su da irin waɗannan dabaru."

Sarkin Sirika ya ce, "Wannan magana gaskiya ce." Waziri yana duban Hazik tsurut, yana yi maŝa dariya.

Da Hazik ya ji haka sai ya ce, "Ai ko da ma ni ba irin waɗanda ke ɓata halin mutane na ke so in yi ba."



Waziri ya ce, "To, gaya mana labari guda na ɓarayin lokacin jahiliyya mu ji, in da daɗi nan gaba a kara, in ko ba daɗi daga wannan a rufe."

Hazik ya kaɗa kai ya ce, "Hakanan ne."

## Labarin Sarkin Noma Da 'Ya'yansa

A cikin lokacin jahiliyya akwai wani manomi wai shi Ɗan'ani, yana da 'ya'ya uku maza. Babban ana ce masa Jimrau, mai bi masa Kosau, ɗan ƙaramin kuwa Nomau. Da suka isa mutane sai ya tara su, ya ce, "Yanzu ni kun ga na tsufa, saboda haka na yarda muku kowa ya shiga duniya ya kama sana'ar da ya ga za ta fisshe shi. Yau kun ga ɗaya ga watan Salla Babba, na sallame ku. Bayan kun ɗaya ga wannan wata, in Allah ya sa muna numfashi, ina so duk ku taru nan, mu ga abin da sana'ar kowa ta ba shi. Na gafarta muku duniya da lahira. Allah kuwa ya gama fuskokimmu da alheri."

Yara suka je suka roƙi gafara ga uwayensu, suka fita, ba su san inda za su ba. Suna fita ƙofar gari, sai suka kai ga wata magama huɗu nan ƙofar garin. Wata hanya ta nufi gabas, wata ta nufi arewa, wata ta nufi kudu, ta yamma kuwa ita ce wadda su ke bisa, watau mai shiga gari.

Da suka isa wurin, sai Jimrau ya ce wa ƙannensa, "Mu tsaya nan, kowa ya kama hanyarsa. In ranan nan kuma ta kewayo baɗi, in da rai, ko ina mutum ya ke ya yi ƙoƙari walima ta yi masa nan, mu koma ga baba gaba ɗaya yadda muka fito."

Saura suka ce, "Allah dai ya ba mu rai da lafiya!" Suka yi sallama da juna suka rabu, ko wanne na hawaye.

Nomau ya kama hanyar da ta nufi arewa. Kwanci tashi, yana cikin tafiya sai shawarce-shawarce ya ke yi, bai san sana'ar da zai faɗa ba. Ya yi shawarar noma, ya ga in don noma da bai tsaya gida ya yi ba? Ya watsad da wannan. Ya yi shawarar saƙa, ya ga ba ya iya jure wa taurin gindi. Ya ce kiɗa, ya ga ba ya iya haushi. Ya ce jaura, ya ga ba ya iya kwana layi. Kai, ko wace sana'a ya kawo a ransa in ya ga wani abin da ya yi mata cikas sai ya watsar, ya gaji ya ce, "Kai, duk sana'ar da ta fara taron gabana, ita zan kama."

Yana cikin tafiya, ya kai tsakiyar dajin nan, sai ya ga hadari ya kama ka'in da na'in, ya rasa inda zai shiga ya fake. Yana 'yan dube-dube ko ya sami wani ɗan kogo, sai ya ga wata 'yar hanya,

ya bita yana cewa, "In ka ga hanya dai, in ba ta kai gida ba, ta kai rafi."

Yana cikin tafiya, can gabannin tasowar ruwa sai ya kai wani ɗan gida shi kaɗai ƙwal cikin daji. Ya isa, ya yi sallama, sai wata tsohuwa ta fito, ta ce masa, "Kai samari, makuwa ka yi? Hala ba ka san inda ka zo ba ne. Nan gidan ɓarayi ne. Kama gabanka tun da girma da arziki, kafin su dawo."

Nomau ya ce, "In kama gabana in je ina cikin wannan ruwa? Da in tafi wani naman daji ya cinye ni a banza, ai gwamma in tsaya nan 'yan'uwana mutane su kashe ni. Ko ba kome, in sun kashe ni lalle sa rufe ni, ko don kada in yi musu wari."

Tsohuwa ta ce, "To, ga zaure nan, zauna." Nomau ya shiga zaure ya harɗe. Yana nan zaune jim, sai ya ji tim tim tim, ɓarayin nan sun dawo. Ga su ƙatta su goma sha huɗu ribɗa-ribɗa. Da suka gan shi sai babban ya ce, "Kai samari, daga ina?" Zai amsa musu, tsohuwa ta tsattsare ta gaya musu abin da ta gaya masa da isowarsa, da kuma shi abin da ya ce. Suka sake tambayarsa dalilin zuwansa nan, ya kwashe duk ya gaya musu, har da yadda hanya ta kawo shi nan.

Babban ya ce, "Tun da ya ke haka ne, ba mu cutarka. Gobe sai mu sa ka hanya ka yi gaba."

Nomau ya ce, "In dai ba kun ƙi yarda da ni ba, nan na ke so in zauna tare da ku. Da ma na ce sana'ar da na fara samu, ita zan bi. Tun da ko sata ta fara bayyana gare ni, ita zan yi. Da ma baba ya ce kome muka so mu yi."

Ɓarayi suka ce, "Ka iya sata? Ba fa sana'ar raggo ba ce, ba ko ta 'ya'yan kirki ba ce, ba ta kuma masu tausayi da jinƙai ba ce, ba ko ta masu gudun azaba ba ce. Sana'a ce ta taɓaɓɓu waɗanda Shaiɗan ya mallaki zuciyarsu. In ƙana iyawa, to, kome ya faru gare ka duniya da lahira kada ka yi kuka da ɗayammu."

Nomau ya ce ai ubansa ya ce ko wace sana'a ya ke so ya yi. Ɓarayi suka ɗauke shi kamar yaronsu. Ko yaushe inda za su sata duk sai su je da shi. Sannu sannu har shi ma ya zama gwani. Suna nan, ka san sata ba ciniki ba ne, ran nan sai rana ta ɓaci wa Sarkinsu, ya taryi wani Buzu wanda ya fi shi ƙarfi, wai shi yana taƙama ba abin da ke sonsa.

Buzu ya zare wuƙa ya daka wa Sarkin Ɓarayi, wuƙa ta karye uku. Sarkin Ɓarayi ya zaburam masa, Buzu ya zare takobi ya cira zai ɗauke kansa, ruwan takobi ya faɗi can gefe ɗaya kyangyaran.

Da Buzu ya ga ya yi amfani da makaman da ke gare shi, duka ba wanda ya yi, sai ya ce, "Hi namiji, galla in ka ci maganin ƙarfe, ka ci na ƙarfi ne?" Sai ya tuɓe, suka rifta da kokawa. Buzu ya fi Sarkin Ɓarayi ƙarfi fat. Ya ɗauke shi ya yi ƙoli-ƙoli da shi,

ya buga ƙasa ya haye, ya take hannuwan, ya kama kan kafiri ya murɗe, ya wuce ya bar shi nan matacce.

Da 'yan'uwan suka komo maɓoyarsu, suka yi jiran Sarki ba su ga ya dawo ba, sai suka bi sau. Suna zuwa sai suka tarad da shi kwance matacce. Suka kinkima suka kai gida suka binne, suna cewa, "Yau rana ta ɓaci wa 'yam maza." Ba wanda ya sake ko tuna shi, balle ya yi masa kuka. Da ma duk taron sakarai ne kiṟa mini shashasha, in ka ga barkatai ku taho tare.

Ko da gari ya waye sai suka shiga shawarar wanda za su wa sabon Sarki. Kowa ya ce shi za a ba. Daga nan sai tsohuwan nan ta ce, "Ai wannan ba abin zafi ciki. Sai ku fita, duk mai jin kansa ku sami wani abu ku gwada. Wanda aka ga dabararsa ta cancanta a ba shi, a ba shi."

Ɓarayin suka ce, "I, ai ko kina da gaskiya." Suka yi shiri kamar waɗansu mutanen kirki, suka fita suka nufi gari. Suka je bakin kasuwa suka zauna. Suna na zaune, sai ga wani mutum ya fito da jakar kuɗi a hannu ya nufi gidansa. Babbansu ya dubi 'yan'uwansa, ya ce, "Wanda duk ya sace jakar kuɗin nan yanzu da rana, ba da ya ko kashe mutumin nan ba, kun san ya isa a yi masa Sarkin Ɓarayi?"

Wani nan ciki ya ce, "Wannan ai ba ko ja. Ban da aljanni wa zai iya raba mutumin nan da jakan nan yanzu da rana ƙiri-ƙiri?" Ya dubi saura ya ce, "Ko kuwa da magagaci?"

Saura suka ce, "Don dai taƙamar sai da rai, mutum zai sa kansa a wahaia haka a banza?"

Nomau ya ce, "Ni ƶan yi ƙoƙari. Da rashin tayi a kan bar araha." Ya tashi ya bi mutumin tinkis tinkis har gida. Ya sami wuri ya maƙe, yana kallon mutumin nan.

Ko da mutumin ya kai ƙofar ɗakinsa, sai ya ajiye jaka daga waje cus, ya ce wa matar ta kai masa ruwa bayan ɗaki zai taɓa. Ta ɗebi ruwa ta bi shi da shi bayan ɗaki. Sai Nomau ya zo nan da nan ya sure jaka ya gudu. Ya kai wa 'yan'uwansa, ya ce, "Ga ta, da ma wuyar wuri ba mu zo ba." Ya gaya musu yadda ya yi duka.

Ɓarayi suka dubi jaka, suka yi ta al'ajibi. Daga nan sai wani mai tsananin hasada a cikinsu ya ce, "Af, wannan ai ba ka yi kome ba, domin yanzu matar na can zai yi ta dukanta ya ce ita ta ɗauke. In dai ka yi dabarar da ka kuɓutad da matan nan daga zargi, sa'an nan kuma ka dawo da jakar, ba ja kai ne Sarkimmu."

Saura suka ce, "Gaskiya ne, gaskiya ne."

Daga nan sai Nomau ya ɗauki jaka ya koma. Ya tafi har ƙofar zauren mutumin nan ya shiga, ya tsaya yana saurare, sai ya ji mutumin nan na ta zagin matar, yana cewa lalle ta nuna masa inda ta kai, in ba haka ba ko yanzu su gamu.

Ɗa Nomau ya ji haka sai ya yi sallama, mai gida ya fito yana zage-zage. Ko da ya zo zaure, sai ga jakar kuɗi hannun Nomau. Ya buɗe ido yana duba, sai Nomau ya ce' "Mutumin da ka zauna rumfarsa a kasuwa ya aiko ni, ya ce wai in kawo maka jakan nan taka da ka manta a rumfa. Ya ce in gaya maka ya kamata ka riƙa lura da kuɗi, ba dukan mutane a ke amincewa da su ba. Da sun faɗa mugun hannu ai da sun ɓata ke nan."

Mutumin ya bushe da dariya, ya yi ajiyar zuciya, ya ce. "Gaskiyarsa." Ya miƙa hannu zai karɓa, yana cewa, "Bari in je in kawo maka tukwici."

Sai Nomau ya ƙi miƙa masa, ya ce, "Ina fa zan ba ka, a zo a ce ban kawo ba? Ko kuwa a ce na kwance na ɗiba. Yanzu ba abin da ya fi sai ka shiga ka yiwo mini 'yar wasiƙa Shaida, ka zo ka ƙidaya, in sun cika ka ba ni wasiƙar in kai masa."

Mai gida ya ce, "Gaskiyarka, amma 'ya'yan kirki irinku ai ba a zarginsu ga wannan. Tsaya dai mu yi yadda ka ce." Ya ruga gida ya ɗauko tawada da takarda, sai Nomau ya fice da jaka.

Ashe sauran ɓarayin sun biyo, don su ji yadda zai yi, kada ya yi musu ƙaryar ya je. Da suka ga ya fito suka tare shi, suna yabonsa a kan wannan hikima. Suka nufi gidansu, suka yi masa Sarkin Ɓarayi.

Da mai gida ya fito bai ga Nomau ba, sai ya ruga kasuwa ya tarad da mai rumfar da ya zauna, ya ce, "Yaron da ka aiko da jakar kuɗina da na manta a nan ya kai mini. Na ce ya miƙa mini, ya ce ba ya ba ni sai na yi masa takardar shaida ya kawo maka. Na shiga gida ɗauko takarda da tawada, na fito ban gan shi ba. Ko ya yi gajin haƙuri ne ya dawo?"

Mai rumfa ya ce, "Ni ban aiki kowa ya kai maka kuɗi ba. Wane kuɗi ma za a kai maka? Da jakarka a hannu ka rabu da nan."

Mai gida ya ce, "Ni ma fa da kamar haka na gani."

Mutanen rumfar suka ce, "Kai, nemi taimakon aljannu, su suka sace maka kuɗi suna son zauta ka! Watakila da ma kuɗin ba na sosai ba ne, irin waɗanda aljannun ke kawo wa mutane ne. Ka ko san irin waɗannan kuɗi, ko ka same su sa gudu su koma ga mai su na asali."

Mai gida ya ce, "Lalle hakanan ne." Ya nufi gidan wani malami aka yi masa laya, don kada ya motsu.

Suna nan, ran nan Sarkin Ɓarayi Nomau, ya yi kamar wata goma tare da ɓarayin nan, suka hana mutanen karkaran nan saƙat da sata. Da abin ya yi yawa, Sarki ya yi bincike ya sami labarin inda su ke, sai ya yi shirin yaƙi cif, aka dakaki maɓoyarsu da dare. Dakaru suka kewaye, aka sa wa gidan wuta. Ɓarayi suka



yiwo waje, aka bi su kama kama, aka bubbuge aka ɗaure. Sarkin Ɓarayi Nomau kuwa, da ya sami wata 'yar kafa ya ɓalla da gudu, ku tara, ku tara, ya yi musu fintinkau, wani Dogari mai kili ya sake shi ya bi shi, ya sa doki ya banke shi. Ja'irin naka sai ya yi laya, aka neme shi ƙasa ko bisa, ya sulale ya yi tafiyarsa yana haki, ko riga bai tsira da ita ba, daga shi sai ba ite da mayafin da ya kwanta da su. Da ma dami ya faɗi kan kaba, lokacin tafiyarsa gida ya yi, saboda haka ya sami 'yar sanda ya tasar wa garinsu. Ga shi nan tik ba sutura, ba ko abin sayen tuwo a hanya. Saboda haka gogan naka sai ya riƙa fizge. In ya taɓad da maciya sai ya tsaya, ya ce a sa masa abinci na taro ko ńa kwalo biyu. Da ya ci ya ƙoshi sai ya tashi ya ɗauki sandarsa ya sata, sai wuce. In mai

tuwo ta tambaye shi kuɗi sai ya zura a guje, ya ce, "Biyo ni ki karɓa!" Kama kama ya tsere. Haka ya yi ta yi har ya isa.

Sarakuna suka ce, "A, a, a! Ashe haka labarin ɓarayi ke da daɗin ji, Waziri ka hana a gaya mana su?"

Waziri ya ce, "Da ma akwai abin da ya fi labarin ɓarayi daɗi? Waɗansu ne da ba su iya ba da su ba su ke faɗin waɗanda za su yiwu a ƙi a koyi sata. Kamar irin wannan daga farko ya yi kyau, amma daga baya ya so ya koma yadda ba mu so ba wajen satar jakan nan. Amma duk da haka ba laifi, ya yi ɗan dama."

Haziƙ zai ci gaba da ba da labarin su Jimrau da Kosau, Alƙalai suka ce, "Bari hakanan, Waziri kuma ya ba da wani sa'an nan gobe ka ci gaba."

Haziƙ ya ce, "To, Waziri, gare ka. Ci gaba."

Waziri ya fara:

# Da Muguwar Rawa Gwamma Kin Tashi

Akwai wani Sarki wanda ya ke da wata Jakadiya wadda ya amince da ita iyakar amincewa, kuɗinsa ma duk ita ta ke ajiyewa. In yana son wani abu sai ya aika kawai ta ba shi.

Suna nan haka kullum in an yi lissafin kuɗi sai ya ga suna saurin ƙarewa. In ya lissafta duk abin da ya kashe cikin yini ya sami kamar fam biyu, in ya shigo ya tambaye ta sai Jakadiyar nan ta ce fam biyar ko shida. Duk abin ya dami Sarki, amma bai bayyana mata ba, don ya tabbata ita dai ba ta ɗaukar ko anini, sai fa in ya ba ta.

Saboda haka ya ce mata, "Daga yau zan riƙa karɓar kuɗin nan sau ɗaya kullum, in zan karɓa sai in karɓi abin da zai ishe ni bukata gaba ɗaya in ajiye cikin aljihuna. Gobe kuma in sun ƙare, ki ba ni waɗansu. Ba zan aiko kowa ba, ni zan zo da kaina. In na zo sau guda, ki riƙe shi ke nan, ba na sake dawowa ran nan."

Jakadiya ta ce, "Allah ya ba ka nasara, ni ma haka na fi so, don in huta da lissafi, sai kuma mu ƙayyade yayin da za ka riƙa zuwa, don kada in riƙa fita wani wuri a lokacin."

Sarki ya ce, "Zan riƙa zuwa da lisha, sa'ad da na shigo gida, don su kwana wurina. Da gari ya waye zan fita fadanci, ba wata tsayawa ke nan. Kuma ke kya fi son ki riƙa ba ni yayin nan, don na san sa'an nan ba inda za ki ce kina son zuwa, balle in tsare ki. Ga shi kuma lokacin ba waɗansu mutanen da za su fitine ni."

Jakadiya ta ce, "To, shi ke nan, Allah ya ba ka nasara, sai a fara tun yanzu. Nawa zan ba ka?" Sarki ya ce, "Ba ni fam biyu." Ta ba shi, ya sa aljihu ya shige.

Ashe duk abin nan da su ke faɗi a kunnen wani ɗam barga ne, yana laɓe yana ji. Da Sarki ya shige ya koma ya kwanta, duk ba a sani ba kuma ashe da ɗam bargan nan ne ke zuwa wurin Jakadiya yana karɓar kuɗi yana cewa Sarki ne ya aiko shi.

Da ya ke Jakadiya ta san an amince da shi ba ta bin sawun abin da duk ya faɗi. Yau da ya ji an gane hanyarsa, ga shi an kashe ta, sai duk ya ƙume sai ka ce an hana shi gadon kuɗin kakansa. Ya koma, kwana da kwanaki yana tunanin yadda zai yi ya sami

hanya daga wannan alkawari da Sarki ya yi da Jakadiya, ya rasa. Yana nan dai kan tunani, har ran nan ya sami wata dabara.

Ka san na gaya maka shi ke satar kuɗin Sarki. Ka san wanda ke haka ba zai yiwu ya zauna ba kuɗi ba. Saboda wannan ya lura kullum Sarki baƙaƙen kaya ya ke sawa in zai fito fadanci da dare, ya shafa turare Ɗangoma. Saboda haka ran nan da ɗam bargar ya ga garin ya fara masa kurkutu, sai ya ɗauki sauran 'yan kuɗinsa ya tafi kanti ya sawo tufafi irin waɗanda Sarki kan shiga da dare, ya sayo turaren nan Ɗangoma, ya dawo gida ya ɓoye.

Da dare ya yi, Sarki na can waje ana fadanci, sai ɗam bargan ya tashi ya sanya kayan nan, ya bulbula turaren, ya nufi ɗakin Jakadiya, kuyangi sai durƙusawa su ke suna gaisuwa. Turare ko duk ya gume gida gum.

Da isarsa sai ya tarad da Jakadiya. Abinka da tsofaffi, har ta sakaya ɗan ɗakinta, barci ya fara ɗibanta. Ya matsa, ya bubbuga ƙofar, ƙwas, ƙwas, ƙwas, don haka ya ga Sarki na yi in ya tarar tana barci. Jakadiya ta tashi firgigi da gigin barci, ta buɗe ɗaki ta durƙusa, ta ce, "Allah ya ba ka nasara yanzu-yanzu na kishingiɗa, ashe har barci ya ɗebe ni. Nawa zan kawo?"

Ɗam barga ya ce, yana wani kumburi wai shi Sarki, "Fam biyar."

Jakadiya ta ce, "Fam biyar? Halama gobe za ka sallami masinjan Sarkin Kudu."

Ɗam barga ya ce, "Ina da niyyar haka." Da ma ga shi kullum yana tare da Sarki, ya saba da jin irin maganarsa, ga shi kuma gwanin kwaikwayo.

Jakadiya ta ƙirgo sule ɗari ta miƙa masa, ya sa a aljihu ya nufi waje. Jakadiya ta ce, "Har yanzu ba ku tashi ba?" Ɗam barga ya wuce bai ko amsa mata ba. Ya je ya tuɓe kayan nan ya ɓoye, ya shige cikin 'yan'uwansa ya kwanta, gabansa na ta faɗuwa kada Sarki ya sani, ya yanka shi.

Ya dawo ke nan sai aka tashi daga hira, Sarki ya shiga gida. Ya nufi ɗakin Jakadiya ya ce mata, "Ba ni fam biyu. Kai, sule talatin ma dai sun isa."

Jakadiya ta ce, "Allah ya ba ka nasara, yau halama baƙi aka yi da yawa, na ga ka saɓa yadda muka shirya za ka riƙa zuwa sau ɗaya."

Sarki ya ce, "To, sau nawa na zo?"

Jakadiya ta ce, "Sau biyu ke nan mana ko? Yanzu ba ka zo ka karɓi fam biyar ba? Watau yau fam shida ke nan fa ka karɓa da sule goma."

Da jin haka Sarki ya san abin da ya auku, lalle wani ya yiwo irin shigarsa ya zo ya karɓi fam biyar. Ga shi ba wanda ya wuto su

sa'ad da suna hira. Saboda haka ya san ba shakka 'yam bargansa ne. Amma da ya ke yana da wayo, ba ya son ya tona maganar, kada Jakadiya ta yi ta kwakwazo har ɓarawon ya ji ya ɓoye, sai ya yi murmushi ya ce, "In na karɓa sau goma, na ce ko nawa ne?" Ya wuce fuu, kamar yana fushi, ya yi waje. Ya ce a ransa, "Hakika wanda ya yi wannan aiki yanzu yana can kwance gabansa na faɗuwa. In dai cikin 'yam barga ne, bari in tafi inda su ke kwana in ƙidaya su, wanda na ga ba shi nan shi ne ɓarawon. In ko duk suna nan, wanda na taɓa na ji gabansa na faɗuwa shi zan tuhunta gobe."

Sai ya tasar wa barga, ya tarar da 'yam barga duk sun yi hululu, suna barci suna ɗiban iska. To, ana ko duhu, saboda haka ya ƙidaya duhu-duhunsu da ya ke gani, ya ga duhu ashirin da biyar, iyakarsu kuwa ke nan. Sai ya bi su yana sa hannu a ƙirjunansu yana jin yadda gaban kowa ke yi, har ya kawo kan ɗam bargan nan da ya yi sata. Ashe da ma idonsa ƙuri yana ji, ba ya barci, yana kuma kallon Sarki a sace. Ko da ya ga Sarki ya tinkaro wurinsa sai tsoro ya ƙara kama shi, ga tsoron abin da ya yi, ga tsoron Sarki ya nuho shi, watakila ko zai gane shi ne. Sai gabansa ya ɗauka ɗar, ɗar, ɗar. Da Sarki ya dafa ƙirjinsa ya ji haka, sai ya gane lalle shi dai ne ɓarawon.

Sarki na tsammani barci ya ke yi, ya yi ƙoƙarin ya duba fuskarsa ya ga ko wane ne. To, ba farin wata, shi ko ba ya son kawo fitila, don kada ya ta da wata hatsaniya cikin dare. Saboda haka ya ɗauki almakashi ya yi masa 'yar hana-salla ƙyas a gaban goshi, yadda zai iya gane shi. Ya koma gida abinsa ya shiga.

Wucewarsa ke da wuya sai ɗam bargan nan ya tashi, ya sami almakashi, ya bi 'yan'uwansa duk ya yi musu ƙi-salla a goshi daidai da nasa. Da gari ya waye suka taru suna wanke ido, wani ya dubi fuskar ɗan'uwansa, ya fashe da dariya, ya ce, "Wane, har ka fara ƙi-salla? Daga nan muka faffara, kuturu ya ga mai ƙyasfi."

Wancan gudan ya dube shi, ya ce, "Wace ƙi-salla? Kai dai da ke neman kafircewa, ai ga shi nan ka tsayar. In takalata ka yi don in nuna wa mutane ka kama hanya, to, sun gani."

Sai wani kuma ya dubi wani, ya ce, "Ai ba ku kaɗai ba kuka tsai da ƙi-sallar, har da wane, ku dube shi, ku gani. In wata jaraba ce Shaiɗan ya saukar muku da ita haka, sai mu ce Allah ya taimake ku. Mu dai muna tudun mun tsira." Ya tofar da mugun yawu, tuf.

Ashe wani can kuma ya hango fuskarsa, sai ya ce, "Kai da ka ke tofad da yawu na ƙarya ba ka ga naka nan ba? Ko kuwa don an ce gwano ba ya jin warin jikinsa?"

Wannan ya tashi da faɗa, "Ina ya ke? Ina ya ke?" Ya harare shi ya ce, "Af, to, ko kai fa? An ce wa mutanen Dumbulun su je aiki. Ba ka faɗi, ashe kai ma ka bi tafarkinsu ne? Gaskiya ka ke faɗa."

Saura suka dube shi, suka ga kuwa hakanan ne, sai suka ce, "A'aha! Yau lafiya?" Kowa ya shafa goshinsa sai ya ji ɗan askin sirit, suka yi ta tafa hannuwa.

Ɗam bargan nan ya ce, "Ba kowa, ma'askin dare ne, ba ku san aikin ja'iri ba."

Saura suka ce, "I, gaskiyarka, shi fa, shi ne fa."

Suna nan suna ta kakabin yadda ya bi su su ashirn duk ya yi musu abu ɗaya, sai ga Sarki ya fito, ya ce su yi holi. Suka yi, ba su san abin da ya arrala ba. Ya koma gabansu, fara dubawan nan da zai yi sai ya ga ƙi-salla a goshin na farko. Sai ya kama hannunsa, zai wuce da shi cikin gida ya je ya tuhunce shi, in ya ƙi faɗin gaskiya ya yanka shi, sai ya ƙyalla ido ya hango wani kuma da goshi askakke. Ya juyo nan da nan ya duba da kyau, sai ya ga ashe dukansu kowa na da ƙi-salla a goshi. Abin ya ba shi mamaki, har ya yi murmushi, don ya gane abin da ya faru. Zai yi magana sai ya ga ba shi da amfani ya ta da hankalinsa da hankalin barorinsa a banza, ba kuwa zai gane ɓarawon ba. Ya ga tun da al'amarin ya ke haka, masu karin magana kuwa sun ce da muguwar rawa gwamma ƙin tashi, sai ya dubi 'yan, barga, ya ce, "Wanda ya yi abin da ya sa na holanta ku nan ya san kansa, ya kuma san abin da ya yi. To, ya san da sani ya yi ɗaron yanka. Allah ya taimake shi, amma ya sani fa, in ya kuskura ya ƙara yin wannan ƙuru, asirinsa na tonuwa. Ba kullum a ke kwana a gado ba. Shi ke nan, ku tafi."

'Yam barga suka watse suna tambayar juna, ba wanda ya san abin da ya faru, balle su gane jawabin Sarki. Shi kuwa wannan ɗam bargan ko da ya ke ya sani da shi a ke yi, ba damar ya furta ya jawo wa kansa. Ya ma furta ai yana so, ya ga aiki da cikawa. Gidan maƙi gudi ai da kara a kan nuna.

Haziƙ ya ce, "Ai ga shi kai ma labarin ɓarayin ka bayar. In ma da wanda ke yiwuwa a kwaikwaya, wannan naka ai ya fi ko wanne sauƙi."

Waziri zai yi magana. Alƙalai suka ga in sun ƙyale su suka fara gardama, har magariba ta yi ba a tashi ba. Sai suka ce, "To, ya isa hakanan, an yi kiran salla." Duk mutanen suka watse.

Magariba na yi, Waziri ya sa aka yi toye-toye aka kai wa Haziƙ, ya ce watakila ya gaji da wahalar tahowa kullum.

Kashegari kuma da azahar aka sake cika bakin aiki. Hazik ya haye bisa wani ɗan tebur, ya shiga sana'a. Zai ci »a da labarin da ya fara na 'ya'yan Sarkin ŋoma da suka fita neman arziki. Jiya ya ba da na Nomau, yau kuwa zai ba da na Jimrau. Sai ya kama:

## Labarin Jimrau Ɗan Sarkin Noma Na Biyu

Jimrau kuwa da ya bi kudu, yana cikin tafiya, a kwana a tashi har ya kai wani ɗan gidan gona cikin dokar daji, ya sallama, aka amsa, sai ya ga wani ɗan yaro mai shekara kamar bakwai ya kunno kai, ya fito, Jimrau ya dube shi, ya ce, "Ina mai gidan?"

Yaro ya ce, "Me ka ke so da shi?"

Jimrau ya ce, "Kai dai yi mini sallama."

Yaro ya ce, "Me ka ke so na ce, ni ne mai gidan."

Jimrau ya ce, "Don Allah, samari, shiga ka yi mini sallama. Ka san na wuce wasa da kai."

Yaro ya ce, "Af, watau ka raina ni ko? Wallahi ni ne mai gidan, tambayi abin da ka ke so, ka ji kuwa na rantse."

Da Jimrau ya ji haka sai jikinsa ya yi sanyi, ya ce wa yaron, "To, in ka yarda ina so in ruruma nan, da safe in wuce."

Yaro ya ce, "Shigo mana. Wa zai ƙi baƙo?"

Jimrau ya tashi, ya kai shi wani ɗan ɗaki, ya ajiye kayansa, duk gabansa na faɗuwa. Sai ya duba gidan nan ba alamar kowa. Ya sake duban yaro, ya ce, "Don Allah, samari, kai kaɗai ke gidan nan? Ko kuwa iyayenka sun tafi gona ne, suka bar ka tsaro?"

Yaro ya ce, "Kana tsammani kamata ya yi rantsuwa a kan ƙarya?"

Da Jimrau ya ji haka sai ya ce, "In ka yarda, na ji dai na huta, ina so in ƙara gaba."

Yaro ya yi murmushi ya ce, "Ka ƙara gaba ina cikin wannan dare? Ko da safe ka tashi, kafin ka tarad da gari ka kai azahar. In tsoro ka ke ji don na ce ni ke da gidan kada wani abu ya gigita ka."

Jimrau ya ce, "To, shi ke nan." Ya kanne ya zauna. Da suka gaisa yaro ya tambaye shi inda ya yi wa tsinke. Jimrau ya gaya masa labarin abin da ya sa ya baro gida duka. Can da dare yaro ya kawo nama soyayye suka ci ya kawo abinci kuma iri iri suka naɗa. Ga abinci sabo, amma Jimrau bai san sa'ad da yaro ya yi shi ba, bai ko ga wani ya kawo masa ba. Zai tambaya yaron ya kwaɓe shi ya ce, "Tsaya. Babban abin da ba na so shi ne

tambaya, iya gani iya ƙyalewa." Jimrau bai sake cewa kome ba.

Da gari ya waye Jimrau ya ce zai wuce. Yaro ya rarrashe shi ya yi mugama. Cikin ranan nan yaro ya yi ta lallaɓar Jimrau ya zauna tare da shi, tun da ya ke dai ya ce neman arziki ya zo. Jimrau ya yarda ya zauna. Sannu-sannu yaro na lallaɓarsa har suka zama jiki. Ga abubuwan mamaki Jimrau na so ya tambaya, yaro ya kwaɓe shi tun da fari. Wasa-wasa Jimrau ya sami kamar wata goma a gidan. Duk aikace-aikacen da yaron nan ke so ya yi masa. Ya yaɓe masa gidansa kaf, ya yi masa zaure sabo, ya ƙara masa wata shigifa, ya ƙara masa taska domin ajiye abinci. Ya dai bi gidan nan duk ya gyara. Da watan nan goma suka cika, ya tambayi yaro yana so ya sallame shi ya koma garinsu. Ya gaya masa ya yi wa ubansa alkawari bayan shekara guda zai koma. Yaro ya yi masa godiya mai yawa, ya kawo kyanwa ya ba Jimrau, ya ce, "Ga arziki nan, na sallame ka."

Ko ɗa ya ke Jimrau ya raina wannan 'yar kyanwa, a ce wai ita ce sakayyar aikin nan da ya sha, duk da haka tsoron al'amuran yaron nan ya sa ya ƙi nuna alamar rainuwa ga fuskarsa. Ya yi masa godiya mai yawa, sai ka ce jaka guda ya ba shi. Ya ɗauki kyanwa zai tafi, yaro ya ce, "Tsaya. Da na yi tsammani za ka raina kyanwan nan ne, amma yanzu da na ga ba ka raina ba, ka yi murna da ita, zan gaya maka duk amfanin da za ta yi maka, da kuma inda za ka je da ita ta yi maka amfanin."

To, akwai wata dodanniya wadda ta ke tare fatake, tana kashe su ta cinye, ta ƙwace kayan, ta tara dukiya mai yawa da kuɗi jakunkuna a gidan jibge. Yaro ya kwashe labarin dodanniyan nan da yadda ta ke rikiɗa ya gaya wa Jimrau, ya kuma gaya masa dawan da ta ke, ya ba shi dabarun da zai yi duka, kyanwan nan ta taimake shi ya sami nasara ga dodanniyan nan, ya kashe ta ya kwashe dukiyar da ta tara.

Jimrau ya yi godiya, ya yi shiri ya nufi dawan da dodanniyar ta ke, yana cewa a ransa, "Mahaƙurci mawadaci, in dai abin da yaron nan ya faɗi gaskiya ne, bana wannan dodanniya ta gamu da gamonta."

Da abokan tafiyarsa suka ga kullum yana fama da ɗaukar kyanwa sai suka ce masa, "Me za ka yi da kyanwan nan girin-girin haka kullum?"

Jimrau ya ce, "Idon matambayi." Sai suka shafa masa lafiya.

Da suka kawo mararrabar zuwa gidan dodanniya, suna sauri su surare su wuce, sai suka ga Jimrau ya ɗauki hanya ya nufi gidan. Abokan tafiyarsa na mamaki, sai suka ƙara mai, kada wani abu ya same shi ya ce ya san su.

Da ya isa tungar da azahar sai ya nufi gidan dodanniya, suna

sauri su surare su wuce, sai suka ga Jimrau ya ɗauki hanya ya nufi gidan. Abokan tafiyarsa na mamaki, sai suka ƙara mai, kada wani abu ya same shi ya ce ya san su.

Da ya isa tungar da azahar sai ya nufi gidan dodanniyar, duk 'yar kyanwar nan tana ɓoye. Tun a kan hanyar ya ke ganin ƙasusuwan mutane bargaja. Ya yi sallama, dodanniya ta fito haƙoran nan zago-zago. Jimrau ya durƙusa ya gaishe ta, ta tambaye shi inda za shi da inda ya fito, tana murna, tana lashe-lashen baki, tana ce, "Maraba gasasshe!"

Jimrau na cewa, "Mhm." Ya dube ta, ya ce da ma gareta ya zo tun daga ƙasar Sudan. Ta tambaye shi abin da ya zo nema garin tun daga can.

Jimrau ya ce, "Labarinki ne fatake ke barbaɗawa ko ina har ya kai Sudan, suna cewa wai kina iya rikiɗa kome ki ke so. Saboda haka ne na zo in gani ko gaskiya ne, don an ce gani ya kori ji. Ni ban kula ba da ki kashe ni, muddin dai na ga abin mamaki."

Da dodanniyan nan ta ji haka ta san shahararta ba inda ba ta kai ba, sai ta yi kyakkyewa, ta dubi Jimrau kuma ta ga alama ya yi mai, sai murna ta ƙara kashe ta. Ta sake dubansa, ta ce, "To, kada fa ka ji tsoro, kai ɗin ma yanzu ka ga abin da ka ke jin labarinsa duk ya bazu a duniya. Duk yadda ka ji an faɗi labarina sai abin da aka rage. Ni ce Dandaƙwarya, Dodanniya Uwar Dodanni!" Nan da nan ta girgiza jikinta, sai ta zama giwa shirim a cikin zauren da su ke. Ta sake girgizawa sai ta zama zaki, sai kura, sai ɓauna, sai kanki, har da su jimina. Da ta gama ta koma mutum sosai yadda ta ke da. Jimrau ya dube ta, ya ce, "Ai! Wani abu sai mai shi. Yanzu kina iya rikiɗa ƙananan dabbobi kamar su ɓera ko?"

Dodanniya ta ce, "Af, ɓeran me kuma? An rikiɗa giwa balle ɓera?" Sai ta girgiza jikinta, ta zama ɓera. Da ganin ta zama ɓera sai Jimrau ya yi farat ya saki kyanwarsa yadda yaron nan ya gaya masa. Ko da kyanwa ta ga ɓera sai ta yi tsalle ta kama shi ta kashe ta cinye. Ko da ta cinye dodanniya, sai ya ji gidan ya ɗauka "Haa! Jimrau, babu kuskure, ka yi nasara."

Da ya ji haka, da har ya sha jinin jikinsa, sai ya tuna yaron nan ya riga ya gaya masa haka zai auku. Saboda haka ya tashi ya kutsa kai cikin gidan, ya kwashe duk abin da lalatattan nan ta tara kaya kyankyandi-kyankyandi ga su nan cike da wani ɗaki, ga wani ingarmar kili, ga jakai, kamar goma sha bakwai duk ya jibga musu kayan nan, ya shiga in da ta ke ɓoye kuɗi ya tarad da su ris. Kai, ya bi kayan gidan nan dai, ko allura bai bari ba, ya ɗora wa jakunansa, ya haye dokinsa barde, ya kora su ya nufi gida, yana waƙa, bukata ta biya.



Waziri ya ce, "A gaisheka, wannan shi ne irin labaran ɓarayi da mu ke so."

Sarki Abdurrahman ya ce, "Wannan ai ba labarin ɓarayi ba ne."

Waziri ya yi dariya ya ce, "Allah ya ba ka nasara, me ya raba dambe da faɗa? Kuɗin nasa ne? Wannan ma ai ya fi ɓarawo ɓarna, bai cin sata ma har ga shi ya yi kisan kai."

Mutane suka bushe da dariya.

Ɗa aka yi shiru, shi kuma Waziri ya shiga ba da nasa labarin:

# Labarin Wani Makaho

A Bobi akwai wani makaho wanda a ke kira Bakin Makaho. Dalilin da ya sa mutane ke kiransa haka, domin wayon da Allah ya zuba masa ne. Kullum in ya yiwo bara ba ya ɓatad da kuɗin a wofi, sai ya sami wani wuri, ya yi ta tarawa har dai kuɗi suka yi yawa.

Ranar Jumma'a, da ya dawo sai ya kwaso kuɗinsa duka ya ƙidaya, sai ya ga har sun kai fam uku. Da ya ga sun yi yawa haka sai ya ji tsoron kada ya bar su a bukkarsa, wani ya zo ya sace. Saboda haka ya yi ta neman inda zai kai su, ya ga in ya ba wani ajiyarsa kuwa lalle za a zalunce shi. Yana cikin tunanin yadda zai yi da su, sai ya tuna ba inda ya fi ya ajiye su sai a masallaci, don ya sani lalle ba ɓarawon da zai yi tsammani akwai wani abu a masallaci ban da buzaye da gorunan alwalla.

Ya ga in ya tafi da azahar lalle ya sami waɗansu suna salla, saboda haka ya bari sai da rana ta yi tsaka, sa'an nan ya ɗauki kuɗinsa ya sa aljihu, ya tasam ma masallaci. Da ya isa bai zame ba sai gindin mumbari, ya tsaya tsit ko ya ji motsin wani ciki, bai ji ba. Sai ya ce a ransa, "Lalle ba kowa. Da ma me zai kawo mutum masallaci da rana tsaka haka?" Ya shafa, ya ƙwaƙwale ramin gindin mumbarin nan, ya zuba kuɗinsa, ya tafi, yana faɗi a ransa, "In na dawo mumbarin nan shi ne shaidata, ba a dai motsa shi."

Ashe duk abin da makahon ya aikata wani maɗinki na nan yana wuridi, yana kallonsa. Wucewar makahon ke da wuya, sai maɗinkin ya katse wuridi, ya ce, "Bukatata ta biya. Allah ya karɓi roƙona." Ya tashi ya tone ramin, ya kwashe kuɗi, ya yi tafiyarsa.


Kashegari wani attajiri ya fid da zakka, Bakin Makaho ya sami kamar sule biyar sadaka. Sai ya nufi masallaci da ƙaramin ɗansa na ja masa gora, ya bar shi waje, shi kuwa ya shige, ya lalubi mumbari ya tona gindinsa ba kuɗi ba dalilinsu. Ya saurara ko ya ji motsin wani, bai ji ba. Sai ya riƙe baki ya yi salati, ya ce, "Ba kome, in dai kuɗin nan halalina ne, ai ba su ɓata."

Ya fito ya tarad da ɗansa, ya ce masa, "Kai, da mu ke zuwa nan ba ka lura da wani na dubammu yana dariya ba?"

Yaro ya ce, "Ba wanda na gani yana maka dariya, sai Sanda, maɗinkin nan da ba ya ba mu sadaka im mun je bara kasuwa. Nan wajen ƙofar gidan Sarki muka wuto shi. Da na waiwaya har gwalo ma na ga yana yi maka. Ina tsammani abokin wasanka ne, shi ya sa ban ce maka kome ba, don ka hana ni tsalma baki cikin sha'anin manya."

Makaho ya ce wa yaro, "To, kai ni wajensa."

Yaro ya ce, "To." Ya ja goran ubansa har rumfar Sanda Maɗinki a kasuwa, suka tarar ya dawo daga yawo.



Ko da ganinsu sai Sanda ya ce, "Baƙin Makaho, me ya kawo ka nan ne yau, ba kuma ma ran Jumma'a ba? Ku dai makafin nan kun dami mutane da bara."

Makaho ya yi dariya ya ce, "Kai Sanda, in da-don kai kaɗai mu ke zuwa kasuwan nan, lalle da mun mutu da yunwa. To, yau ba bara na zo ba da karayarka, magana ce gare ni da kai, fito ka ji."

Sanda ya fito, suka koma wuri ɗaya, Baƙin Makaho ya ce, "Tun tuni na ke son ba ka shawara, na dakata tukun a ƙare rigimar zakka mu gani. Yau kuɗin da na ke tarawa na bara yanzu na ga sun yi ɗan yawa, saboda haka na ke so in ka yarda in ba ka su ka riƙa juyawa, kana sayen 'yan kayayyaki kana sayarwa, ka ga da ni da kai duk sai mu amfana. Yanzu ɗinki ba ya ciwuwa da damana, da ma ka bar shi sai kaka. Yau ma can inda na ke ajiya na tafi in kai waɗansu 'yam fam guda da na samu wajen zakkar da attajirai suka fid da jiya, na tarar wurin da na ajiye kuɗin

akwai mutane, saboda haka na bari sai rana ta take tsaka, sa'ad da ƙafa ta ɗauke na tafi in kai waɗannan. Gobe kuma in na je, abin da na samu daga waɗanda Sarki zai fitar, zan komo ma'ajina in ɗauki waɗancan in gama, in kawo maka. Kai na ga kana iya riƙon amana, shi ya sa na ba ka. Amma don Allah kada ka ci amanata. Ka san fa kowa ya ci amanar wani, Allah ya ci tasa."

Da Sanda Maɗinki ya ji haka sai ya yi murna a ransa, ya ce, "Subuhana lillahi, ai tsakanina da kai babu cin amana. Kai ne watakila ba ka sani ba, ai na ji labari da tsohona da tsohonka sa'ad da suna yara ba abin da ke raba su. To, gobe da azahar ina nan ina jiranka."

Baƙin Makaho ya ce, "To, Allah ya kai mu." Sanda ya raka shi, suka yi sallama. Yaro ya ja goran ubansa, suka nufi gida.

Da wucewarsu sai Sanda ya yi wa makaho gwalo daga baya, ya ce a ransa. "Bari in je yanzu im mai da kuɗin nan fam uku a masallaci, don idan an jima, da rana tsaka Baƙin Makaho ya kai fam gudan da ya ke faɗi, ya tarad da waɗannan can. Idan ya kai waɗannan, watau sun cika fam huɗu ke nan, da magariba sai in laɓaɓa in kwashe su duka, in zo in sayi turame in yi ta ɗinki. Kafin kaka kuwa ai lalle in sayi keke, in shiga cikin 'yan'uwana ina kece raini."

Nan da nan sai ya ɗauki kuɗin nan ya ƙidaya, ya ga ashe ma jiya har ya sai wa matansa zannuwa na sule goma daga ciki. Saboda haka ya tafi ya samo rancen sule goma ya gama, suka tashi fam uku daidai, ya kai inda ya tono su a masallaci, ya binne. Ya ce, "Ashe dai ba shakka abin da mutane ke faɗi gaskiya ne, dare, ɗaya Allah ya kan yi Bature. Dubi wannan baiwa da Ubangiji ya yi mini yau, in sami fam huɗu ba saye ba sayarwa." Ya kama hanya ya tafi.

Da rana ta yi tsaka, Baƙin Makaho ya komo masallaci ya tona mumbari sai ga kuɗinsa fam uku cur. Ya yi godiya ga Allah da ya nufa wannan dabara tasa ta fita. Ya kwashe ya koma gida.

Magariba na yi, Sanda shi ya riga Liman zuwa masallaci. Da aka yi salla aka ƙare, sai ya kama wuridin ƙarya don mutane su watse su bar shi, shi kuwa ya tone kuɗin. Da ya ga duk an fita, sai ya tashi ya nufi gindin mumbari, ya tona ya tona, bai ga kome ba. Sai duk ransa ya ɓaci, ba don ɓatan sule hamsin ɗin nan ba, amma don sule goman nan da ya ranto ya cika. Da zai fita ya ce, "Kai, me ma zai ɓata mini rai ga wannan? Da ma na ɗauke su, zunubin da zan kwasa na wannan bawan Allah ai Ubangiji kaɗai ya san iyaka." Ya wuce yanan tunanin abin da zai yi ya biya mutane sule goma ɗinsu.

Da gari ya waye ya yi ta jiran Baƙin Makaho har azahar ta wuce, bai gan shi ba. Sai ya tashi ya bi shi gida, ya ce, "Na zo bisa ga maganar da muka ƙulla jiya ne, ka san ni ba na son in na ce i, in komo in ce a'a."

Baƙin Makaho ya ce, "Ai ni ma yadda ka ke ɗin nan haka na ke. Kuɗin na zamani ke da ban al'ajibi, in ka duba inda ka ajiye su, wata sa'a sai ka ṭarad da su sun tafi yawo. Da yanzu fa zan kai maka, sai na tarad da duk sun fita shan iska, ba ko ɗaya, sai fa in sun dawo ka gan ni da su."

Da ya ji Baƙin Makaho ya tasar wa yi masa ba'a sai ya yi fushi, ya haura takalmansa ya tafi yana cewa, "Mutanen duniya dai yanzu Turawa sun ɓata su da wayo, ko ina ka fito musu suna maƙe suna kallonka."

Waziri na ƙare ba da wannan labari sai ga wanni mutum ya zo a sukwane, ya faɗi gaban Sarkin Sirika, ya ce, "Ai shekaranjiya da Daudu ya hau kili za shi kilisa sai ya miƙe ya ka da shi, har ya karye hannu. An tafi nemo Malam Jiyya mai ɗori, an tarar ya yi tafiya, sai ɗansa aka samu ya ɗora shi hakanan a karkace."

Da mutane suka ji haka sai duk aka yi tsit, don Daudun nan shi ne autan Sarki, ba ko wanda ya ke so kamarsa.

Sai Waziri aku ya ce, "A'aha! Ashe da na ce a aika maka kada ka bar masa dokin nan, kome nacewar da ya yi ƙin kulawa ka yi? To, ba kome, in dai ka bi abin da na ce."

Sarkin Sirika ya harare shi, ya ce, "Don Allah ka rufa mana baki nan da maganar ban haushi, kada ka ṣa in fyaɗe ka. Ko na zo da shi, ko ban zo da shi ba, ai lalle in Allah ya ƙaddara zai karye sai ya karye."

Sarki Abdurrahman ya ce, "Kada ka ƙi ta Wazirin nan nawa, bari ya taimake ka, kai ne ba ka san shi ba."

Da Waziri ya yi fushi, aka dai rarrashe shi, ya ce, "To bari in je in kawo maka taimako irin namu." Sai ya tashi fir. Jim kaɗan ya dawo da waɗansu ganyaye, ya ba Sarkin Sirika, ya ce a je a dafa su, a riƙa tsoma hannun cikin ruwan, kada a sake neman wani mai ɗori har kwana uku mu gani. Aka sa mota nan da nan ta ɗauka ta kai. Da aka koma gida mutanen Sirika suka yi ta mamakin Waziri Aku.

Haziƙ ya ce, "Ba kome, rigima ce, amma ku ce ni na gaya muku."

Yau da gari ya waye har za a huta da jin labari don wannan baƙin ciki, Waziri Aku ya ce, "Ba kome, a ci gaba, in an dakata ba a yi tawakkali ke nan ba. Dakatawa na sawa ya waiƙe ne, ko kuwa tana sa ya ƙi warkewa?"

Sarkin Sirika ya ce, "Gaskiyarka Waziri, ga shi kai ɗan tsuntsu har za ka ba da mu!" Ya dubi Haziƙ, ya ce, "To, bismilla."

Haziƙ ya gyara murya, ya ce, "Shekaranjiya na fara ba ku labarin Sarkin Noma da 'ya'yansa. Na gaya muku labarin Nomau da ya koyo sata. Jiya kuma na gaya muku labarin Jimrau da kyanwarsa ta kashe dodanniya, har saboda mutuwarta ya sami kaya mai yawa a gidanta. Yau zan gaya muku labarin babbansu, Kosau.

# Labarin Kosau Ɗan Sarkin Noma Na ƙari

Kosau kuwa da ya bi gabas, yana cikin tafiya, a kwana a tashi, ya kai wannan gari ya wuce, ya kai wannan gari ya wuce, har Allah ya kai shi Sabon Birni. Da isarsa garin, da zai tambayi gidan wani mai harka ya je ya yi barantaka, sai wata zuciya ta ce masa, "Kai Kosau, gadon gida alala ga raggo, kowa ya bar gida gida ya bar shi." Saboda haka ya tambayi gidan Sarkin Noma, aka kai shi, ya sallama ya shiga.

Da suka gama gaisuwa da Sarkin Noma, ya kwashe abin da ya rabo shi da gida duk ya faɗi. Da Sarkin Noma ya ji haka sai ya ce, "To, in abin da ka faɗi hakanan ne, zama da ni ba zai yi maka wani alfanu ba, don ni ma manomi ne, ka ko san ribar noma sai mai haƙuri. Kuma ma da ubanka na son ka ka yi noma, ai da ya bar ka wurinsa. Abin da ya fi kyau sai ka sake wata sana'a, don in ka zauna wajena an yi ba a yi ba ke nan, juyin gatar fara."

Kosau ya ce, "Ni dai gare ka zan zauna, arziki duk ga Allah ya ke."

Sarkin noma ya ce, "Hakanan ne." Suka zauna nan da Kosau, ya bauta masa iyakar zarafi. Da suka sami kamar wata tara, Sarkin noma bai ga Kosau ya yi masa wani abin Allah wadai ba, ko da rana ɗaya, sai ran nan ya kira shi, ya ce, "Ai ko lokacin komawarka gida ya kusa ko?"

Kosau ya ce, "I, zuwa saba'a wa ashirin ga watan nan na ke son in yi harama."

Da lokacin ya yi Sarkin Noma ya ce, "Yau wata tara ke nan kana bauta mini. Rana ɗaya kuwa ba ka yi mini wani abin tashin hankali ba, tun ran da ka fara yi mini aikinka na ko wace rana. Yau abin da na gani gare ka fam takwas da sule goma. Yanzu ka zaɓi ɗaya, ina da wani ɗan'uwa mai ba fatake sa'a in za su Gwanja, in kana son in kai ka ya ba ka sa'a, sai ka kai masa fam takwas ɗin nan da sule goma. In kuwa ka fi son kuɗinka, ga su, Allah ya gama fuskokimmu da alheri."

Kosau ya ce, "Tun da ya ke haka ne, baba, na fi son a ba ni sa'a. Ai malamai sun ce sa'a ta fi manyan kaya."

Sarkin Noma ya ce, "Ka fi son sa'a?"

Kosau ya ce, "I."

Sarkin Noma ya tasa shi gaba, ya kai wajen ƙanen nan nasa wanda a ke kira, Malam Lamiri, ya gaya masa duk abin da suka yi da Kosau.

Da Malam Lamiri ya ji haka sai ya dubi Kosau, ya ce, "Ai ko ka yi kasada, samari. Karɓi kuɗinka ka tafi, ƙwai a baka ya fi kaza a akurki."

Kosau ya ce, "Ni dai a raina na fi son sa'a, sai dai na fawwala maka, abin da ka ga ya fi, shi zam bi."

Malam Lamiri ya ce, "A gaishe ka samari! Sai ka tashi goɓe saba'a wa ashirin, in rana ta yiwo guda za ta fito, tun ba ta baje ba. Allah ya taimake ka. Amma ka kula da abubuwan nan uku da zan gaya maka. Na fari ko wane gari za ka shiga ka shige shi ta ƙofar yamma, in za ka fita daga gare shi ka fita ta ƙofar gabas. Na biyu, kada ka kwana wurin da ruwa ke wuya. Na uku, ka lura kuma kome tsoron da ka ke ji kada ka kuskura ka shiga gari da magariba. Shi ke nan, ga sule uku ka yi guzuri. Allah ya taimake mu." Kosau da Sarkin Noma suka fita.

Gari na wayewa, ko da rana ta yiwo guda, Kosau ya shirya, ya sallami Sarkin Noma, ya sami waɗansu fatake ya shira cikinsu. Suna cikin tafiya, ran nan sai suka kai wani gari goshin faɗuwar rana. Da har Kosau zai shiga, sai ya tuna da ƙofar da za su shiga ta arewa ce, shi ko an ce masa kullum ya shiga ta ƙofar yamma. Saboda haka ya rabu da sauran abokan tafiyarsa, shi ko ya kewaya ya tasar wa ƙofar yamma. Amma da ya ke garin na da yawa, kafin ya kai rana ta faɗi. Sai ya sami wuri nan bayan gari ya zauna har gari ya waye ya shiga, don Malam Lamiri da ya ba shi sa'a ya gaya masa kada ya shiga gari da magariba.

Yana nan zaune ƙofar gari, sai kuma ya tuna a ransa Malam Lamiri ya ce masa kada ya yarda ya kwana inda ba ruwa. Saboda haka ya ga ashe bai ga ta gindin zama ba tukun, sai ya tashi ya yi ta yawo a bayan gari yana neman wata 'yar rijiya, ko wani ɗan rafi, ya kwanta kusa da shi, har ya kai hurumin mutanen garin. Ya shiga yana ta kewayawa, yana famar neman wajen ruwa, har Allah ya sa ya yi kiciɓis da wani tabki cikin hurumin nan ya je bakinsa ya ajiye 'yan kayansa, ya kwanta. Can sai ya ce a ransa, "Da in kwana nan daji, ba gwamma in tashi in riƙa yi wa Musulmin da aka binne wurin nan addu'a ba?" sai ya tashi ya yi ta binsu yana yi musu addu'a.

Yana nan, zuwa talatainin dare ya ga hadarin ruwa ya taso, aka ko tsinke da ruwa kamar da ƙwarya. Kosau ya rasa inda zai sa kansa ya fake. Ya yi shawara ya shiga wani kogon kuka da ke nan

kusa, ya ga ba ya da girman da zai ɓoye shi. Saboda haka ya ba mutuwa kai, ya fito waje ya tsuguna yana zargin kansa da wautar da ta sa ya ƙi karɓar sulensa ɗari da saba'in, ya huta da azaba.

Yana nan tsugunne yana makyarkyata, bayan an ɗauke ruwa sai ya ga waɗansu mutane biyu sun sako wani akwati-akwati daga bisa garun birni. Da ya faɗo ƙasa su kuma suka biyo ta magangari suka fito. Suka ɗauki akwatinsu suka kai shi kogon kukar da Kosau ke shawara da ya shiga, suka jefa. Suka koma gari, guda kamar zai taka ƙafar Kosau, don ana duhu ba su gan shi ba.

Da suka wuce Kosau na tsammani ɓarayi ne suka sato waɗansu kuɗi suka ɓoye nan. Saboda haka ya tashi da murna, yana cewa a ransa, "Sa'a ta ci!" Ya je ya leƙa cikin kogon, ya zaro akwatin, sai ya ji shi jin-jin: Allah ya sa ba a kulle da kwaɗo ba. Ko da ya ajiye ƙasa, yana ɗokin zai buɗa ya kwashe abin da ke ciki, sai ya ga akwatin na motsi. Ganin haka fa ya ba shi tsoro, har ya ja da baya zai ruga. Sai ya tuna Allah ɗaya ne, ya dawo. Buɗawar da zai yi haka, sai ya ga wani mutum a kwance ciki, sai numfashi ya ke yi ɗai ɗai. Kosau ya dube shi, ya ce, "Kai taliki, mutum ko aljan?"

Mutumin nan ya ce, "Mene ne kuma na tambaya? Ku dai ku ida nufinku ku huta, amma ku rubuta takarda ku yar, don in 'yan'uwana sun gani hankalinsu ya kwanta su dangana."

Kosau ya dube shi hawaye na zuba, duk akwati ya cika da jini, sai ya ce, "Nan yanzu a hurumi na ke, waɗansu mutane suka zo da kai, ni ba ruwana. Ina nan laɓe na ga sun jefa ka cikin kogon nan. Na yi tsammani ɓarayi ne ke ɓoyon kuɗi, shi ya sa na zaro ka. Gaya mini labarinka in ji ko na iya taimakonka."

Mutumin nan ya ce, "Ni yanzu kusa na ke ga mutuwa, ba na iya ba ka wani labari. Kai dai in kana iyawa, taimakan ni daga baya in ina da sauran kwana gaba ka ji, in ko ba ka iya taimakona, don Allah ɗauki wani dutse ka fasa kaina, in iyad da mutuwa in huta."

Tausayi ya ƙara kama Kosau, ya ɗauki tsumman rawaninsa ya ɗaure wani sara da ke zubar jini a cinyar mutumin nan. Da gari ya kusa wayewa sai ya lallaɓa shi ya tafi da shi wani ɗan ƙauye nan yammacin gari, ya ce ɗan'uwansa ne, ɓarayi suka tsare su. Aka ba su ɗaki. Kosau ya yi ta jiyyar mutumin nan, har Allah ya sa ya warke sarai. Da ya ga ya warke sa'an nan ya tambaye shi sunansa, da sana'arsa, da kuma abin da ya sa wannan abu ya faru.

Mutumin nan ya ce, "Sunana dai Maikoma, sana'ata ko su. Wata rana wani ɗan tsoho gajere fari, mai ido guda, ya zo ya ce in ba shi sadaka don Allah. Na ji tausayinsa, na kawo sule, da wata

tsummar riga tawa, da wando, da hula, da rawani, na ba shi, ya yi godiya ƙwarai ya tafi.

"Dare na yi sai ya komo gidana, ya ce ni kuma me na ke so ya yi mini. Ka san kowa ba abin da ya ke so ransa illa a san shi bisa kan sana'arsa. Saboda haka na ce ni ba ni da wani buri sai ɗaya, kome ya shiga cikin komata sa'ad da na ke su ya zama kifi, ko da ganye ne, ballantana su kwaɗi masu rai. Sai tsohon nan ya yi murmushi, ya ce mini da tsakad dare wata aljana za ta zo wajena, kada in ji tsoro in tambaye ta abin nan da na ce ina so. Ya gaya mini wani ganye kuma, ya ce duk sa'ad da na so ganinta in turara shi a ɗakina, ta zo nan da nan.

"Da dare ya yi tsaka kuwa ta zo, na tambaye ta, ta ba ni wannan iko. Da sauran 'yan'uwa suka ga na fi su su, duk garin ba a maganar kowa sai ni, sai suka tasam mini har suka yi dabarar da suka rabo ni da garimmu watan jiya, don su zo da ni nan garin su kashe ni. To, su ne ka ga sun miƙo ni ta kan ganuwa. Tsammani su ke sun kashe ni, ba su san ina da sauran kwana gaba ba. Yanzu gobe daren Lahadi zan yi maka alheri guda, ni kuma. In aljanan nan ta zo wajena zan gaya mata duk wannan abin da ya faru, in ce ta taimake ka in da dama."

Kosau ya yi godiya, sa'an nan ya ce, "Ka ga tsohon nan da ka ke labari, lalle shi ne ni kuma ya ba ni sa'a, sunansa Malam Lamiri. Ko bai gaya maka ba?"

Maikoma ya ce, "Lamiri kuwa."

Kosau ya ce, "Lalle ya san haka zai faru ne, shi ya sa ya ce mini in zo don in taimake ka." Ya kwashe labarin da ya gudana game da shi da Lamiri duk ya faɗa wa Maikoma, suka yi ta tu'ajjabi.

Kafin rana ta faɗi Maikoma ya nemo ganyayen nan na turare ya ajiye. Sai da ya bari ba sauran mai motsi, sa'an nan ya tashi ya ɗauki ganyen nan ya turara. Turarawarsa ke da wuya sai aljanan nan ta fito. Ya kwashe duk abin da ya gudana gare shi ya gaya mata.

Da ta ji sai ta ce, "Ayya! Haba, gaskiya na ga ka rabu da kirana. Ina yaron da ya taimake ka? Shi ne nan ke barci? To, tashe shi, mu kuma mu saka masa, ai tun kamar wata guda ke nan Malam Lamiri ya ba ni labarinsa." Aka ta da Kosau, suka gaisa da aljana. Da suka gama gaisuwa ta tambaye shi abin da ya ke so. Ya ce shi ba ya son kome sai in ya koma gida ya zama duk abin da 'yan'uwansa suka samo nasa ya shafe nasu.

Aljana ta ɗauki wani zoben gorar ruwa daga hannunta, ta ce masa, "Karɓi, ga sakayyar aikinka nan."

Kosau ya karɓa ya sa a hannu bai san amfanin zoben nan ba, aljana ta ɓace. Ya dubi zobe, ya ce wa Maikoma, "Ko kai ka san amfanin wannan zobe? Ko na sayad da shi dai ba ya yin ahu."

Maikoma ya ce, "Wallahi ko ni ban san amfaninsa ba. Tsammani na ke da ko kuɗi za ta ba ka. Abin da ya fi da wannan shiriritar, gobe sai ka bi ni garimmu in taimake ka da guzuri, kada 'yan'uwanka su yi maka dariya."

Ƙosau ya ce, "Ai ba dama in koma baya, yanzu saura kwana uku ke nan mu gamu a inda muka yi alkawari. In ma ba zango na ci ba sai na saɓa. Yanzu dai tun da ka warke sai mu yi sallama, da asuba ni kuwa in rarrafa ko na rage hanya." Suka yi sallama har da koke-koke don sabo.

Asuba na yi Ƙosau ya tashi ya kama hanya, yana ta ƙutawa. Am ba shi sa'a, bai ga sa'ar ba. Ya yi kamar ya yad da ɗan zoben nan don haushi, ya ga in ya yad da shi ba abin da zai nuna wa 'yan'uwansa da ubansa, sai ya bari. Yana cikin tafiya, can ya kai ƙungurmin daji sai gari ya waye. Ya nemi ruwa ƙasa da bisa ya yi alwala, ya rasa, sai ya tsuguna ya bugi ƙasa ya yi taimama, ya ba da farali. Abin ka da wanda ba malami ba, bai san cire zobe a ke ba in za a yi taimama, shi sai ya buga ƙasa da shi sau biyu yana kakkaɓewa, sa'an nan ya shafa a fuska, ya shafo zira'ar hannunsa na dama ya tsettsefe yatsunsa, ya kuma shafo zira'ar hannunsa na hagu. Ko da ya fara tsettsefe yatsunsa, ya kawo ga yatsan da zoben nan ya ke ya goge shi, sai kawai kamar daga sama ya ga wani gwabjejen ƙato ya tsaya gabansa, ya ce, "Ga ni, faɗi abin da ka ke so yanzu in yi maka!"

Ƙosau bai san sa'ad da ya katse taimamarsa ba, yana tsammani ɗam fashi ne, ya ce, "Wayyo! Wallahi ba ni da ko anini. Ga kayana kuma, buɗa ka gani."

Mutumin nan ya ce masa, "Allah ya ba ka nasara, kada ka ji tsorona, ni ba ɗan fashi ba ne, aljani ne. Ni ne bawan zoben nan da ke hannunka, duk wanda ke mulkinsa shi zan wa bauta. Na ji ka murza shi, shi ya sa na fito. Umurtan ni, ka ga aiki da cikawa!"

Ƙosau na kaɗuwa, ya ce masa, "To, kawo mini ruwa in wanke ido." Rufa bakinsa ke da wuya sai ya ga aljani ya ɓace. Jim kaɗan sai ga shi da tulun ruwa. Ƙosau ya wanke ido, ya yi alwala, ya yi salla, ya tashi ya ci gaba yana cewa, "A'a! Aljanin nan wasa ya ke mini, ko kuwa da gaske ne? Bari mu gani." Sai ya sake murza zobe.

Sai aljani ya fito, ya ce, "Ga ni, umurtan ni!"

Ƙosau ya ce, "In gaskiya ce ka ke faɗi ba wasa ba, samo mini abinci." Aljani ya ɓace. Can ya dawo da kayan abinci iri iri, ya kawo wa Ƙosau. Ƙosau ya zauna ya naɗa, sai da ya kai masaɓar gatari. Waɗansu ma bai san ko mene ne ba, shi dai ya ci. To, da ma ya taɓa jin labarin irin waɗannan cikin Dare Dubu da Ɗaya,

saboda haka tsoron aljanin nan ya rabu da shi. Ya kama hanyarsa ya nufi gida, yana ta amfani da aljanin nan sa'ad da bukatar wani abu ta same shi. Da ya gaji da tafiya ƙasa ya sa aljanin ya kawo masa doki taka hau, ya ɗare ya yi ta tahowa bisansa.

Mutane suka ɗauka gaba ɗaya, "Wannan duk ya fi su sa'a."

Waziri ya ce, "Ku bar saurin yaɓo. Tun da ya ke sata ce cinikinsa, ai akwai ranar ƙin dillancin tana zuwa, ranar da hajjar Sarki ta ɓace."

Sarki Abdurrahman ya ce, "A'aha! Ka ce Jimrau ɓarawo ne, to, wannan kuma Kosau ina ya gamo da sata?"

Waziri ya ce, "In ko ba a ce wa wannan ɓarawo ba, ba sauran ɓarawo ke nan a duniya. Kuɗin da aljannun ke kawo masa da kayayyaki, saƙa su su ke yi? Ba kayan waɗansu bayin Allah ba ne na wata ƙasa su ke satowa suna kawo masa?"

Alƙalai suka ce, "Ai ko gaskiyarka. Ko cikin labari ma mutane kan ce abokin ɓarawo ɓarawo ne."

Waziri ya ce, "Aha! Ku duba mini hanya dai, makaho ya so tsegumi. Wannan labarin har ya tuna mini labarin Dauda da Ɗan'iya.

## An Ki Cin Biri, An Ci Dila

Wata rana wani ɗan sane wai shi Daudu ya shigo kasuwar Kano, sai ya tarad da wani ɗan sane kuma da ya sani yana raɓuke bayan kasuwa kamar mummuni, sai tasbaha ya ke ja.

Daudu ya dube shi, ya ce, "Ɗan'iya, wane tarko ne aka kafa nan, ba a ko son yin magana da mutane?"

Ɗan'iya ya ce, "Wane tarko fa?"

Daudu ya ce, "Hala ka sami abin da ka cika cikinka ne. Don Allah tashi mu shiga kasuwa, mu ga abin da Allah zai kawo. Ko ka ƙoshi, ba ka son na bukata? Ga shi yau na ji Fage ana shirin wani gamammen wasa, duk masu gogen Sabon Gari da masu molo za su taru.

Ɗan'iya ya ce, "Ai ni sai ku ɗauki niyya, ni na tuba da sane tun watan jiya. Ni yanzu ba na wani aiki sai ibada. In mutum bai sami abin da ya kama ba tun da sauran ƙuruciya, ai ya lalace."

Daudu ya ce, "Ka bar sane! Ai ko abin da ban mamaki. To, me ka ke ci?"

Ɗan'iya ya ce, "Ni ba na cin kome sai 'yan abubuwan da na samu daga dabaru. Ka san bakin da Allah ya tsaga ba ya hana masa abin da zai ci."

Daudu ya ce, "A, a sake, ai Kano ba ta ɗaukar waɗannan banke-banke, sai gaskiya. To, waɗanne irin dabaru ka ke ci? Kada fa a ƙi cin kare a ci dila."

Ɗan'iya ya ce, "Tun da na gaya maka na bar sata, ai na bari ne. In da ina yi in ji tsoron gaya maka, ko me? A ɓoye wa abokin kuka mutuwa? Kai dai tafi ka bar ni nan, kome ka kalato ka kawo nan in ajiye maka ka koma, don kada ka riƙe hannunka a gani."

Daudu ya ce, "Ai ko da ka kyauta." Sai ya nufi kasuwa.

Ɗan'iya ya ce, "Allah ya ba da sa'a!"

Daudu ya shiga kasuwa, ya yi ta yanko aljifan ƙauyawa yana kawowa, Ɗan'iya yana ajiye masa kayan da ke ciki. In bai sami kuɗi ya yanka ba, sai ya fige hula, ko ya zare turmi kan dillali, ya yi ta kawo wa Ɗan'iya dai, yana tara masa a cikin wani tsohon bargo.

Ko yaushe ya kawo sai Ɗan'iya ya ce masa, "Kai, yau ka fito cikin sa'ida, kama jiki! Ba shakka kome muka bari rufe kuna buɗewa. Ashe ko da muka bar abin nan mun sami magada."

Daudu ya ce, "Bari! Wai Turawa suna da dabara, sun sa 'Yan Doka. Ba su sani ba, ko duk garin nan an mai da su 'Yan Doka ba a hana mu sane, sai dai a hana ƙauyawa zuwa Kasuwa. Haba, a haife mu Kano, mu tashi Kano, sa'an nan wai a ce za a yi mana wata dabara, muna cikin Kano kuwa?"

Ɗan'iya ya cafe, "Jalla babbar Hausa, gari ba Kano ba dajin Allah! Kamisilika alfun, yaro ko da me ka zo Kano an fi ka. Sa himma ka gani, ɗa magajin baba, a bari ya huce shi ya kawo rabon baƙo! Daudu ya sake kutsawa kasuwa, ya yi ta aiki dai har la'asar sakaliya.



Da Ɗan'iya ya ga la'asariya ta yi sai ya sami wani Ɗan Doka suka gama baki. Ɗan doka ya sa masa ankwa, ya tsaya bisa kansa yana mari. Ga igiya kuma ya ɗaura masa a gindi yana riƙe. Da Ɗan'iya ya hango Daudu tafe da wadansu kaya sai ya ce wa Ɗan Doka, "Riƙa mini nan." Ɗan doka ya same shi da mari, shi ko sai wayyo, wayyo ya ke yi, yana cewa, "Ba nawa ba ne, ga mai su can tafe, ni tun watan jiya na tuba."

Da Daudu ya ji haka sai ya sake hanya. Ɗan'iya ya ce, "Ina za ka? Zo, ga kayanka."

Daudu ya ce, "Kayan wa? Na rantse har da kabarin tsawona ban ba ka kaya ajiya ba."

Ɗan'iya ya ce, "Haba Daudu, don ka gan ni haka yau rana ta ɓaci za ka guje ni?"



Daudu ya ce, "Yaushe muka taɓa wani abu tare, balle in guje maka yau? Kai kana Fage, ni ina nan Bakin Kasuwa. To, me gamin kifi da kaska? Kai dai da ka ce ka ji ka gani ku yi can."

Ɗan'iya ya ce, "Abin da ka ba ni ajiya ka yarda? Ni in tafi abin da shari'a ta yi a yi mini, a yi mini? Wuya dai maficiya ce. Ba ko ni kaɗai aka fara ɗaurewa nan birni ba."

Daudu ya ce, "Da ma ajiyar me na ba ka? Yi ta kanka, ka ji da abin da ya same ka. Zaman duniya iyawa ne, kowa tasa ta fisshe shi." Ya surare abinsa.

Ko da ya ɓace Ɗan'iya ya ce wa Ɗan Doka. "Kwance ni."

Ɗan Doka ya ce, "In kwance ka yaya? Sake magana. Yaya zan kama ɓarawo in sake shi? Don me Sarki ya ajiye mu?" Ya iza ƙeyarsa zuwa rumfar Alƙalin Kasuwa.

Alƙalin Kasuwa ya tambayi Ɗan'iya abin da ya yi. Ɗan'iya ya ce, "Allah ya gafarta malam, ina na sani? Sai dai a tambayi Ɗan Doka abin da na satar masa har ya ɗaure ni."

Alƙali ya juya ga Ɗan Doka, ya ce, "Kai, lafiya ka kamo shi?"

Ɗan Doka ya kwashe yadda Ɗan'iya ya sa a ɗaure shi ya faɗi. Ya kuma maimaita maganar da ya ji ta gudana tsakaninsa da Daudu.

Alƙali ya sa aka kwashi kuɗin nan da 'yan kayayyakin nan, aka shiga kasuwa cigiya. "Wa aka yi wa sata yanzu?" Shiru. To, abinka da kasuwa kamar ta Kano, kowa harkar gabansa ta ishe shi, ba wanda ya san Allah ya halicci wani. Kuma ma ko mutum ya ji ana cigiya, kai da aka yanke wa kamar sule goma, ka ji ana cigiyar wanda aka yanke wa fam uku da sule biyu da sisi da sisin kwabo, ka sa baki a zo a yi ta jagade-jagade da kai?

Aka karaɗe kasuwa ba a ga masu kaya ba. Alƙalin Kasuwa ya ce, "To, ni yanzu ba wata hanyar da zan bi in yi hukunci da zanni bisa kan wannan al'amari. Domin an ce zato zunubi, ko da ya zama gaskiya. Ɗan Doka, sai ka sake shi, in halinsa ne ya ƙara." Aka kwance Ɗan'iya.

Da aka kwance shi sai ya durƙusa gaban Alƙali ya ce, "Allah ya kyauta yin malam, ni kuma ina da ƙarar Ɗan Doka don ya yi mini ƙage. Ga shi kuma ya karya mini irli cikin kasuwa, sai a fitar mini da nawa alhakin."

Idanun Ɗan Doka suka ɗuri ruwa. Alƙali ya ce, "A'a, abin da ya fi, na roƙe ka dai yanzu, sai ku yafe wa juna, ka yi tafiyarka. Ɗan kaciya in bai ci kaza ba ai ba ya yin bara."

Ɗan'iya ya ce, "To, Allah ya kyauta yin malam, saboda kunyarka na yafe masa." Ya tashi ya kwashe kuɗinsa da turamensa huɗu ya fita, ya tasam ma layin da Daudu ke zaune ya tarad da shi. Da ganinsa Daudu ya fashe da dariya, ya ce, "Bulala nawa?"

Ɗan'iya ya ce, "Bulala! Haba, sa'an nan ban cika ɗan garin nan ke nan ba. Ai ga kayayyakin, da kuɗin duk an bar mini!"

Daudu ya ce, "Af, to, sai mu raba, don nawa ne."

Ɗan'iya ya ce, "Mu yi me? Mu raba? Da gaske ka ke, ko kuwa da wasa? Ai da ma na gaya maka na bar sata, mu sai dabara mu ke ci. To, ɗaya ke nan ka fara gani daga cikin dabarun da mu ke samun abinci ta hanyarsu. Kai dai ga sule biyar ka sha fura."

Daudu ya ga kada ya bar banza, ya karɓa. Ya dubi Ɗan'iya ya ce, "Lalatacce, tafi! Ba kome, sata gidan ɓarawo rance."

Mutane suka fashe da dariya, suka ce, "Lalle ko Ɗan'iya shi ne wanda ya ƙi cin biri ya ci dila." Aka watse ana mamakin 'yan Kano.

Yau da aka taru da azahar kuma sai Haziƙ ya ce "Zan ci gaba da labarin 'ya'yan Sarkin noma."

# Gamuwar Kosau Da Jimrau Da Nomau

Ranar ɗaya ga watan Sallah Babba, watau ran da Sarkin Noma ya ce wa 'ya'yan nan nasa su komo gida, sai su duka ga su sun taru a magama huɗu da suka yi alkawari. Jimrau ya fara zuwa, ya sauke kayan jakunansa a wata inuwa, ya yi musu tabaibayi suna kiwo, shi kuwa ya sami wuri ya hakince bisa wundi.

Yana nan zaune sai ya hango wani tafe yana cin ingarma. Da ya matso sai ya ga ashe Kosau ne, ya kama masa ya sauka, suka zauna suna gaisawa. Ga mutanen gari suna kallo, sun ƙi shiga don sun yi alkawari in da rai duk su taru tukuna sa'an nan su shiga.

Suna nan sai suka hango wani tafe, daga shi sai lage, ga wata umara ya saɓo yana tafe yana waƙe-waƙe. Da ya matso sai suka ga ashe ƙanensu ne Nomau. Ya zo ya zauna, suka gaisa da 'yan'uwansa. Jimrau ya dube shi, ya ce, "An yi maka fashi ne a hanya?"

Nomau ya ce, "Fashi? Ni ba wanda ya yi mini fashi. Me ka gani?"

Jimrau ya ce, "Ba kome." Ya buɗe kayansa ya ɗauko 'yar madaka, aikin nan har ga shafi, ya ba shi ya ce ya sa su shiga gari.

Nomau ya ce, "Ai! Ni ka raina abin da na samu ne? To, mu tafi, ni ban raina ba, na gode Allah. Dauki rigarka, ni abin da na samo ya ishe ni." Ya ɗauki rigarsa ya mayar kyankyandi. Suka shirya suka shiga gari gaba ɗaya yadda suka fita.

Da ma ran nan ubansu ya sa an share gidansa, an yi abinci, don yana tsammani lalle ko ba su dawo duka ba, wani daga cikinsu ya dawo. Yana nan zaune, yana duban hanya. Can sai ga su gaba ɗaya. Sarkin noma ya tashi ya rasa inda zai sa kansa don murna. Aka yi ta kinkimar kayan Jimrau ana shiga da su. Aka kama wa Kosau ya sauka. Yara suka shiga gida, kowa ya tarad da uwarsa, suka yi ta murna.

Da aka ƙare murna, mutane suka tsagaita da zuwa, sai Sarkin Noma ya kira su a turaka, yana tambayarsu labarin yadda kowa ya yi da sana'ar da ya bi. Aka fara kan Jimrau, don shi ne babba. Ya kwashe labarin ɗan yaron nan da ya yi wa bauta, da labarin

kyanwar da ya ba shi, da abin da ya gudana tsakaninsa da dodanniya duk ya faɗa wa ubansa da 'yan'uwansa. Suka yi ta tu'ajjibi.

Da gari ya waye kuma Sarkin Noma ya sake tara su, Kosau ya ba da labarin abin da ya auku tsakaninsa da Sarkin Noma, da yadda ya zaɓi sa'ar da Malam Lamiri ya ba shi, har ya zo ya sami Maikoma, ɗan sun nan da 'yan'uwansa suka bubbuge suka sa cikin akwati suka kai cikin kogon kuka. Ya kuma ba da labarin yadda Maikoma ya taimake shi aljana ta ba shi zobe. Ya bayyana musu amfanin zoben nan duka. Nan da nan, don ya gwada musu abin da ya ce gaskiya ne, ya dubi ubansa ya ce, "Me ka ke so, baba, nan duniya duka yanzu ka gan shi."

Sarkin noma ya ce, "Ina son nama soyayye."

Kosau ya dubi Jimrau ya ce, "Kai me ka ke so?"

Jimrau ya ce, "Kujerar zinariya."

Ya ce wa Nomau, "Kai fa?"

Nomau ya ce, "Layar zana."

Sarkin noma ya harare shi, ya ce, "Kai, kowa na tambayar abin kirki, kai sai ka ce wani abu wai layar zana? Sata za ka yi?"

Nomau ya ce, "Sai dai kada a ƙara. Na ce ko abin da ke ran kowa ya faɗi? To, ni abin da ke raina ke nan." Sarkin noma bai gane ba, ya ƙyale.

Kosau ya murza zobensa, sai suka ga aljani ya zo gabansa ya tsaya, ya ce, "Allah ya ba ka nasara, faɗi naka, aikatawa tamu."

Kosau ya ce, "Ina so yanzu ka kawo mana nama soyayye da kujerar zinariya in tana samuwa, da layar zana. Kana da ita?"

Aljanni ya ce, "An gama, ba abin da ba na iya kawo maka, sai abin da babu shi a duniya." Sai ya ɓace. Sarkin Noma ya buɗe ido suna ƭsammani dabo Kosau ya koyo, ba kome ba. Suna nan sai ga aljani ya dawo da dukan abin nan da aka aike shi. Nomau ya sa hannu ya ɗauki laya ya sa aljihu.

Ko da Jimrau ya kware kujerar zinariyan nan, sai suka ga wuri ya haske. Suka kewaye ta suna al'ajibi. Kosau ya ce wa Jimrau, "Ga ta, in kana iya zama ƙanta."

Jimrau ya ce, "Don Allah rufa mini asiri, kada ka sa a yanka ni. Ai ko Sarkin Sirika, wanda Alhaji Imam ya ba da labarinsa cikin Ruwan Bagaja, ba ya kwanta a wannan kujera ba." Jimrau ya sa aljani ya ɗauke ta bakinsa ƙanen ƙafarsa ya mayar. Sarkin Noma ya sa hannu suka ci abinci da 'ya'yansa, suka watse.

Kashegari kuma suka sake taruwa, Sarkin Noma ya dubi Nomau, ya ce, "In ta bi daga daga na ƙurya ka sha kashi. Ɗan autana, kai wace sana'a ka bi? Ban ga alamar ka zo da kome ba."

Nomau ya ce, "Ni ko gani na ke tafiyata duk ta fi tasu sa'a, sai

dai ni abin da na samo ya sha bamban da nasu. Wannan ko ba kome ba ne, da ma an ce kowa da kiwon da ya karɓe shi, maƙwabcin mai akuya ya sayi kura."

Sarkin noma ya ce, "Hakanan ne, kai ko wace sana'a ka yi? Kuma me ka samo?"

Nomau ya ce, "Ni sana'ar da na koyo ba cinikin raggo ba ce. Ni ilmi na koyo da wayo."

Sarkin Noma ya dafa kansa, ya ce, "Hakika ka koyo babban abu. Wane fanni ka ɗauka na ilmi? Furu'a ka koyo, ko Tasrifi, ko Lugga, ko Nahawu?"

Nomau ya ce, "Kada in wahal da kai, baba, ni ban koyo ɗaya daga cikin waɗannan fannoni ba. Ni sata na koyo. Na ko samo nasara har an naɗa ni Sarkin Ɓarayi."

Sarkin Noma ya ce, "Sata! Wa iyazu billahi! Allah ya ƙiyashe mu da wannan sana'a da ka koyo. Wane ɓatan basira ya kai ka wannan aiki?"

Nomau ya ce, "Ina laifina cikin wannan abu? Ka yarda mana kowa ya bi sana'ar da ya ke so. To, ni ko sata na ga ta fi riba, shi ya sa na ɗauke ta." Ya kwashe abin da ya faru duka tsakaninsa da ɓarayin ya faɗi.

Sauran 'yan'uwansa suka yi ta yi masa shewa, suna cewa ba su sake zama da shi. Uban ya ce, "Lalle kuna da gaskiya. In ka ga mai arziki na zama gida da ɓarawo, ai ka san ana zaman ƙarya, baƙauye ya zo birni ya tambayi masussuka an ce babu."

'Yan'uwan suka ce sai a kore shi, ko kuwa uban ya gaya wa Sarki a ɗaure shi. Sarkin Noma ya ce, "To, yaya za a yi haka, mutum ya soki cikinsa ya yi kirari?" Ya dubi Nomau, ya yi salati, ya ce, "Ka dai zama mana dungu, a bar ka ana ƙyamarka, a yanke ba a samun sabo."

Nomau ya ce, "A'a, baba! Na ga za ka kai ga yi mini baki, ka sa in lalace ba da alhakina ba. Yadda ka sawa kowa albarka ni ma sai ka sa mini, don sa'ad da za mu rabu ba ka ce mana ban da sata ba, cewa ka yi sana'ar da mutum ya ke so ya bi."

Sarkin Noma ya rasa ta cewa. Ya yafe wa Nomau, suka zauna hakanan da shi kan dole. 'Yan'uwan sai dariyarsa su ke yi, suna zunɗe, ko ina ya ratsa suna cewa, "Ko can ma in ka bibiya shege ne, ba ɗan'uwammu ba ne."

Ana nan, ran nan sai Jimrau ya ga wata 'yar Sarkin gari ya ko maƙale wa uban ba wadda ya ke so sai ita. Abinka da 'yan'uwa, ashe kuma Kosau ya gan ta, shi kuma ya nace wa uban sai a nema masa ita, kome aka ce ya yi dominta. Da Nomau bai sa baki ba, sai ya ce a ransa, "Ya kamata ni ma in sa hancina wurin neman yarinyan nan. Na san halin 'yan'uba, in sun ga na ƙyale sai su mai

da ni talaka, wai don ba ni da wuri ne.'' Sai ya ce wa Sarkin Noma lalle shi ma ita za a nema masa.

Da Sarkin Noma ya ji maganar Nomau sai ya ce, ''Ai, mai rai ba ya rasa motsi. In ba haka ba, ka ji 'yan'uwanka masu kuɗi na tsoron zuwa yin magana, balle kai mai ƙakama da sata? Sai ka ce Akware!''

Nomau ya ce, ''Tun da dai kai ka haife ni, ba shege ne ni ba, in ji yadda ka aikata wa saura lalle ka aikata mini.'' Yara fa gaba ɗaya suka tasar wa uban lalle sai ya nema musu 'yar Sarkin nan.

Sarkin Noma ya ce, ''Waɗansunku sai su dangana a bar wa guda, in yi kasada in tafi in yi masa magana.'' Yara kowa ya tsaya shi dai ba ya iya ƙyalewa, sai fa ƙarfinsa ya ƙare dole. Suka tilasta wa uban dai, har ya tafi ga Sarki ya faɗi saƙonsu gaba ɗaya. Sarki zai sa a lallasa Sarkin Noma don wannan rashin hankali da ya yi, Waziri ya ce ''Allah ya ba ka nasara, wanda ya ce yana son gama zumunci da kai ai ba maƙiyinka ba ne. Mutane kuma sun ce, ''In ka ji makaho ya ce mu yi wasan jefe-jefe ya taka dutse.''

Sarki ya ce, ''Wannan jawabi naka mai jiwuwa ne, Waziri? Amma me ka ga ya fi mu yi?''

Waziri ya ce, ''Sai a tambaye shi abin da ko wanne daga cikin 'ya'yan nan nasa ya taka da ya yi wannan magana, domin lalle ruwa ba ya tsami banza. In an sami abin da kowa ya ke ƙakama da shi, sai a jarraba shi ta hanyar da abin da aka san ba ya yiwuwa. Ka ga da ɗai ɗai sai a yi musu kora da hali wadda ta fi kora da kara.''

Sarki ya ce, ''Wannan magana taka ba ja.'' Ya sa baki ya kira Sarkin Noma (domin da Waziri zai yi magana ya kori mutane ne). Da Sarkin Noma ya shigo, Sarki ya tambaye shi abin da 'ya 'yansa suka taka, da suka kasa neman daidai da su sai suka tinkari 'yarsa su yi kasayya.

Sarkin Noma ya ce, ''Ba abin da babban ya taka sai kuɗi. Ka ji an ce yaro da gari abokin tafiyar manya. Ma bi masa kuwa duniyan nan kome aka sa shi yana iya yinsa. Karamin kuwa Allah ya ba ka nasara, ka yi mini gafara, da ya je yawon duniya sata ya koyo, har Sarkin Ɓarayi ya ci don shahara.

Waziri ya ce, ''Ba ka ji ba, yanzu, Allah ya ba ka nasara, ai ka ga sai a yanka wa kowa sadakin da zai biya ta hanyar gwanintarsa.

Sarki ya ce, ''Wannan batu farilla, Waziri.'' Ya dubi Sarkin Noma yana ɗan murmushi, ya ce, ''Je ka, gaya wa babban ɗan nan naka sadakin 'yata jaka goma ne, ya kawo maza a yi shirin aure.'' Sarkin Noma ya ruga ya gaya wa Jimrau. Ba a tashi daga fadanci ba sai ga su ya aiko Sarkin Noma ya kawo ya ba Waziri, Waziri ya ba Sarki.

Sarki ya dubi Waziri, ya ce, "A'a! Waziri, ga shi sun kawo, yaya ke nan?"

Waziri ya ce, "Allah ya ba ka nasara, talakan da ya ba da sadakin jaka goma ai ba a kiransa talaka. Wannan fa ai a yi da shi. Da ma ba a ce 'ya'yan Sarki ba su auren tajirai ba. Saura abin da za a yi sai a sa wa sauran abin da ba shi yiwuwa, don hankalimmu ya koma ga wannan shi kaɗai. Da mun sani ma, da jaka ashirin muka sa sadakin 'yarka."

Sarki ya ce, " Kai dai kuma yi shiru." Ya dubi Sarkin Noma, ya ce, "Ka je ka gaya wa ma bi wa wannan, wanda ya ce kome aka sa shi ya yi, kafin gobe war haka ya gina mini gida mai tsawo taki metan, faɗi taki ɗari, tsawon katangar ya zama ta wuce hangen ko wane mai ingarma. Ya gama zauruka goma sha biyu waɗanda za a wuce kafin a kai cikin gidan. A ciki kuma ya gina ɗakuna huɗu, turakata guda, duk kuwa ɗakuna da zaurukan nan a yi musu ɗaurin guga. A cika su kuma da katifu, da kilisai, da dangogin kayan ƙawa iri iri."

Sarkin Noma ya yi kasaƙe, don ya ji abin kamar ba shi yiwuwa. Ya sallami Sarki dai, ya tashi ya tafi ya tarad da Kosau, ya gaya masa abin nan da ya faru duka. Kosau ya ce, "Ba kome, Allah ya gyara." Ya murza zobensa, nan da nan aljani ya fito, ya nuna masa inda Sarki ya ce a gina gida kafin safe, da irin fasalin da ya ce yana so duka. Ya tambayi aljanin in ya iya taimakonsa, don Sarki ya yi alkawari wannan shi ne zai zama sadakin 'yarsa da ya ke so.

Aljani ya ce, "Wannan har wani aiki ne? Tun da ka mulki zoben nan, ka tabbata rai kaɗai ne ba ka da ikon sa ni in hura." Sai ya ɓace.

Sarki kuwa na can da Wazirinsa, suna dariya suna cewa, "Ka ga wannan shi mun rabu da shi!" Da lokacin tashi fadanci ya yi, suka watse.

Ko da gari ya waye Sarki ya farka ya leƙa ta taga, sai ga gidan gingirin kamar daga sama. Bai ko tsaya wanke ido ba, sai ya tashi ya nufi can, ya shiga ya yi ta yawo ciki yana ta kakabi. Gidan dai ga shi na ƙasa ne, amma sai ka ce na suminti ne. Zaurukan nan ko wanne ya shiga sai ya tarad da karaga da shimfiɗu da kayan ƙawa iri iri, in ya wuce su sai ya isa barga ya tarad da dawaki 'yan Azbin firɗa-firɗa suna harbin iska. Da ya shiga tsakar gidan, kallo ya yi kai. Ga barori da kuyangi sai kai da kawowa su ke ciki. Ko wane ɗakin kwana ya shiga in ya ga gadaje da kilisai da katifu da shinfiɗu iri iri sai ya yi tsammani ya fi na baya da ya fito kyau. Kayan da ya gani a wannan ɗaki kuwa, in ya shiga mai bi masa ba su zai tarar ba. Kai, wani al'amarin ya fi gaban a bayyana. Da ya

ga haka, ya aika Waziri ya zo ya taya shi kakabi.

Suna nan sun kasa fitowa don sha'awa, sai ga Sarkin Noma ya shiga. Ya durƙusa ya gai da Sarki, ya ce, "Ga gidan nan ya ce a gaya maka an gama. Ya yi yadda ka ke so?"

Sarki sai tafa hannu kawai, Waziri ya ce wa Sarkin Noma, "Je ka, ka ce masa ya ƙayatad da mu ainun." Sarkin Noma ya fita.

Sarki ya ce wa Waziri, "To, ƙaƙa tsara ƙaƙa, yanzu kuma me za mu yi? Wannan dai lalle yana sha'ani da rauhanai ne."

Waziri ya ce, "Ai ba sai an faɗi ba. Abin da ya fi yanzu sai mu ba autansu nasa abin da zai yi na wajen sana'arsa ta sata, don ya kasa, mu ɗebe shi mu san da waɗannan mu ke yi. Don fa ko kura ta tsufa ai ka san ta fi gaban kare ya zungure ta. Haka kuma ko 'yarmu ta lalace ta fi gaban a aura wa Sarkin Ɓarayi."

Sarki ya ce, "Haba, a ma fara? Allah ya sawwaƙa. In Allah ya kai mu gobe muna rayayyu, sai in aika Sarkin Noma ya zo tare da autan nan nasa Sarkin Ɓarayi, mu ga abin da ya ke ƙobobo da shi."

Waziri ya ce, "Allah ya ɗaukaka ka, hakanan ne. Yau cikin dare sai mu tuna abubuwa masu wuya waɗanda za mu ba shi ya sata." Ya durƙusa, ya ce wa Sarki, "Na bar ka lafiya." Ya nufi gidansa.



Da Waziri aku ya ji Hazik ya tsaya sai ya ce, "Don Allah wuce ka ƙare labarin mu ji, labari guda ɗaya ne ka ke ta yaƙwanƙwana shi haka kwana da kwanaki. Shi ko ba wani mai daɗi ba balle mu ce, ba ko amfani gare shi ba, sai koya mugun aiki."

Haziƙ ya ce, "Ai da ma ko ba ka yi magana ba yau zan ci gaba ne."

# Jarrabawar Da Aka Yi Wa Sarkin Ɓarayi Nomau

Da gari ya waye Sarki ya aika Sarkin Noma ya zo da shi da Nomau, ya ce masa, "Tun da ka ce sata ce ka ke taƙama da ita, in za ka shiga cikin maneman 'yata, zan jarraba ka da abu huɗu. In ka kasa ko ɗaya na kashe ka, don fa ka zo yi mini sata ne. Ka yarda?"

Sarki ya ce, "Gobe ka zo ka sace zobena. Ga shi nan zan ajiye shi bisa tebur da rana ana fadanci. Ba na ko yarda da a yi layar zana."

Nomau ya ce, "To, Allah ya kai mu." Ya yi ban kwana ya tafi.

Mutane suka ce, "Ai ko gobe muna shirin ganin bidiri yadda za a saci zobe da rana kata gabammu muna ji muna gani, ba da ko an yi laya ba."

Kashegari Sarki ya fid da zobe ya ajiye a tebur, mutane suka kewaye ana ta fadanci. Sun tabbata zoben ba ya satuwa. Suna nan zaune sai ga wani tsoho da sanho a riƙe, ya leƙo Majalisan nan, yana bara yana cewa, "Allah ya ba ku na Allah, Allah ya sa mu cikin cetattu."

Da wani bafade ya gan shi sai ya buga masa tsawa ya ce "Kai, tafi daga nan, ba ka san nan fada ba ce? Tsufa hauka ne?"

Sarki ya ce, "Kyale shi ya yi ta yi, ai yanzu shi daidai ya ke da yaro." Sai tsohon nan ya kaikaici idonsu ya saki zomo a zauren.

Da ganinsa sai fadawa suka ce, "Ihu, ga zomo! Ihu, ga zomo!"

Sarki ya ce, "Kai, ku ƙyale shi, ku lura da abin da ku ke yi." Sai tsohon nan kuma ya sake sakin gudan. Fadawa suka ce, "A, ga wani, ga wani! Ashe biyu ne! Ai ko firɗa-firɗa ne. Watakila ko da mace da namiji ne, sa yi raha a gwama su da naman dajin da Sarki ke kiwo."

Sarki ya ce, "Har yau ko ban taɓa kiwonsu ba. Amma dai ku ci gaba da aikinku." Tsohon nan na nan tsaye na ta bara, ya sake sakin guda.

Sarki ya yi wuf ya tashi, ya ce, "Ku tara a kama su, in gama cikin waɗanda na ke kiwo." Mutane suka tashi suna bin zomaye cikin gida su kama, suka bar zobe nan bisa tebur. Da suka kama

zomanyen suka dawo. Ko da Sarki ya zo ya duba tebur, sai ya yi salati, ya ce, "Wa ya ɗauki zoben da ke nan yanzu yanzu?" Ba wanda ya amsa. Duk fadawa suka shiga lalabe-lalabe cikin ƙura ba zobe ba dalilinsa.

Can da azahar sai ga Nomau ya zo da zoben Sarki, ya yi gaisuwa ya ce, "Ga shi, Allah ya ba ka nasara."

Sarki ya karɓi zobe ya duba, ya ga dai nasa ne, ya ce, "Karya dai ka ke yi, layar zana ka yi ka zo ka ɗauka, an ko ce ban da layar zana."

Nomau ya ce, "Ba layar zana na yi ba, Allah ya ba ka nasara. Ni ne na yiwo shiri kamar tsoho, na zo ina bara a wajenku ɗazun da hantsi, na saki zomaye don ku bi. Wannan ai ba wani abu ba ne. Sai ka faɗi na biyu."

Sarki ya ƙuta, ya ce, "To, yau da dare ka zo ka sace gunya ɗin nan nawa Ɗantsito."

Sarkin Ɓarayi Nomau ya yi gaisuwa ya fita ya tafi gida, 'yan'uwansa suka yi ta yi masa dariya.

Tun kafin rana ta faɗi ya je ya sami tulun giya ya sayo ya ajiye. Da dare ya raba, ya yi shiri kamar 'yar tsohuwa, ya ɗauki tulun giya ya nufi gidan Sarki. Kafin ya kai hadarin ruwa ya taso, ruwa ya yi ta dukansa, ya isa gidan Şarki tsamo-tsamo yana makyarkyata. Da isarsa sai ya tarad da Sarki ya sa dogarai takwas na tsare da Ɗantsito, ko wanensu ga baka da kwari rataye. Ya tarad da huɗu daga cikinsu kowa ya kama ƙafar dokin nan guda ya riƙe. Ɗaya ya sa masa ragama ya riƙe, ga wani can kame da wutsiya, wannan kuwa ya kama dokin ya ɗare. Guda kuwa, watau babbansu, shi sai kewayar gida ya ke yi yana gadi. Da ya fito wajen zauren barga yana leƙe, sai ya ga 'yar tsohuwa da kayan tulu duk ta jiƙa, sai makyarkyata ta ke yi, haƙora na kaf kaf kaf, ga ta tsugunne gindin katanga daga waje. Sai ya fito ya daka mata tsawa, "Ke tsohuwa, ina za ki?"

'Yar tsohuwa ta durƙusa jiki na rawa, ta gigice, ta ce wa dogarin nan, "Na fito kasuwa ne, dare ya yi mini, har na sha kashin ruwa, shi ya sa na raɓo in fake. Giya na kawo kasuwa tun daga ƙauye, ga shi na uiwo dare ba ta sami kasuwa ba."

Dogari ya matsa ya ƙwace tulun giya, ya kafa kai ƙwaƙwal ƙwaƙwal, wai ya yi mąganin barci. Bai san giyan nan akwai banju a ciki ba. Tsohuwa ta ce, "Don Allah yi hankali kada ka fasa mini tulu."

Dogari ya harare ta, ya ce, "Tulun banza! Wane tulu ke gare ki?"

Ya sami giya ya ƙyanƙyama ɗayan cikinsa, sa'an nan ya koma gefe guda ya kishingiɗe, wai ya shaƙata sa'an nan ya shiga wajen aikinsa. Can sai kafirar ta fara ɗibarsa yana tangaɗi, kafin a yi



haka banju ya taso ya shiga aikin nasa, sai barci. Tsohuwan nan da ta ga ya yi barci ta tashi sannu kan hankali, ta tuɓe rigar dogarin nan da rawaninsa ta sa, ta ɗauki umararsa ta riƙe, ta nufi inda dogaran nan ke ƙumun Ɗantsito, ta ce musu kamar ita ce dogarin, "Ba ku sani ba fa, fitan nan tawa sai da na gamu da ja'irin, na ɗana kibiya zan ɗirka masa, ya faɗi yana roƙona gafara. Tausayi ya kama ni na ƙyale shi, bayan na sa ya rantse ba ya dawowa. Mai so duk ya yi ta barcinsa, ba kome. Kuma in wani na tsoron wani abu, ko Sarki ya tambaye ku da safe ku ce ni na ce ku yi. In ko kun fi so ku yi ta zama, ku yi ta yi, ni dai don sule ashirin da biyar ba na wahal da kaina, kun ga kwanciyata." Sai ya ɓingire kamar yana barci.

Sauran dogarai sun samu babbansu ya ce ko wani abu ya faru da safe su ce shi ne, to, me ya dame su? Sai suka yi ta gyangyaɗi nan har da minshari. Da Nomau ya ji sun fara jan rago sai ya tashi ya fita waje ya ɗauko kayan da ya ɓoye, ya sa itatuwa huɗu masu gwafa ya gina rami ya kafa su, biyu baya, biyu gaba, ya aza waɗansu itatuwa bisa kamar masaƙa, ya cicciɓi wanda ke bisan dokin nan ya aza bisa itatuwa, ga shi yana gyangyaɗi bai sani ba. Ya ɗauki igiyoyi ya ɗaura wa itatuwan nan. Dogarin da ke riƙe da wutsiya, da mai riƙe da ragama, ya ba su suka riƙe igiyoyin ɗai ɗai, suna barci ba su sani ba. Waɗanda ke rike ƙafafuwan ko wanne ya ba shi icen nan guda ya riƙe. Shi kuwa ya kwance dokin, ya ɗaura masa tsumma a kofato, ya ja ya surare da shi, ya bar dogarawa nan na ta sharɓar gyangyaɗi, Sarkin Dogarai kuwa babbansu na ƙofar gida, giya ta buge shi.

Da gari ya waye Sarki ya buɗe gida ya tarad da yadda Nomau ya yi wa zaɓaɓɓun dogarawansa, abin kuma ya wuce na ban haushi, sai ya bushe da dariya. Ya raɓa ya fita, ya bar su nan kowa na ta sharar barci, waɗansu da ice a hannu, waɗansu da igiyoyi sun riƙe. Ya aika aka ta da Waziri, suka zo suka yi ta dariya. Sa'an nan Sarki ya ɗauki bulala ya yi ta tsala musu, suka farka suna ta zurawa a guje.

Hantsi ya yi sai ga Nomau da Ɗantsito yana janye, ya kawo wa Sarki. Sarki ya fusata, ya ce, "Yau da dare ka shigo turakata ka sace bargon da na ke kwance sama. Zan haɗa bindiga, in ka zo ko in kashe ka. Yau ko na ke so ka zo, ban ce gobe ba ko jibi. Ba na sa kowa gadinka."

Sarkin Ɓarayi Nomau ya ce, "Allah ya kai mu." Ya miƙe tsaye ya ce, "Sai ni daki bari na Sarkin Noma, kushewar baɗi sai baɗi!" Ya sallami Sarki ya tafi.

Magariba na yi ya tafi hurumi, ya duba wani sabon kabari ya tone, ya ɗauko gawar ya kawo gida, ya sami tsani ya gama ya ɓoye. Can da dare ya tashi ya ɗauki gawan nan da tsanin, ya nufi gidan Sarki ya shiga. Ya tasam ma turakarsa ya tarad da taga buɗe, ga fitila na ci kamar rana. Sai ya jingina tsani daidai taga, ya ɗauki gawan nan ya saɓa a kafaɗa ya-kama hawan tsani da ita. Can kan gawa ya kai daidai da taga sai Sarki ya gan shi, ya aune shi da bindiga kwararam, ya sami gawa a ka. Sai Sarkin Ɓarayi ya saki gawan nan ƙasa tim.

Sarki ya ce wa uwargida da ke nan tare da shi, "Haba kin ji na kashe shi, kowa ya huta. Amma fa a ce 'yar cikina ta rasa wanda za ta aura sai ɓarawo, ai kin san da sake! Sai ya tashi ya ɗauki fitilà, ya biyo matakin soro ya gangaro ya gani.

Sa'ad da yana gangarowa sai Sarkin Ɓarayi ya shiga ta taga, ya

ce wa matar Sarki, "Miƙo mini bargon nan da mu ke kwance kai in yafa, wannan luru bai ishe ni ba, ɗari! Haba, abu yau sai ka ce daren nan jaura ke wucewa."

Abu cikin duhu, matar na tsammani Sarki ne, ta ɗauki bargo daga kan gado ta durƙusa ta ba shi, ta ce, "Mun dai huta da wannan ƙanƙama."

Nomau ya ce, "Da ma daga an ƙyale shi, ai rashin jini rashin tsagawa." Yana nan kamar yana gyarawa, da ya ji Sarki na hawowa shi kuma sai ya sake bin ta taga ya fita da bargon.

Da Sarki ya hawo da fitila sai ya ce wa matar, "Na kashe shi, amma na ga kamar ba shi ba ne, don wannan har yana da gemu, shi kuwa saurayi ne, bai isa tsai da gemu ba. Watakila ja'irin ne ya rikiɗe."

Matar ta ce, "Ya aika."

Sarki ya duba bai ga bargo ba, ya ce wa matar. "Ina bargo?"

Matar ta ce, "Wane bargo kuma ban da wanda ka zo ka karɓa yanzu?"

Sarki ya ce, "Yaushe na zo na karɓi bargo?"

Matar ta bayyana masa yadda aka yi. Ko da ya ji haka sai ya yi salati, ya san abin da ya faru. Da gari ya waye ya gaya wa Waziri. Suna nan sai ga Sarkin Ɓarayi ya zo da bargo, ya yi gaisuwa ya miƙa wa Sarki, ya yi sallama ya koma gida ya bar su nan suna kakabi.

Suna nan sai Limamin garin ɗa ladaninsa suka zo gaisuwa. Da suka ji abubuwan da Nomau ya aikata wa Sarki sai haushi ya kama Liman, ya dubi Sarki, ya ce, "Allah ya ba ka nasara, wannan labari ai bai kamata mu bari wadansu su ji ba, kada a yi mana dariyar wauta. Abinku ne ku ke yi kullum ba shawara, sai ka ce wai kome Waziri ya gaya maka ya isa. Mutum guda ya taba shawara shi kaɗai? Da kun sanad da ni wannan abu, habawa! Nomau ɗin banza, ba cikin 'yan shekarun nan muka gama share masa majina ba?" Ya dai sami Sarki nan ya yi ta yi masa ƙanƙanci. Ga shi ya tsufa, saboda haka Sarki ke raga masa, shi ko bai sani raga masa a ke yi ba, yana neman ya wuce gona da iri.

Liman ya fita ya bar Sarki na cizon yatsa, sai ga Sarkin Ɓarayi ya shigo. Sarki ya dube shi a fusace, ya ce masa, "Yau da dare ka sato mini Liman, ka kawo mini shi nan gobe da safe! Aikinka na hudu ke nan."

Sarkin Barayi ya ce, "Don wannan ta kwana gidan sauƙi, ni ban ci sarautar ɓarayi ba sai da na shirya." Ya yi gaisuwa ya fice.

Da isarsa gida 'yan'uwa suka ji abin da ya faru, sai suka ce, "Ku bar shi, ai ba kullum a ke kwana a gado ba. Yau ko shi ne

Gwamnan ƁBarayi, ba Sarkin Ɓarayi ba, ma ga yadda zai yi ya saci mutum."

Sarkin Ɓarayi dai bai ce musu kome ba, sai ya fita bakin rafi da wani sanho, ya yi ta neman ƙaguwa yana kamawa yana zubawa cikin sanho. Da ya cika shi fal da ƙaguwa sai ya ɗauko ya kawo gida ya ɓoye. Ya tafi kasuwa ya sawo kyandir ɗauri ɗauri. Ya kuma sawo ƙatuwar waga ya kawo ya gama ya ajiye. Can da tsakad dare sai ya tashi ya nufi masallaci da kayan nan nasa. To, masallacin kuwa yana kusa da gidan Liman ne. Da shigarsa masallacin sai ya yi ta fid da ƙaguwoyin nan yana liƙa wa ko wannensu kyandir, yana kunna wuta daga bisa kamar fitila, ya bi su duka ya lilliƙa, ya sake su nan cikin masallaci suna yawo. Sa'an nan ya tashi ya kama kiran salla, bayan ya bi jikinsa ya naɗe kaf da wani farin zawwati.

Da Liman ya ji kiran salla sai ya fito yana tsammani ladan ya ruɗe ne. Da shigowarsa masallaci sai ya ga masallacin duk ya haske, ga waɗansu halicce-halicce kamar ɗari sai yawo su ke yi da fitilu suna ci bayansu. Ga wani mutum kuma fari fat yana jan tasbi. Liman ya ja da baya ya buga salati, zai ruga sai Nomau ya ce masa, "Kada ka ji tsoro, wajenka aka aiko ni, an ce ba don kai ba zunubin mutanen garin nan ya isa a kife su. Saboda haka aka ce in zo in tafi da kai, don mutane su ga misali daga gare ka, su ƙara lura da al'amarin addini."

To, Allah ya ba ka nasara, ban taɓa ganin jahilin Liman irin wannan ba. Da ma ba Musulmin asali ba ne, irin mujusan nan ne da suka tsinci Musulunci da rana tsaka. Sai ya yarda da maganar Nomau, ya durƙusa gabansa ya ce, "To."

Sarkin Ɓarayi Nomau ya ɗauko waga, ya ce, "Ga abin da aka umurce ni in ɗauke ka ciki, in tashi da kai zuwa sama. Shiga ciki ka yi ta salati, in ina tashi da kai."

Liman na rawar jiki ya kama waga ya shige ya dunƙule. Sarkin Ɓarayi ya bi bakin waga ya rufe, ya sa igiya ya layyace ram yadda Liman ko ya so fitowa ba ya iya yi. Ya ɗaura wa wage igiya, ya yi ta janta ya nufi gidansa ƙuwuwuwu. Liman tun yana salati har zafi ya sa ya kasa. In sun faɗa dutse Liman ya ji ƙugunsa ya buge sai ya ce, "M."

Sarkin Ɓarayi ko sai ya ce, "Yi shiru! Nan sama ta biyu mu ke, mun wuce sama ta ɗaya tuni."

Da suka faɗa wani kwari, waga ta birkice, bakin Liman ya bugi ƙasa ƙumus, ya ji zafi har ya yi ƙara, "Wayyo!"

Sarkin Ɓarayi ya ce, "Yi shiru! Yi ta salati mana, mun kawo sama ta huɗu."

Kai, ya Allah ka kiyashe mu da aikin jahilci! Can Nomau na ta

tiƙar gudu da shi wai yana tashi, sai suka tarad da wani tabki. Nomau ya ji kwaɗi na ta kuka ƙwa, ƙwa, ƙwa, cikin tabki, sai ya ce, "An kawo sama ta biyar, ka ji ana yi maka maraba. Kai dai yi ta salati."

Liman ya taƙarƙare da salati. Can bayan an jima suka isa gidan su Nomau, ya buɗa ɗakin tattabarunsu ya tura Liman ciki ya rufe. Tattabaru suka yi fafafafafafa. Sarkin Ɓarayi ya ce, "Kwanta kurum ka yi ta salati, har Sarki ya ba da izni in isa da kai. Nan inda ka ke sama ta bakwai ke nan, wannan motsin da ka ke ji Mala'iku ne masu tashi ke maka maraba. Za ka ji suna wani abu ƙu, ƙu, ƙu, ƙu, ƙu, irin harshensu ke nan kamar na tattabaru. Ni zan tafi in nemo iznin isa da kai." Nomau ya tafi ya bar jahili nan yana ta salati, shi kuwa ya je ya yi ta shara barcinsa.

Da gari ya waye ya taho ya buɗe ɗakin tattabaru ya jawo shi, ya ce, "An ce in isa da kai. In ka lura ka ga annuri ya sake, ba kamar na yadda muka baro duniya ba." Ya yi ta jansa har gidan Sarki. Ya yi gaisuwa. Liman na ta alla-alla a buɗe shi ya ga abin da zai gani. Sarkin Ɓarayi ya ce wa Sarki, "Ga wata 'yar gaisuwa irin tamu na kawo maka. Sai ka buɗa da kanka ka gani."

Sarki ya tashi ya buɗa waga, sai ga Liman ciki ido wuri wuri, da tasbaha a hannu yana salati yadda Sarkin Ɓarayi ya ce ya yi. Ko da Sarki ya gan shi haka bai san sa'ad da ya ɓarke da dariya ba. Mutane suka yi kamar za su suƙe don dariya. Sarki ya kama Sarkin Barayi, ya cire hular da ke kansa da rawaninsa ya naɗa masa, ya ce, "Na tabbatad da sarautarka ta ɓarayi. Batun aure kuma sai mun yi shawara tsakaninka da 'ya'yayenka." Don kunya Limamin nan ya kasa fitowa sai da aka kama shi aka kai shi gidansa.

Da aka watse Sarki ya dubi Waziri, ya ce, "To, Waziri, baki fa shi kan yanka wuya. Yaya ke nan?"

Waziri ya ce, "Ba yadda za a yi sai mu san yadda za mu yi mu rarrashi sauran su dangana, mu kuwa mu ba Ƙosau. Don wanda ya gina wannan gida cikin dare guda, ba mai jayayya da shi."

Sarki ya ce, "Gaskiyarka, sai mu aika Sarkin Noma ya zo da su, su duka." Da aka zo da su Sarki ya shiga rarrashin Jimrau da Nomau su yarda Ƙosau ya auri 'ya tasa. Jimrau ya ce ya yarda. Nomau ya ce shi faufau ba ya yardam masa, sai dai in za a hana shi da ƙarfi a hana shi, ya san Sarki ya bar batun adalci.

Da Sarki ya ji haka sai ya dubi Waziri. Waziri ya fusata da maganan nan ta Nomau, ya dube shi, ya ce, "Mece ce sana'arka?"

Ya ce, "Sata."

Waziri ya ce, "To, kai ko a ranka ka ga ya yiwu a ce 'yar Sarki

ta rasa wanda za ta aura sai Ɓarawo? In dai mu muka haifi 'yarmu, to, mun ba Ƙosau." Duk fada ta watse. Daga nan aka tafi aka yi ta shagalin biki.

Da gari ya waye Sarakuna suka taru za a ɗaura aure, sai Sarki ya ce wa Sarkin Gida ya je taska ya ɗauko masa kayansa na ado, da lambobinsa na girma. Sarkin Gida ya ruga. Jim ya dawo a guje, duk ya ruɗe, jiki na rawa, ya faɗi gaban Sarki, ya ce,



"Allah ya ba ka nasara, ai duk taskokin nan na tutafi ba sauran ko ƙyalle yau, sai wannan tsohon bargo da a ke ɗaure alkyabbu."

Mutane duk suka yi zugudun suna jin abin mamaki, Sarki zai buɗe baki ya yi magana sai ga ma'aji kuma a guje rawani a hannu ya zube gaban Sarki, ya ce, "Allah ya ba ka nasara, ka ji ƙaina, na tuba, na bi ka!"

Mutane suka ce, "Me ya faru haka?"

Ma'aji ya ce, "Ai yau baitulmali ɓara yi sun yi masa ƙat, ban da ahu da na tarar bakin ƙofa ba abin da aka bari!"

Yana cikin ba da labari kuma sai ga Sarkin Zagi ya zubo a guje ya nufo fada, ba ko wando. Shantali zai yi masa magana sai ya ga ya durƙusa gaban Sarki, ya ce, "Allah ya ba ka nasara, ai barga yau ba sauran doki, duk an sace!"

Sarki ya miƙe tsaye, sai kuma ga Jakadiya ta fito daga cikin gida, ta durƙusa, ta ce wa Sarki, "Mun taru za a yi wa amarya ƙunshi, mun duba, ƙasa da bisa cikin gidan nan duk ba mu gan ta ba."

Sai aka ga Sarki ya yi shiru. Can ya dubi dogarawa baki na rawa, ya ce, "Ku yi maza ku zo mini da Nomau!" Dogarawa suka



zuba a guje suka nufi gidan Sarkin Noma. Jim kaɗan suka dawo, suka ce, "Ai an ce rabonsa da gida tun jiya da dare." Sarki ya baza mutane cikin ƙasa aka yi ta nema, amma ko ɗuriyarsa ba a ji ba.

Waziri aku ya dubi Haziƙ ya ce, "Shi ke nan? Da ma irin abin da ba mu so ke nan cikin labarun ɓarayi a ce sun sami sa'a bisa ga mutanen kirki."

Haziƙ ya ce, "Su wane ne mutanen kirkin nan ciki? Ai ka ce su duka ukuɓarayi ne."

Waziri aku ya ce, "To, ko ba kome dai wannan labari naka ya gundurad da mutane. Kwana uku ana abu ɗaya? Bari in ba ku wani ɗan gajere, a tashi a yi salla.

# Labarin Waɗansu Maɗinka Guda Uku

A Wata ƙasa an yi waɗansu maɗinka guda uku, ba a taɓa ganin inda suka sayi zawwatin da su ke ɗinkawa ba, har mutane suna zaton sautu su ke yi a wata ƙasa ana kawo masu. Waɗansu suka ce watakila aljannu ke gare su masu ba su zawwati. Ashe duk ba haka ba ne. Su yadda su ke yi, kullum da tsakad dare sai su gamu, su ɗauki hanyoyi su nufi hurumin garin, watau inda a ke rufe mutane, su yi ta haƙe sababbin kaburbura suna zare likkafanin daga jikin matattu, sai su zo gida su riƙa ɗinka 'yan taguwoyi da wanduna suna sayarwa.

Al'adar ƙasan nan kuwa, idan mai zarafi ya mutu sai su sa masa kayansa duk, su haƙa babban rami su sa shi a ciki, su ɗauko dutse mai girma su rufe bakin. Ana nan sai Wazirin garin ya mutu, aka tafi kurmi aka haƙa masa ƙaton kabari, aka shimfiɗe wurin da kilisai da barguna da katifai. Da aka gama aka ɗauko Waziri, aka sa masa kufta da jabba da wando mai zina, aka yafa masa alkyabba. Da ka gan shi sai ka yi zaton in an ce masa, "Ranka ya daɗe" zai ce "Mhm." Aka kawo wani zobe na zinariya aka sa masa hannu aka kai shi kabarin nan aka ajiye, aka nemo wani jibgegen dutse aka rufe bakin.

Kafa na ɗaukewa sai maɗinkan nan su uku suka taho wurin kabarin, don su sace abin da ke ciki. Amma su duk abin da suka fi bukata cikin kayan nan shi ne zoben nan na zinariya, don ko shi kaɗai ma ya iya sayen duk abin da ke cikin kabarin. Da zuwansu suka yi dako-dako a bakin ramin, suna shawarar wanda zai shiga ya miƙo kayan. Kowa aka lalabo sai ya ƙi, ya ce ɗan'uwan ya shiga. Babbansu ya ce ƙaramin ya kamata ya shiga. Karamin ya ce, "A'a, ai wannan irin wuri sai ku manya." Suka yi ta jayayya haka, har dai ƙaramin ya yi ta maza ya ce ya shiga, a buɗe, ai mai rabon ganin baɗi sai ya gani.

Da suka buɗe zai shiga sai mabi masa ya ce, "In ka ɗauko zoben nan fa ka lura kada ya sumbule maka."

Ya juyo, ya ce, "Ina ruwanka, ko ya sumbule mini, ko kada ya sumbule mini, kai dai ba tsoro ya hana ka shiga ba?"

Ya shiga, ya yi ta miƙo musu kaya, suna karɓa, suna ajiyewa. Ya zare zoben ya ɓoye a kubakar wandonsa, ya ci gaba da miƙo musu kaya. Can ya fara miƙo shimfiɗu sai babban ya ce, "Na ce ko dai ka ɗauki zoben nan? Kada ka manta da shi."

Ya ce, "Ku karɓi waɗannan dai, ina zuwa." Da ya ƙare miƙo musu dukan sauran kayayyakin, sai ya ce wai ya duba ko ina jikin Waziri bai ga zoben nan ba, ko ƙasa ko sama bai gan shi ba.

Ma bi wa babban ya ce, "Kai dai duba yatsansa na hagun, yana nan, in dai ba makirci ka tasam ma yi ba." Ya ce allambaran, ya duba ko ina bai gan shi ba. Suka yi juyin duniyan nan da shi, ya ce bai ga zobe ba. Alhali kuwa ga shi a maƙale a wandonsa.

Da babban ya ji haka sai ya ce, "Ashe haka za ka yi mana? To, je ka da shi, in zobe na yi maka wani amfani lahira. Da kai da sake shaƙar iskar duniya har abada." Da faɗin haka sai suka mai da dutsen nan, suka toshe bakin ramin, suka yi tafiyarsu.

Ɓarawon nan ya tashi ya yi gabas, ya yi yamma, ya yi kudu, ya yi arewa, ya rasa inda zai sa kansa. Ya je ya kwanta kusa da Waziri, ya yi ta kuka. Da ya ga dai kuka ba shi da wani amfani a irin wannan wuri, sai ya tashi ya nufi bakin ramin nan ya yi yunƙuri; ya iza, ya iza, ya ji dutsen nan ko motsawa bai yi ba. Sai ya ce, "Ai ƙaddara dai in ta zo ba ta da makawa! Ko da na shigo nan, ko ban shigo ba dai, mutuwa zan yi, domin da ma duniya ba gidan tabbata ba ce ai da mun tarad da kakannimmu a ciki. Kai na ma dai huta da azabar duniya da masifarta."

Sai ya haye gadon waziri, suka kwanta, yana jira bayan ko kwana uku yunwa ta kashe shi, ya mutu ya huta. Can dare ya raba sai ya ji maganar mutane sun yiwo wa kabarin nan tsinke. Ya yi kamar ya yi magana su buɗe, ya ga dai ko ya yi ma, tsoro ba zai bari su tsaya ba, balle ma su ji ko shi wane ne, su buɗe. Ya tuna ma dai ko sun buɗe shi lalle ba su barinsa kawai, ga Sarki za su kai shi. Ba shakka kuwa in Sarki ya ji abin da ya ke ciki, kashe shi zai sa a yi ba rai ba girma, ya bar wa jikokinsa abin faɗi har iyakar ransu.

Da ya tuna da haka sai ya dangana, ya ƙyale. Jim kaɗan sai ya ji mutanen nan sun zo bakin kabarin sun tsaya. Ya saurara ya ji ko abokansa ne suka ji tausayi, suka zo su fid da shi, ya ji ba muryarsu ba ce. Ashe waɗansu ɓarayi ne kuma su uku suka yi wa wannan kabarin tsinke, don su buɗe su sace kayan da ke ciki, su ɗauke zoben nan da suka ji ana labarinsa da rana. Ba su san har an riga su ba. Suka tsaya cirko-cirko bakin ramin, suna shawarar wanda zai shiga ya miƙo kayan. Ko wanne aka ce ya shiga sai ya ƙi. Wani ya ce kansa ke ciwo, shi ya hana shi ya shiga, guda kuma ya ce shi dundumi ya ke yi. Suka yi ta bayayya dai yadda

waɗancan na farko suka yi. Daga can sai ya ji wani mai karambani kamarsa ya ce shi zai faɗa. Wai mamaci na kama mutane ne, har da za su riƙa raki haka?

Ko da wannan mutumin ya ji haka sai murna ta kashe shi. Ya tashi, ya zo bakin ramin ya laɓe. Suka buɗa ramin. Wancan zai shigo ke nan, har ya janye wando ya miƙo ƙafa, zai sulalo ciki. Ko da na laɓen nan na ciki ya ga ƙafarsa, sai ya kama ya riƙe. Ya ja, ya ja, ya ji an riƙe kam. Sai ya yi Salati, ya ce, "Wayyo Allah, ya riƙe mini ƙafa! Ku taimake ni, zai janye ni!"

Ko da sauran suka ji haka sai ko wanne ya ce in ba ka yi ba ni wuri. Suka yi ta gudu, kowa na ta kansa. Da wancan na cikin



ramin nan ya ji sun watse, sai ya saki ƙafar wannan. Ko da ya ji dai an saki ƙafarsa, sai ya yunƙura ya yi waje. Ya yi ta gudu yana waiwaye kada a kama shi ɗaga baya. Da wancan na cikin ramin ya ji ba kowa, sun bar ƙofar a buɗe, sai ya fito da zobensa a kubakar wando, ya yi tafiyarsa. Daga wannan fitar kutsu da ya yi sai ya tuba, bai sake yin sata ba.

Alƙalai suka ɗauka gaba ɗaya, "Duk labaran da aka bayar nan baya na game da ɓarayi, wannan duk ya fi su daɗi." Mutane kowa ya tashi ya nufi gida ana dariyar ɓarayin nan.

Kashegari yau da aka zo kuma Haziƙ ya shiga aiki:

# Kuda Wajen Kwaɗayi A Kan Mutu

Akwai wani matsiyaci wai shi Alti yana zaune a wani gari. Abin da aka sani ga ɗam Musulmi, ko wace masiba ta dame shi ya rika dangana yana tuna Allah, amma shi halinsa ta wajen rashin dangana sai a yi kurum. Shi kullum ba shi da wata magana sai, "Yau dai ina tafiyan nan in tarad da akwati cike da sulalla, haba!"

Ana nan wata rana yana yawo cikin daji zuwa rana faɗuwa yana saran itacen wuta, sai ya ci karo da wani ɗan tsoho tukuf. Da ɗan tsohon nan ya ga Alti sai ya yi ajiyar zuciya ya ce, "Bawan Allah, ka ji ƙaina ka taimake ni, na yi makuwa ne, tun safe na ke cikin dajin nan ban san gabas ba, ga shi rana ta kusa faɗuwa, ko ƙwayar hatsi ba ta ga bakina ba."

Alti ya ji tausayinsa, ya kama hannunsa ya kai shi gida, ya kawo abinci ya ba shi ya ci. Da hankalinsa ya komo ya ce zai lallaɓa kafin rana ta faɗi ko ya ƙara gaba.

Alti ya ce, "A'a, sai ka kwana nan har gobe hankalinka ya komo, kada ka fita ka sake ruɗewa, watakila makuwar ba ta sake ka ba sosai har yanzu."

Tsoho ya ce kansa ya waye, zai ci gaba. Alti ya ƙi, ya ce, "Ga shi rana ta kusa faɗuwa, ka ce za ka faɗa dajin nan kai kaɗai? Sai dai ka kwana sai gobe."

Da tsoho ya ga ya yi, ya yi Alti ya bar shi ya wuce ya ƙi, sai ya yarda da ya kwana. Alti ya kai masa tabarma bisa wani gado a ɗakin da ya yi da ma domin baƙi, ya hura masa wuta. Tsoho ya shiga ya yi ta ƙahon dandi yana 'yan soshe-soshensa, Alti kuwa ya koma ɗakinsa ya ba shi wuri ya sake.

Da gari ya waye tsoho ya ce zai yi harama. Alti ya ce, "To, mu je in ɗan taka maka mana."

Da suka ɓace wa mutane sai ya ga tsohon nan ya yi girgiza. Nan da nan sai ya koma ga siffar aljannu. Alti ya ja da baya kamar zai ruga, aljani ya ce, "Tsaya!" Ya tsaya. Ya faɗi gabansa ya gaishe shi da ladabi.

Aljani ya ce, "Ni ba mutum ba ne, aljani ne. Da ma ban yi wata

makuwa ba. Can da ka ke saran ice jiya ka sari wani reshe ya faɗa wa ɗana da ke gindin icen yana wasa, har ya karya masa hannu. Saboda haka na komo kamar tsoho na tafi wajenka, domin in gwada ka in gani in kai na kirki ne rashin sani ya sa ka yi wannan aiki in gafarta maka. Don an ce rashin sani ya fi dare duhu. Idan kuwa na ga kai shaƙiyyi ne maras tausayi in kashe ka, ko da ya ke na san ba ganin ɗan nawa ka yi ba, sa'ad da ka karyi icen ya faɗa masa. Na jarrabi alherinka da tausayinka, na ga sun wuce na mutanen zamani. Saboda naka zan yi maka alheri guda. Gaya mini abu biyu da ka ke so, ko mene ne in ba ka su, maimakon alherin da ka yi mini."

Alti kuwa da ma na gaya muku ba abin da ke ransa illa ya sami kuɗi, in ya san za ka ba shi kwabo, kome cin mutuncin da za ka yi masa ya bi ka. Har mutanen ƙauyensu su kan riƙa yi masa ba'a da haka, suna cewa, "Alti sai da irli domin wuri." Wannan ma alherin da ka ga ya yi don yana son a yi masa addu'ar samu ne. Saboda haka ko ban furta ba ka san abin da ke ransa. Da jin wannan jawabi na aljani sai ya durƙusa, ya ce, "Ni ba abin da na ke so sai kuɗi, in mutum ya same su duk bukatar duniya ta ƙare."

Aljani ya ce, "To, yaya ka ke son in ba ka su? Kana son in nuna maka taskar Aljannu ne ka yi ta kwasa? Ko, kuwa kana son in sa a kai maka gida?"

Alti ya ce, "Ni dai in ya yiwu in samu ikon kome da na taɓa ya zama sule."

Aljani ya ce, "Shi kaɗai ka ke so?"

Alti ya ce, "I, in na samu wannan iko in ya so kome ya yi kyau, in taka kowa yadda na ke so."

Aljani ya ce, "To, na ji ɗaya. Faɗi kuma abin da ka ke so ban da wannan."

Alti ya ce, "Ni in na sami wannan ya ishe ni."

Aljani ya ce, "Ai abu biyu na yi alkawari zan ba ka, faɗi gudan kuma."

Alti ya ce, "Wallahi ni wannan kaɗai ya ishe ni, daga kuɗi ai burin duniya ya ƙare."

Aljani ya ce, "Tun da na yi alkawarin zan ba ka abu biyu ba na saɓawa. Duk sa'ad da ka yi bukatar wani abu, ga garin maganin nan ka turata da tsakad dare, ka yi kirana sau uku, 'Samsam, Samsam, Samsam!' ka ga na tsago ƙasa na fito."

Alti ya ce, "To, amma ni ba sauran wani abin da zan yi bukata gare ka in dai na sami wannan."

Aljani ya ce, "In dai don wannan ne, je ka an ba ka. Amma kome ya same ka fa kada ka zarge ni ka ce na rama alheri da mugunta."

Alti ya ce, "Ina da ikon kome na taɓa ya zama sule, sa'an nan wane abu zai same ni? Haba, ai kuɗi su ne maganin takaici."

Aljani ya ce, "To, shi ke nan." Ya ɓace. Alti kuma ya nufi gida yana murna, yana kirfa abubuwan da zai yi in ya sami kuɗin nan. Yana cikin tafiya sai wani ɗan ƙwaro ya cije shi a kai. Ya sa hannu ya buge shi, sai ya ga sule ya faɗo ƙasa kyangaran. Sai ya duƙa ya ɗauka yana murna, yana cewa, "Af, abin ba wuya, da farawa da iyawa?" Sai ya tasam ma waɗansu taron ciyawa ya taɓa, sai duk suka zama sulalla. Ya cire mayafinsa yana ɗokin zai kwasa, sai mayafin shi kuma ya zama sule, ya faɗi cikin na ƙasa cas. Sai Alti ya ɓata fuska, ya ce, "Kai ba kome, don mayafi abin sule da sisi na sayi wani."

Alti ya ga ba abin da zai zuba su ciki, sai ya bar su ya tafi gida, ya ce, "Wannan ma ba su da haske, me zan yi da su?" Ya tara mutane ya gaya musu ya ce shi yana da ikon kome ya taɓa ya zama sule. Za su yi masa gardama sai ya taɓa waɗansu duwatsu nan gabansu sai suka zama sulalla, ya kwashe ya ba mutane. Ya ɗebi waɗansu, ya ce a sawo masa tufafin sawa sababbi. Ko da ya taɓa tsofaffin zai cire sai suka zama sulalla, suka bar shi tsirara. Ya riɗi sababbin ya yi sutura, su kuma suka zama sulalla. Daga nan abin duniya ya dame shi, ga shi tsirara cikin mutane suna yi masa dariya. Ya iza ƙeyar ɗansa, ya ce, "Je ka gida a ba ka abin sutura ka kawo mini." Da taɓa ƙeyar yaron sai yaro ya faɗi ya zama sule.

Ko da mutane suka ga haka duk sai suka watse suka gudu, suna cewa, "Aljannu suka zauta shi. Wa zai tsaya shu'umi ya taɓa shi ya zama sule a banza?"

Da matansa da 'ya'yansa duk sai kowa ya kama gabansa, aka bar Alti shi kaɗai cikin gida. Da ya ji yunwa sai ya fito, duk inda ya tasam ma sai mutane kowa ya yi ta kansa ba mai bari ya taɓa shi.

Da ya ga haka sai ya ce, "Bari in je yara, ai ko mutane sun watse na sami abin da zan ci." Da hango shi sai mutanen yara suka watse, suka bar kayan da su ke sayarwa nan kome bargaja. Da ya isa sai ya tasam ma tukubar tsire, ya tsuguna ya ɗauki tsinke guda zai ci, sai tsiren ya zama sule. Ya riɗi wani da sauri, kafin ya kai ko baka ya zama sule. Ya yi ta neman abinci, da ya samu in ya taɓa sai ya zama sule.

Ya sake wata dabara wai ya riƙa dungura baƙi yana ci kamar dabbobi, amma duk banza. Kome bakinsa ya taɓa sai ya zama sule. Ya rasa abin da ke masa daɗi a duniya, ya yi da na sani, ya gwammace kiɗi da karatu, ya yi ta yawo hakanan tsirara.

Da gari ya waye duk hankalinsa ya fara fita daga gare shi, ya

wuni ran nan a lalace, har dare. Yana kai da kawowa cikin gari yana ce, "Allah wadai, ashe dai kuɗi ba wani alfanu gare su ba. Allah ya tsine sule!" Yana nan haka sai ya tuna da aljanin nan ya ce masa yana da saura abu guda da zai tambaya ya ba shi. Nan da nan sai ya yi al'adar da ya gaya masa, ya kira sunansa "Samsam! Samsam! Samsam!" Sai ya ga ya tsago ƙasa ya fito, ya ce "Mene ne ka dame ni da kira da tsakad dare haka, ka ko yi alkawari ba za ka sake nemana ba?"

Alti ya ce, "Don Allah ka ji ƙaina, ka mai da ni yadda na ke da!"

Aljani ya ce, "Da ka ce kai in na ba ka kuɗi kome ya yi."

Alti ya ce, "Don Allah dai raba ni da sulallan nan, ni dai wallahi ba na sonsu, na fi so in zauna kamar da, zamana na talauci mai daɗi!"

Aljani ya fashe da dariya, ya ce, "Ka yi arziki da ya ke kana da sauran abu guda da za ka tambaye ni. Je ka, ka koma yadda ka ke." Alti ya yi ta murna, ya koma gida ya sami abinci ya ci. Gari na wayewa ya gaya wa mutane ya warke, aka yi ta kura-kura da shi, sai dai da aka hakikance ya warke sa'an nan aka saki jiki da shi. Mutane suka yi ta yi masa dariya, suna kiransa "Kuda wajen kwaɗayi akan mutu."

Waziri aku ya ce wa Haziƙ, "Tun da ka ke ba da labari yau kaɗai na ji ka bayar da mai ɗan daɗi. Amma fa sauran da ka yi ai ni jinsu na yi kamar tarihi. To, da kyau, tun da ka fara ƙaruwa. Ka yi ƙoƙari ka yi waɗanda suka fi wannan in an jima."

Mutane suka fashe da dariya. Waziri ya yi kamar shi bai ga abin dariya ba cikin abin da ya faɗi, sai ya ci gaba da ba da nasa labarin.

# Yaro Ɓari Murna Karenka Ya Kama Zaki

A Tunga akwai wani ladani baduniyi, ga shi ya kai muddin dattawa, amma ba ya son a ce ya tsufa. Yana da gemu har da saje. Kullum in za shi kasuwa sai ya bi gemun nan da sajen nan ya shafe da shuni. In ya duba madubi ya ga 'yar furfura ta tsiro ya fizge ta, wai shi dai kullum a ce masa yaro. Jumma'a kuwa duk ba ta wuce shi sai ya yi sukola, ya sa zargina, ya bi ƙafafun nan nasa ya ƙunshe da lalle. Ga shi ladani, amma tadarsa sai ka ce ta tsohon Soja. Don licin gemunsa, da alfarmar da ya ke yi da shi, har mutane na ce masa "Ladan mai kyaun gemu."

Ana nan, ran nan wata Lahadi Ladan ya ci ado ya nufi kasuwa, ya cika bakinsa da goro, ga sigari yana tafe yana busawa, sai takawa ɗai ɗai ya ke yi, yana duban kasa. Ya tafi rumfar 'yan janhol ya kame, sai ka ce tasa. Suna nan zaune sai aka ta da maganar fata, 'yan janhol suka ce, "Ai yanzu fata ba ta samuwa. Kowa ya ajiye sai an fara hada hada, don sa'an nan ta fi riba."

Daga nan ko me ya kai sa bakin Ladan, shi ba ɗan janhol ba, ba kowa ba, sai ya ce, "Kai ai ko mutane sun cika sakarci. In dai na san inda zan sami riba ko yaya ta ke, ai kome gare ni na sayar."

Da wani Ɗan Janhol ya ji haka sai ya ce, "Haba malam, ba kome ba dai. Yanzu in ka ji za a sayi gemenka da sajenka ka sayar?" Duk sai aka bushe da dariya.

To, Ladan kuwa Allah ya sa shi wani irin mutum ne, duk abin da ga zai yi ya sami kwabo, kome wulakancinsa, sai ya yi, shi dai idonsa idon kwabo kome ya yi kyau. Saboda haka ya ce, "Sai in sayar mana, in dai an ce ana so, in kuwa a iya biyana ko nawa na ce."

Ɗan Janhol ya ce, "Da za ka yi musu kuɗi na gaskiya, ko ni ma da sai in saya."

Ladan ya ƙyafci wani nan kusa da shi, ya kuma kaɗa wa wani can nesa da shi ido, ya nuna musu Ɗan Janhol da baki, ya ce, "In kai ke so sai in yi maka araha."

Ɗan Janhol ya ce, "Nawa za ka iya bar mini?"

Ladan ya ce, "Na bar maka sule talatin." Ya dubi jama'a da ke nan, ya ƙyafce su da ido, yana zunɗen Ɗan Janhol. Ɗan Janhol ya ce, "I, ai ko sule talatin ba tsada ba ne ga gemu kamar naka. Na ce ko ka sayar mini?"

Ladan ya ce, "I." Ya kaikaici idonsa ya yi masa gwalo.

Ɗan Janhol ya ce, "Da gemun da sajen duk fa."

Ladan ya ce, "I!" Yana murmushi.

Ɗan Janhol ya ce, "Na saya. Yaushe zan yanka?"

Ladan ya ce, "Na sayar maka, duk sa'ad da ka ke so ka zo in ba ka."

Ɗan Janhol ya tashi tsaye, ya dubi mutane ya ce, "Jama'a ku shaida, na saya, ya sayar mini. Ya kuma yarda duk sa'ad da na ga gemma na ciwuwa in zo ya ba ni abina in kai ko Allah ya ba ni sa'a wuri ya ja wuri."

Mutane suka bushe da dariya suka ce, "Mun shaida duniya da lahira." Ɗan Janhol ya kawo kuɗi ya ba Ladan sule talatin cif.

Ladan ya tashi, suka ce, "A'a! Abin ba ko la'ada? Ko ba ka son mu sa albarka ne?" Ya kawo sule ya ba su su rarraba, shi kuwa ya sa kai ya fita da kuɗin. Ya shiga kasuwa yana cewa, "Bari in kashe kuɗin nan dai in ga ƙaryar ja'ircin 'yan Janhol da a ke faɗi."

Sauran mutane suka yi ta yi wa Ɗan Janhol ɗin nan dariya, saboda wannan sakarci da ya yi. Ɗan Janhol ya ce su bar yi masa dariya tukun, sai sun ga ya faɗi bai ci riba ba.

Bayan an yi'yan kwanaki, duk sa'ad da Ladan ya gamu da Ɗan Janhol ɗin nan sai ya bushe da dariya, ya ce masa, "Yaushe za ka karɓi ajiyarka?"

Ɗan Janhol ko ya kan ce masa shi dai ya ajiye, amma ya riƙa shafa musu shuni da mai, don su yi raushi. Ran da ya ke son karɓa ba sai ya tuna masa ba. Ya kan ce yana sane da su, mutum ya manta da dukiyarsa? Kasuwarsu ce ba ta tashi ba tukun. Shi ko wai ba ya son ya karyar da su araha. Sai su yi dariya su tafa, su rabu.

Da Ladan ya ga Ɗan Janhol bai kula da shi ba, sai ya yi tsammani sakarci dai ne, kuɗi suka yi masa yawa, su ke sa shi nishaɗi haka. Saboda haka ya tafi ya yi ta gaya wa abokansa dabara ya yi wa Ɗan Janhol, yana kirari wai shi ko a Birnin Kano ya isa wayayye.

Ran nan ranar Jumma'a Ɗan Janhol ya tafi rumfar wanzamai, sai ya tarad da Ladan can ana yi masa aski, ya ɗauki madubi yana tsefe sajensa da gemunsa, don ya ji daɗin zuwa masallaci. Da ganin Ɗan Janhol sai ya ce, "Hala ka zo karɓar gemunka?"

Ɗan Janhol ya ce, "Ni ba wannan ya kawo ni ba, aski ne na zo. Kai dai yi ta sha'anin gabanka."

Ladan ya yi murmushi, ya ce, "Ni fa kullum shirye na ke, in ka tashi so, ga shi." Ya kama rawaninsa yana naɗawa, yana sauri ya je masallaci.

Ɗan Janhol ya zauna, har an fara shafa masa ruwa a kai, sai ya sake tunani, ya dubi Ladan, ya ce, "Kai, na sake shawara, zauna Sarkin Aska ya ɗebe mini sajena."

Ladan ya ɓata fuska, ya harari Ɗan Janhol, ya ce, "Don Allah ba ka bari sai an taso daga masallaci yau, in ya so in zo a ɗebe maka?"

Ɗan Janhol ya ce, "Na san yau Jumma'a ce, amma ba ka gane ba, in an aske maka sai ka ji daɗin shiga mutane, fuskarka ta komo fes, ta yi ta ƙyalli sai ka ce ta ɗan shekara ashirin? Wane rarrashinka ma na ke yi, ban ga dalilin da zai sa ka je mini da gemun masallaci ba yau. Zauna, a ɗebe mini abina."

Ladan ya harare shi, ya rasa abin da zai ce, sai ya share wuri ya zauna gaban wanzami, yana 'yan ƙunƙuni. Wanzami ya jiƙe fuskar Ladan da ruwa kaf, ya ɗauko aska zai fara, sai Ɗan Janhol ya ce, "Tsaya, tsaya, Sarkin Aska! Ba na ma bukatar gemun yau, ƙyale shi ya tafi abinsa, sai wata rana kuma sa'ad da na tashi so a cire."

Ladan ya yi wuf, ya miƙe da faɗa yana cewa, "Zancen banza ke nan. Yaya za ka sa a jiƙa mini fuska, sa'an nan ka ce ba ka so? Sai ka sa a cire maka abinka yanzu, ni ma in huta."

Ɗan Janhol ya ce, "In maganar tawa ta ɓata maka rai ne, baba, ga ni ƙasa. Tsammani na ke mutum na da iko ya yi abin da ya ga dama da dukiyarsa. Ban san zamanin nan abin ya sake haka ba."



Sai ya tashi, ya bugi rigarsa, ya karkace hularsa ya kai ta wajen goshi, ya sa kai ya fita, ya bar Ladan nan na wanke fuska don jirwayen da Sarkin Aska ya yi masa.

Ran nan Ɗan Janhol na zaune rumfarsu sai ya hangi Ladan cikin kasuwa, duk yara sun biyo shi suna cewa, "Eho, ga wanda tsiya ta sa ya sayad da gemunsa! Eho, yanzu fa ba shi da ikon susar gemun nan, kada Ɗan Janhol ya ga gashi guda ya faɗi, ya kai shi ƙara, a ci mutuncinsa!" Kai, duk gari labarin sai da gemu ya bazu.

Ladan ya rasa inda zai sa kansa ya ji daɗi, ya gwammace ma a



aske ya huta. Ga shi gargasa, sai tsawo su ke yi, ba damar ya yi gyaran fuska, kada Ɗan Janhol ya sami ƙafar kamawa. Ya yi rarrashin duniyan nan Ɗan Janhol ya sa a aske masa abinsa ya huta, ya ce shi bai tashi so ba tukuna.

Ran nan Ɗan Janhol yana zaune da 'yan'uwansa a kasuwa, waɗanda aka yi cinikin gemun gabansu, sai zance ya ta da zance har suka yi maganar gemun da Ɗan Janhol ya saya. Suka ce masa don Allah kada ya ɗebe sai rana wa ta yau, jajibiri, a gani Ladan

ya je Idi hakanan, ko kuwa kwantawa zai yi gida, ya aika wa Liman ba shi da lafiya.

Ɗan Janhol ya ce, "Da ni ba ranar jajibiri zan ɗebe ba, sai safiyar Salla kafin a je Idi, sa'ad da ya yi ado, ya ɗauki dogon sandar nan tasa, za shi gidan Liman su tafi."

Saura suka ce, "Wallahi gaskiyarka, wannan shi ne lokacin da ya kamata."

Ran safiyar Salla Ɗan Janhol ya aiki wani saurayi, ya ce ya je ya kira Ladan, amma kada ya yi masa sallama, ya tsaya ƙofar gidan dai, sai ya ga ya fito da shirin zuwa Idi tukuna.

Saurayin ya tafi ƙofar zaure, ya laɓe. Can da hantsin fari sai ya ga Ladan ya fito da takalma da sanda, za shi Idi, ya ci ado car, ya kawo ɗan kura ya bulbula. Saurayin ya gaya masa ana nemansa. Sai ya ga duk ransa ya ɓaci don ya san abin da aka ƙulla. To, ba yadda zai yi, sai saurayi ya shiga gaba Ladan na biye, har rumfar 'yan Janhol. Da isarsu ya ga rumfar nan ta cika makil da yara, da 'yam mata, da sauran mutanen can da suka shaida Ladan ya sayar wa Ɗan Janhol da gemunsa da sajensa sule talatin. Da ganinsu sai gaban Ladan ya faɗi, ya gama girar ƙasa da ta sama ya murtuke, sai ƙuta ya ke yi kamar wanda aka mara wajen faɗa bai sami ramawa ba har aka raba. Bai ko yi musu sallama ba, ya sa kai a rumfar ya tsaya ƙerere gaban Ɗan Janhol, ya ce, "Ga ni, na ji an ce kana nemana." Duk mutane suka ɗauka "Ha!"

Ɗan Janhol ya ce, "Ba don faɗa muka kira ka ba, zo zauna."

Ladan ya zauna, ya jingina da bango, ya ce, "Yi abin da ka ke so, in tafi. Yanzu Liman na can na jirana, an kusa fita Idi."

Ɗan Janhol ya ce, "I, lalle gaskiyarka, ga shi kuwa ku ne manya a wurin." Ya juya ya ce, "Ina Sarkin Aska? Cire mini gemuna da sajena." Duk mutane suka ɓarke da dariya.

Sarkin Aska ya shafa ruwa a fuskar Ladan, ya fid da aska ya fara askewa. Ya aske rabi, sai Ladan ya ɗokanta, don ya san Liman na can yana jiransa, ya ce "Don Allah yi maza ka ƙare in tafi, ujila na ke yi."

Daga nan sai Ɗan Janhol ya ce wa Sarkin Aska, "Af, to, da ya ke sauri ya ke yi, bari hakanan. Wata rana ka ƙarasa cire mini. Bai kamata ba mu tsai da shi haka, mu hana shi zuwa masallaci. Ni ban ɗokanta ba da a cire mini yanzu." Da mutane suka dube shi da saje rabi askakke, suka ce me za su yi kuwa ba dariya ba.

Ladan ya ɗauki madubi ya dubi fuskarsa, sai ya yi kamar ya zub da hawaye don haushi. Ya dami Ɗan Janhol ya sa a cire duka.

Ɗan Janhol ya ce, "Mun yi alkawari na iya ɗaukar abina sa'ad da na ke bukata, ba mu yi da kai za ka tilasta mini in cire ba, ko

ba na so. To, yau rabi na ke bukata, na ko samu, saura kuma sai na yi bukata."

Da Ladan ya ga dai ba ya da niyyar sawa a ɗebe, sai ya ce wa mutanen da ke nan su roƙam masa Ɗan Janhol ya sayar masa da sauran. Suka lalaɓi Ɗan Janhol da batun sayarwa, ya ce kada mutane su wahal da kansu, shi sauran ba na sayarwa ba ne. Ya ajiye abinsa ne, sai bayan kamar wata biyu ko uku ya ɗeɓe.

Ladan fa ya shiga tangwa dai a sayar masa. Ya ce ya ba shi sule goma. Ɗan Janhol dai bai ce kome ba. Ya ce ya ba shi sule ashirin, duk dai aka yi masa damo. Ya sake duban Ɗan Janhol ya ce, "Shin ka bari sule talatin?"

Ɗan Janhol ya ce, "Malam, ka cika mu da yawu a banza. Ni ba zan sayar da gemuna ba don watan gobe, na jibi ma albarka."

Ladan ya ce, "Don Allah in kana sayarwa faɗi yadda za ka bar mini, ribar da za ka samu in ka ajiye sai watan jibi duk na ba ka yanzu."

Ɗan Janhol ya ce, "Mhm. Yanzu na ji ka faɗa hanyar gaskiya da ka fito mini da lalama ta hanyar ciniki. Da ina ce ko kuɗi za ka nuna mini da ka ke saurin ƙari haka. Ni kuwa sa'an nan ko nawa ka saya in ce ba na sayarwa ba ne, ka san kuwa an ce ta gagari Kundila. In za ka ba ni riba mai mai, to, ai sai in sayar maka. Da ma mu ai kome namu na sayarwa ne."

Ladan ya ce, "To, nawa ka ke nufi ka sayar?"

Ɗan Janhol ya ce, "Sule sittin cif. Ka san lalle wuri ya ja wuri."

Ladan ya ce, "Ba siyasa ko ta anini?"

Ɗan Janhol ya ce, "A, ai ba dama. Don ma kana kai ne shi ya sa na bar maka haka."

Ladan yana marairaicewa ya ce, "To, ai sai in biya hakanan. Ya ya na iya da raina? Da ma ai an ce kwaɗayi dai mabuɗin wahala. Mu je gida in ba ka, amma ai ka gama da karɓar kaddara."

Ɗan Janhol ya ce, "Ai tsakanimmu don wannan ba kome, mu tafi har kaddarar ka ba ni."

Ladan ya tashi ya shiga gaba, mutane suka bi shi ɗuu, sai ka ce wanda ya yi sata. Ya je gidansa ya fid da 'yan rigunansa da zannuwan matarsa, aka yi musu kuɗi. Ya kuma shiga, ya kawo sule ashirin da shida da ke gare shi ajiye, wanda ya sayad da wani jaki nasa jiya don ya yi sha'anin Salla, aka gama duk ba su biya ba. Ya kama awakin matarsa guda uku da ragonsa na layya, aka fito da su aka yi musu kuɗi, duk ba su biya ba, sai da ya gama da ba da kayan jikinsa, sa'an nan ya fanshi kansa. Ya dubi Sarkin Aska ya ce, "Don Allah aske mini sauran wannan g-g-g-gemuna, in huta da azaɓa." Suka zauna, aka aske.

An aske ke nan sai ga Liman ya aiko yana jiransa tuni, bai zo ba, lafiya? Ladan ya ce a je a ce cikinsa ke ciwo, sai a nemi wani a je da shi, shi ba ya iya zuwa.

Mutane suka bushe da dariya, suka yi ta kakkawa, suka watse suna yi wa Ladan shege.

Da Ladan ya ga in ya kuskura ya bari aka taso Idi, Sarki da manyan gari suka ji wannan labari, lalle ya kaɗe, sai ya kwashe 'yan sauran kayansa, ya sa matarsa gaba suka bar garin kafin a dawo Idi.

Ka ji aikin kwaɗayi mabuɗin wahala. In da kwaɗayi da wulakanci, in kuwa ka haɗiye shi ba ka ganin zilla.

Mutane suka ɗauka, "Wallahi yau ka yi mana gargaɗi mai amfani."

Waziri ya ce, "Ai ba yau kaɗai ba, kullum ma in kun lura ku ga ko wane labari na bayar haka ya ke."

Sarakuna kowa ya tashi ya nufi gidansa, mutane suka watse.
Haziƙ yau da safe da aka taru sai ya ce, "Jiya na ji kuna sha'awar labarin da Waziri ya bayar ya zama maku gargaɗi. To, idan da ma ku wa'azoji suka tara ku nan, ai na nan gare ni ma sun ishe ku. Ku saurara in fara muku da ɗan gajere."

# Kukan Kurciya Ma Jawabi Ne, Mai Hankali Ke Ganewa

Wata rana wata mace wai ita Juma ta tashi daga garinsu ta tafi Soro, don ta ziyarci iyayenta da ke can. Tana cikin tafiya sai wadansu 'yan garin shaidanu suka tare ta suna yi mata ature suna jifarta wai bakauyiya ce don adonta ya sha bamban da irin nasu. Yara da suka ji ana eho suka yi ta zuwa suka tasam mata, masu jifa na yi, masu mari na yi, suka kifar mata da 'yar tsarabar da ta shiryo ta kawo wa iyayenta.

Juma ta ruga ta nufi gidan Sarki, wai ita ta kai kara. Sai mutane suka ce mata, "Da ma kin dangana, don kin kai su ga Sarki sai ki bata bakinki a banza, in ma kin yi arziki allura ba ta tono garma ba."

Juma ta ce, "To, in kuwa ban kai ga Sarki ba, ku ku biya ni?"

Mutane suka ce mata, "Mene ne na bakar magana? Tafi mana, wane ne bai san wuya ba dakin kura a shiga a fita da gurje-gurje."

Juma ta sa kai za ta wuce, wani tsoho ya ce mata, 'Yata kada ki ki ta mutane, wannan Sarki yana nan dai ne kwakwai ya babu, shi bai kula da azage shi ba, balle ya kula da in an zagi wani ya yi hukunci. Shi dai muddin cika cikinsa, ko marinsa ka yi ba ya ce maka kome. Al'amarin nasa ba mu san kansa ba, in dai hakuri ne haka, wannan ya wuce na Muhammadiya, in ko sakarci ne, sai mu ce Allah ya sawwaka. Yanzu nan garin da rana sai barayi su je su yi maka kwace ana gani kirikiri, in kana da karfi ka sa dantsenka ka tsama, in ko ba ka da karfi sai ka dangana ka ce Allah ya isa."

Da Juma ta ji haka sai ta durkusa ta yi wa tsohon nan godiya, ta ci gaba ta nufi gidan Sarki dai tana kuka. Da zuwa ba ta zame ba sai gaban karagarsa inda a ke fadanci, ta durkusa, ta ce, "Allah ya ba ka nasara, yanzu da zan shigo nan gari yara suka tarye ni suka ba ni kashi, suka yi mini rotse, suka kwashe 'yan kayana, suka gudu. Na yi, na yi in hade bakin cikin nan in kyale su, na kasa kannewa. Saboda haka na zo gare ka yanzu ka taimake ni. Ba so na ke ka tara yaran garin ka yi musu fada ba, ko kuwa ka yi mini wani alheri. Abin da na ke so ka taimake ni da

shi, shi ne yadda zan yi in koyi haƙuri da rashin kula da al'amura, yadda na ji kai ka ke. Ka taimake ni yadda Allah ya taimake ka, don ni ma in riƙa jurewa da tirsasawar da mutane ke yi mini. Domin lalle na gaba ba don ya tsawata aka sa shi ba, domin ya yi haƙuri ne, ya yi zamansa, ya ƙyale mutane su yi zaman kifaye a ruwa, kowa ƙarfinsa ya fisshe shi."

Da Sarki ya ji jawabin matan nan sai ya fahimta, ya yi kamar wanda ya tashi daga barci. Ya fara tara yaran nan tuƙuna, ya hore su bisa ga abin da suka yi wa Juma, ya kawo kuɗi kuma masu yawa ya ba ta sakayyar abin da aka yi mata. Shi kuma tun daga ran nan ya zama wani ƙaƙuza cikin al'amarin mulkinsa, ya zama ba sani ba sabo, kowa ya ɗebo da zafi bakinsa.

Mutane suka ce, "Lalle ko wannan babban jawabi ne, matan nan Juma ta yi. Mai hankali kaɗai ke gane abin da ta yi nufi."

Waziri aku ya ce wa alƙalai, "Wannan labarin ya faye gajarta, bai kamata a ba shi wata daraja ba." Ya shirya zai fara, alƙalan nan suka ce, "Mu ba mu son wa'azi, labarai mu ke so kawai masu ban dariya da ma'ana, a kuma ba da su yadda Bahaushe na asali zai ba da su."

Waziri ya ce, "Ni tun da na fara abin da na ke ƙoƙarin yi kawai ke nan. Bari kuma ku ji wannan da zan bayar."

# Labarin Wani Sarki Da Yaronsa

Da akwai wani Sarki wanda ba shi da wata ta'ada sai ta karanta labarun mata da irin makidarsu. Da dai ya fahimta lalle mata sun kai matuƙa cikin iya makirci, ya ga babu shakka tarkunansu na makirci, kowa suka kafa masa babu ɗaro sai sun kama. Saboda tsoronsu ma bai yarda da ko abinci su riƙa yi masa ba, ya sami wani yaro ya sa shi ya riƙa dafa masa.

Suna nan haka sai ran nan Sarki ya tafi daji farauta. Ya yi yawo har Allah ya gajishe shi, bai kaso kome ba sai gauraka guda ɗaya tak. Da la'asar ta yi ya hawo dokinsa, ya dawo gida. Da isowarsa sai ya kawo gaurakan nan ya ba yaron ya dafa masa, dahuwa mai kyau, amma kada ya yanyanka, ya bar shi hakanan gudansa. Yaro ya je ya dafa ruwa, ya saka gauraka, ya fige sumul, ya tsage, sa'an nan ya ƙyafe shi. Bayan ya ƙyafe ya ɗauka ya tura cikin wata ƙatuwar tukunya, ya yi ta dahuwa har ya dahu limis, ya sauke tukunyar don ta huce. Da ta huce, ya sa nannu ya tsamo gaurakan nan ɗungum, ya ɗibiya bisa kwano. Ya yunƙura zai fita ya kai wa Sarki ke nan, sai wata bazawara wadda ya ke nema da aure ta faɗo ɗakin kwaram.

Bayan ta durƙusa ta gaishe shi, sai ta ƙyalla ido ta ga gaurakan, yawunta kuwa ya yi gudu, ta ce ya sam mata ƙafa guda ta ɗanɗana. Ya ce, "A'a, na Sarki ne, ba ni da iko in ba ki ko fiffike, ɗunguminsa haka Sarki ya ce a dafa."

Ta dube shi, ta ce, "To, abin da ke tsakanimmu ke nan, har cinyar gauraka ta fi ƙarfina? Ban zo gidanka ke nan ba, ran da na zo fa? Tun da na sai da kunyata na roƙe ka, Wallahi in ka hana ni ita ce za ta zama sanadin ɓatawarmu."

Yaron nan kuwa yana ji da bazawaran nan kamar ya haɗiye ta. Da ya ga dai ranta ya ɓaci sai ya ji tsoron kada su ɓata, ya sa wuƙa ya yankam mata ƙafa guda. Ya ɗauki saura ya kai wa Sarki.

Ko da Sarki ya duba ya ga an yanke ƙafa guda sai ya ce masa, "Ina wannan ƙafar? Ban gaya maka ba ka dafa shi gaba ɗaya? Kai wanda na zaɓa har ka fara munafunci ko?"

Yaro ya ce, "Ranka ya daɗe, ai gauraki ƙafa guda guda gare

su, ga ta kuwa nan. Ba ka lura ba ne, ai haka aka kawo mini shi."

Sarki ya buga masa tsawa ya ce, "Wawa! Yaushe ka taɓa ganin gauraka da ƙafa guda?"

Yaro ya ce, "Na rantse har da rawaninka na taɓa gani. Ai wannan abin mamaki ga halittar gauraka ba a ɓoye ya ƙe ba. Da kana da bukatar gani, ranka ya daɗe, da gobe tun da sassafe sai in kai ka ka gani da idonka."

Wannan jawabi na sakarci ya sa Sarki ya ƙume, har ya kasa magana. Sai can ya nisa ya ce, "To, je ka, Allah ya kai mu. Ai kowa ya yi ƙaryar dare, gari ya waye."

Yaro ya durƙusa ya yi gaisuwa ya koma ɗakinsa. Da ya je ya kwanta duk abin duniya ya dame shi, ya yi da 'ka ce' bai ɗauki wannan alkawari ba gaban Sarki. Ya yi shiru, ya ce, "Wai! Lalle dai baki shi kan yanka wuya. Amma ba abin da ya fi sai in mun je mun ga gauraki in ƙiririce ƙafa ɗai ɗai ke gare su. Ko yaya aka so a juya ni, in ƙi juyuwa. Tabarmar kunya ai da hauka kan naɗe ta. Da a ce na yi wa Sarki sata har ya sa a ci zarafina, ai gwamma a ce motsuwa na yi, Sarki ya fid da ni. Watakila ma in abin ga motsuwa aka maishe shi bayan kwana kaɗan sai a mai da ni."


Bai farga ba yana nan yana waɗannan saƙe-saƙen zuci yana kwancewa, sai ya ji ana kiran assalatu. Ko da ya ji ladan ya yi ƙara sai gabansa ya faɗi ras, ya ce, "Ta faru ta ƙare, an yi wa mai dami ɗaya sata." Ya tashi ya yi alwala, ya yi salla, ya ɗauki tasbaharsa ya shiga salati, yana roƙon Allah ya sa ya sami nasara bisa wannan al'amari. Ya kewaya tasbaha sau biyu ke nan, a na uku sai ga Sarkin Zagi ya zo ya kira shi. Ko da ya ce masa, "Sarki



na waje yana jiranka," sai gabansa ya faɗi, cikinsa ya ba da ƙulululu. Suka tashi suka fita.

Da fitarsu sai ya tarad da Sarki da Shamaki da Turaki da Shantali, kai, duk manya-manyan bayin Sarki dai sun haɗu suna jiransa. Ya faɗi ya yi gaisuwa, Sarki ya karɓa, ya ce, "Mu tafi." Ya shige gaba, duk aka bi shi. Yana tafiya kamar ba shi da rai, sai tuntuɓe ya ke yi don tsoro da kwarjinin Sarki. Ya duba gaba, ya duba baya, ba wajen gudu. Ga madaka ƙatti nan biye da Sarki, waɗanda ko wuta Sarki ya ce su faɗa kafin ya rufa baki sun kai. Sai ya dogara ga Allah, suka yi ta tafiya dai har suka zo bakin fadama, suka tarad da gauraki da yawa suna barci.

Ashe dai in gauraki suna barci sai su ɗauke ƙafa ɗaya su sa ta cikin fiffike, su tsaya bisa ɗayar, in sun gaji kuma sai su sako gudar, su janye waccan ta ƙasar. Ko da yaron nan ya duba ya gan su a tsaye bisa ƙafa ɗai ɗai, sai ya yi murmushi, ya ce wa Sarki, "Allah ya ba ka nasara, don ba ikon gardama da kai ne tun jiya, shi ya sa na ƙyale, amma duba ka gani, duk ƙafa ɗai ɗai ke gare su."



Sarki ya dube shi, ya ce, "Kai dai wawa ne. Haka su ke barcinsu, sai su janye ƙafa guda su tsaya bisa guda. Karya ka ke yi, ba ƙafa guda ke gare su ba. Kuma bari ka gani." Sarki ya yi tafi, ya ce, "Hirr! Hirr!" Duk sai suka sako ƙafafunsu, suka tsaya firga-firga, sa'an nan suka tashi. Sarki ya ce, "Ka gani ko? Kafa biyu biyu ke gare su."

Yaro ya ce, "Na gani yanzu, ko wanne ya sami ƙafa biyu biyu da ka yi musu ihu. Amma, ranka ya daɗe, wanda na dafa maka jiya

ba ka yi masa ihu ba sa'ad da na kai maka shi da ƙafa guda. Da ka yi masa ihu, Allah ya ba ka nasara, ai shi ma da ya fito da ƙafa gudar ya hutad da mu wahala, tun da ya ke al'adarsu ke nan in an yi musu tsawa.''

Wannan jawabi na wauta ya sa Sarki da mutanensa suka bushe da dariya. Sarki ya dubi yaron, ya ce, ''Gaskiyarka. Wancan da ka kawo mini jiya ban yi masa tsawa ba. Lalle shi ya sa muka gan shi da ƙafa ɗaya.'' Sarki ya yafe masa. Suka koma gida, suna ta yi masa dariya a kan wannan ƙiriricewa da ya yi.

Talakawa da ke can gefe guda suka fashe da dariya, suka ce, ''Duk labarurrukan da aka yi cikin 'yan kwanakin nan wannan ya fi su daɗi.''

Yau ko da gari ya waye sai ga wani ya fito daga Sirika ya zo ya ce wa Sarki, ''Allah ya ba ka nasara, ai maganin da aka kai mana ba mu taɓa samun maganin karaya mai amfani irinsa ba. Na rantse har da girmanka ko da muka dafa, aka tsoma hannun yau, aka tsoma gobe, gari na wayewa sai muka ga ya miƙe. Jiya da magariba kuwa da na sami mota na shigo, na bar shi har ya je kilisa.''

Sarkin Sirika ya ce, ''Don Allah raba mu da Waziri-wazirin nan ''Ka ji dai?''

Sarki Abdurrahman ya ce, ''Ka fara ganin aikin Wazirina ke nan.''

Sarkin Sirika ya ce, ''Don Allah raba mu da Aziri-wazirin nan naka. Shi dai ya i ma bakinsa ba laifi. Amma kana tsammani karaya ce yaron nan ya yi? Haba, 'yar gocewa kawai ya yi, duk suka ruɗe. Waziri naka ya sami sa'a, amma ka ga yanzu in ya ji sai ya dame mu da rigima. Bari in aika a kira shi ya zo mu ji yabon kai.'' Nan da nan aka aika Waziri Aku ya zo, aka gaya masa abin da aka aiko na labarin Dauda duka.

Waziri ya ce, ''Muddin dai kuna bin shawarata, in Allah ya so ba ku ganin tashin hankali. Yanzu kuma sai a koma a sami turɓayar tsamiya a kasuwa, a gama da kitsen agwagwa, a shafa masa game da wani ganye da zan ba ku yanzu, ya warke ke nan sarai.'' Ya tafi ya kawo ganyen, aka ba manzon nan ya koma. Sarkin Sirika na kallonsa yana dariya a ciki, yana tsoron kada ya yi a fili ya ɓata masa zuciya.

Suna ta kan hira nan har azahar ta yi suka tashi suka yi salla. Da suka gama, aka taru, Haziƙ ya shiga aikin da ya kawo shi:

# Zafin Nema Ba Ya Kawo Samu

Akwai wani mutum matsiyaci ne ƙwarai da gaske, ba shi da kome sai gatari da jakuna biyu. Sana'a ƙasa kullum sai ya tafi ya saro itace, ya ɗora wa jakunansa, ya kai kasuwa ya sayar, su yi awon abin da za su ci ran nan. Allah ya yi mutumin nan ba mai kasala ba ne ko kaɗan, rani da damina, kome ruwa kome ɗari, bai taɓa makarar tashi ba. Shekararsa kamar bakwai ke nan yana itace, bai taɓa fasawa ba, ko da rana ɗaya. To, ce ma ya fasa, me za su ci ran nan? Ga yara ƙanana. Da 'ya'yansa suka tasa suka shiga taimakonsa, amma duk da tarin ƙoƙarin nan nasa bai ƙulla kome ba, yana nan a matsiyacinsa.

Ran nan ya gaji, zuciyarsa ta ɓaci, ya zauna shiru ya rasa abin da ke masa daɗi nan duniya. Ya ce, "Kai na gaji da wahalar banza, mutum ya yi ta wahala shekara da shekaru, amma duk da haka bai ƙulla kome ba? Nan gaba in Allah ya yarda, na bar sake tafiya jeji garin saran itace. Bari in yi kwanciyata, idan da nufin nan gaba in yi arziki, ina bisa gadona ya zo ya iske ni!"

Kashegari ya yi kwanciyarsa, har lokacin tafiyarsa jeji ya yi, har ya wuce bai tashi ba. Matarsa ta tashi ta gama dukan aike-aikenta na gida, ba ta ji motsin maigida ya tashi ba, sai ta shiga ɗaki ta gani ko lafiya. Da ta shiga ta iske shi ya mimmiƙe a gado, ta ce masa, "Maigida, maigida, yau lafiya? Ba ka ji gari ya daɗe da wayewa ba? Ya kamata ka tashi hakanan mana, ka tafi neman mana abin da za mu ci."

Shi maigidan ko ma ya ta da kai ya dube ta, sai ya ce, "Haba uwargida, in tashi in yi miki aikin me?"

Ta ce, "A'a! Yau ba za ka tafi jeji ba ne?"

Ya ce, "Ba zan tafi ba. Ina amfanin dukan wahalan nan da na ke yi shekara da shekaru, tun da ya ke zan fita tun da jijjifi in tafi jeji, duk da haka da ƙyar zan sami abin da zan ciyad da ku?"

Ta ce, "To, maigida, haka Allah ya yiwo mu, sai mun yi fatafata sa'an nan mu samu. Kowa ka gani nan duniya kuwa haka ya ke, ba wanda ke kwance a gado. Yaya mu ka iya da rammu?"

Sai maigida ya ce, "Ni dai yanzu abin da zan gaya miki na gaji

da wahalar banza ta neman arziki, idan da nufin in yi arziki a nan gaba, ya zo har bisa gadona ya same ni, amma na daina wahalar banza har abada.''

Matar ta durƙusa, ta ce, ''Haba maigida, kada dai tsiya ta sa ka haukace mana, duk duniyan nan wa ka taɓa gani yana kwance arziki ya zo ya same shi a bisa kan gadonsa, in ba ya tashi ya nema ba? Tashi, saɓa gatarinka, fita da jakuna ka tafi jeji, ka yi abin da ka saba yi. Ya kamata ka gode wa Ubangiji Allah da ya ba ka ƙarfi da lafiya. Tashi! Yau ba mu da ko ƙwara a gidan nan.''

Mijin ya harare ta ya ce, ''Ke, na ce miki ban gode wa Allah ba ne? Ki rabu da ni, ko muna da hatsi, ko ba mu da shi, ni ban kula ba. Hasali ma dai tafi abinki, kada ki ƙara wahal da ranki a banza, duk duniyan nan babu abin da zai sa in koma saran itace.'' Matarsa ta yi, ta yi da shi, amma duk a banza, har ta gaji da 'yan surutanta, ta tashi.

Ba ta daɗe da tashi ba sai wani maƙwabcinsu wanda a ke kira Sambo ya zo gidan ya yi sallama. Matar ta fito, suka yi gaisuwa, ya ce mata ya zo ne ya roƙi arziki wajen maigidanta ko ya yarda ya ba shi aron jakunansa, yana da wani aiki ne, har shi ma idan yana da zarafi yana so ya zo ya taimake shi.

Sai matar ta shiga gida, ta shaida wa mijinta ana sallama a ƙofar gida. Mijin ya waiwayo da hushi, ya ce, ''Na rigaya na gaya miki duk garin nan babu wanda ya isa ya fito da ni daga kan gadon nan. Ko wane ne ya ke son ganina ya shigo.''

Sai matar ta koma ta shaida wa Sambo. Sambo ya shigo, ya mayar wa maigida da jawabi kamar yadda ya gaya wa matarsa. Amma maigidan ya ce, ''Wayyo, na rigaya na yi rantsuwa ba zan tashi daga nan ba, babu kuwa abin da zai sa in sake maganata.''

Sambo ya ce, ''To, in ba za ka ba, ka ba ni aron jakunanka idan na komo na taimake ka da abin sayen goro.''

Maigida ya ce, ''Haba, don wannan? Tafi da su, sai ka komo.''

Sai Sambo ya kama jakuna ya ɗaura musu mangala, ya fita. Ashe abin da ya sa ya ke neman aron jakkai ke nan, ya gano wani wuri ne inda ɓarayi suka ɓoye wadansu kuɗi gangariyarsu cikin wani kogon dutse. Sambo yana tsammani kuɗin Sarkin garin ne, don yau bai fi kwana uku ba da wadansu ɓarayi suka shiga taskarsa, suka yi masa ƙat, ana kuwa tsakiyar nemansu ne a lokacin nan. Saboda haka ya ke so ya kwashe kuɗin gaba ɗaya kafin a gane. Da isarsa wurin sai ya yi ta ɗibar kuɗin yana zubawa a mangala. Ya ɗiba gwargwadon yadda jakunan za su iya ɗauka. Ya sami wani tsumma ya rufe da kyau yadda ba za a gane abin da ke ciki ba, ya ɗauki wata 'yar hanya zai koma gida.

Yana cikin tafiya, kwaram sai ya hango waɗansu dogaran Sarki guda biyu. Abinka da mara gaskiya, yana tsoron kada su gane abin da ya ke ciki ya sani kuwa idan suka kama shi suka tafi da shi wurin Sarki shari'arsa kashewa ce. Saboda haka ya runtuma da gudu ya bar jakai. Su kuwa suka kama hanya, da ma sun saba bi zuwa itace, suka nufi gida, ba su zame ko ina ba sai a turkensu.



A lokacin nan kuwa matar gidan na waje na tsigar tafasa sai ta ga jakuna da kaya niƙi-niƙi, da ƙyar su ke cin ƙafa. Ta sheƙa a guje tana kiran mijinta ya fito, ga jakuna sun kamo ɗauke da wani abu mai nauyi.

Da maigida ya ji ta sha masa kai da kira ya ce, "Haba, don Allah na ce kada ki dame ni. Sau nawa zan gaya miki ba zan fito ba?"

Da dai ta ga mijinta ya ƙi tashi, sai ta tafi wajen jakai ta buɗa mangalolin, sai ga ƙarfe tsabarsu, sulalla ja wur, sai ɗaukan ido su ke. Da ganin haka sai ta sake sheƙawa a guje wurin mijinta, ta ce masa, "Don Allah ka fito maza. Ashe gaskiyarka da ka ƙi tafiya itace yau, kana jiran arziki ya zo maka har gado. Ga jakunanka sun komo ɗauke da sulalla. Na rantse har da kabarin tsohona, yau duk ƙasan nan babu wanda ya fi mu arziki!"

Da dai gagon naka ya ji haka sai ya yi farat daga kan gado, ya nufo waje da gudu zuwa wajen turken jakuna. Matar ta kama masa, ya sassauke mangalolin ya buɗa, sai hawaye don murna. Da shi da matarsa suka kinkima suka je suka ɗura cikin tukwane. Ya dubi matar, ya ce, "Uwargida, yanzu kin ga abin da na gaya miki ya zama gaskiya ba? Arziki abu ne mai wuyar kangado, muddin kai ke nemansa shi kuwa sai ya daɗa guje maka, amma in ka guje shi, sai ya neme ka har inda ka ke."

Matar ta ce, "Wallahi na dai yarda, gaskiyarka, maigida." Azahar ba ta yi ba sai ga Sambo ya biyo. Ya tambayi mai gida kayan da jakunansa suka kawo. Da mai gida ya gane kuɗin nan ba na Sambo ba ne, shi ma lalle akwai yadda aka yi ya same su, sai ya ce, "Allah ya ba ni ina kwance. Duk duniyan nan kuwa ba mai karɓarsu, in kana jin wani abu yi ƙara."

Sambo ya san kuɗin Sarki ne, lalle in ya faɗi aka gane, kashe shi za a yi. Saboda haka ya ce, "Je ka, na ji, Allah ne ya ba ka, amma kai kuma yadda Allah ya ba ka, in kana ƙaunarsa ka taimake ni."

Mai gida ya shiga ya kawo fam ashirin ya ba Sambo, ya karɓa ya wuce yana cewa, "M, ka ga halin 'yan Adam, ba su ganin mutum ya yi abu, su ma sai sun yi masa abu!"

Mutane da ke nan duk gaba ɗaya suka yi tafi, suka ce, "A'a! Yau mun ji abin mamaki, ashe mutane ba su sani ba ne su ke wahal da kawunansu a banza?"

Waziri Aku ya ce, "Ranku ya daɗe, kada ku bi ta wannan, ba kullum a ke kwana gado ba. Limamin Sama Jannati da ya kwaikwayi wannan bai ji gidan daɗin ba."

Sarkin Sirika ya dubi Waziri, ya ce, "Su wane ne kuma Sama Jannati, sai ka ce Dujal? Yaya Limaminsu ya yi? Don Allah gaya mana maza mu ji labarin waɗannan mutane.

Waziri ya gyara murya, ya ce, "Allah ya ba ka nasara, ka ko yi tambaya ga ɗan gida."

## Allah Na Taimakon Wanda Ya Taimaki Kansa


Akwai waɗansu Filani a wajen arewa waɗanda a ke kira 'Yan Sama Jannati, su ba su cikin Muhammadiya, ba su cikin Mashiya, suna nan dai kamar jemage, ba su nan, ba su can. Duk da haka a ganinsu kowa a cikin ɓata ya ke. Saboda haka ba su yarda wani mutum wanda ba ya bin addininsu ya shiga ko ƙauyen da su ke. Mutanen nan ba su sa riga sai warki, ba su wanki, ba su wanka, ba su shan miya da gishiri, ba su cin nama. Kai, wani abu duk na ban sha'awa cikin abubuwan duniyan nan ba su yi, wai duk bidi'a ce.

Matansu kuwa ba su ganin kowa sai 'yan'uwansu. Idan wani al'amari ya tilasta baƙo ya shiga wurinsu, sai su rurrufe matansu cikin gida har baƙon nan ya gama abin da ya kawo shi ya tafi.

Babban abin mamaki cikin addininsu, shi ne wai tun asalin addinin nan wani ya taɓa gaya musu can zuwa ƙarshen zamani wata shekara za ta zo sa'ad da Ubangiji zai ba su ikon su tashi kamar tsuntsaye, su rabu da duniya, don sa'annan za ta faye dauɗa har bai kamata ba ɗahirai kamarsu su zauna cikinta. Saboda haka ko wace shekara sai su yi taguwoyi masu manyan hannuwa, su sallami iyalansu su ce za su je su gani in lokacin tashi ya zo. Sai su ce in ba su dawo ba, matan su kuma su sa nasu taguwoyi su bi. Dalilin da ya sa su ke yi wa taguwoyin manyan hannuwa don su zama kamar fikafikai, su taimake su wajen tashi. Idan sun tafi sai su tsaya gindin wani itace su ce wa Limaminsu ya fara, don ya fi su tsarki duka. Sai Limamin ya hau itacen ya kai can ƙoluluwà, sa'an nan ya yunƙura ya yi tsalle ya bar itacen ya yi ta kaɗa hannu buja-buja yana yiwo ƙasa, su kuwa sai su yi ta cewa, "Sama Jannati, Sama Jannati, Sama Jannati," har ya kawo ƙasa. Sai ka ji tim, nan zai karairaye rugu-rugu, ba ya ko motsawa. Sai su kai shi gida su rufe, su ce wa matan, "Liman ya kasa, bana ma ba sa'a, sai Allah ya kai mu baɗi kuma." Sai su nemi wani wanda ya cancanta su yi masa Limami. Haka su ke yi ko wace shekara.

To, cikin Limamansu ne ran nan wani na yawo a daji, sai ya ga

shaho ya ɗauko ɗan tsako ya kawo wata sheƙa ta hankaka, yana gutsuttsurawa da haƙori, yana ba ɗan hankaka yana haɗewa. Shahon nan kuwa ko sau ɗaya bai haɗiye ba. Da ɗan hankakan nan ya cinye, sai shaho ya tashi ya nufi neman wani.



Da Limamin nan ya ga haka sai ya riƙe baki ya ce, "M, ashe tun da haka al'amarin Ubangiji ya ke, don me na ke wahal da kaina a banza, in faɗi nan in tashi nan don neman abinci? Dubi hannuna yadda ya yi kaushi, dubi ƙafata yadda na sossoke don rashin sani, dubi bara yadda maciji ya sare ni wajen noma. Ashe duk abin da ya same ni dai ba ni da kaito, rashin danganata ya jawo mini. Ba abin da ya fi yanzu sai in sami wata 'yar bukka a gonata in shige in kwanta, in roƙi Allah ya nufe ni da samun abinci a nan kwance yadda ya nufi ɗan hankakan nan da samu, ko da ya ke da shi da shaho ba dangin uwa ba na uba." Sai ya tashi ya tafi gonarsa ya shige bukka ya kwanta, ya ce wa iyalinsa kada kowa ya zo wajensa ko ya kawo masa wani abu. Shi da fita bukkarsa sai bayan ya zama waliyyi.

Yana nan kwance kamar kwana uku, shi ba azumi ya ke yi ba, ba ko salla ba, ba wata addu'a kuma ya ke ja ba, ya yi ta ramewa kullum har ta kai ga inda ba ya iya ko fita fitsari. Yana nan dai sai jira ya ke wani abinci ya zo masa ya ci. Tun yana ƙulla irin waɗanda ya fi so su zo masa, har ya gaji ya bar zaɓe. Ya kwanta ya ce ko kunu ya zo masa yana so.

Yana nan can bayan kwana uku ya kai gargara, sai ya yi mafarki an ce masa, "Ba ƙarya ka yi ba, wannan bawa, Ubangiji na aikata abin da ya so, domin shi ne mahaliccin kome. Yana iya

mai da dare rana, ya mai da rana dare, shi ke ci da tsuntsayen sama, ya ci da kifaye da kwaɗi na cikin ruwa, ya ba dabbobi da mutane hanyoyin da za su yi su sami abinci. Amma ko cikin littattafan da ya sauko da su an ce Ubangiji na taimakon wanda ya taimaki kansa. Kuma in kana son kwaikwayon tsuntsayen nan da ka gani guda biyu, sai ka kwaikwayi shahon wanda ke ci da hankakan nan, ba hankaka wanda a ke ciyarwa ba. Hankakan ya faye ƙanƙanta, har ba ya iya tashi ya nemi hanyar da Ubangiji zai taimake shi ya sami abinci. Kai kuwa Allah ya ba ka ƙarfi da lafiyar da za ka iya tashi Ugangiji kuwa ya taimake ka. Tashi, ka kwashe iyalinka ka nufi cikin mutane, ka kama addini da gaskiya, ka bar jahilci, kada ka mutu kana kafirci, ba ka ga samun duniya, ba ga na lahira.''

Daga nan sai Limamin nan ya farka. Allah kuwa ya yi masa gyaɗar dogo, yana farkawa sai ga wani daga cikin 'ya'yansa yaňa kewayar dabin ya gani in yana nan da rai, sai ya kira shi. Yaro ya zo, ya ga ubansa ya fita daga kamannin mutane. Sai ya ruga gida ya faɗi, aka zo da gudu, aka ɗauke shi kamar matacce aka kai gida aka yi ta jinyarsa, da ƙyar aka samo shi.

Da ya farfaɗo ya yi ƙarfi, sai ya tara mutanen unguwan nan duka ya gaya musu mafalkin da ya yi. Ya kuma ce shi daga ran nan ya fita daga cikin addinin Sama Jannati. Ya kwashe iyalansa ya koma gari, ya shiga Muhammadiya. Saura kuwa suka ce ba su barin abin da suka gada kaka da kakanni. Suka naɗa wani Limaminsu, Shaiɗan ya ƙara iza su cikin wannan ɓata. Inda jahilci ya yi kauci sakarci ne mutum ya je ya ce zai nuna wayo a wurin. Allah ya kiyashe mu, amin!

Sarakunan nan suka ce, ''Kai, ai ko waɗannan Filani sun isa sakarkaru. Wai ko don Allah labarin nan gaskiya ne, Waziri? Akwai Filanin da a ke kira 'Yan Sama Jannati, ko kuwa shara ta ka ke yi?''

Waziri aku ya ce, ''Allah ya ba ka nasara, ai ni ba na ƙarya, sai dai don abin da ba a rasawa, don an ce mai rai duka ba ya rasa kuskure hanya wata rana. Amma dai nan arewa na rantse har da girmanka akwai Filanin da a ke kira 'Yan Sama Jannati. Ba don kada in tsai da ku ba, ai da na ƙara gaya muku labarin wani ɗan'uwansu, wanda cikin ransa bai taɓa aikin kirki ba ya zama waliyyi a cikinsu bayan da ya mutu.''

Sarkin Sirika ya ce, ''Don Allah ci gaba, la'asar ma ai ba ta yi ko kusa ba tukuna.''

Waziri ya shirya zai ci gaba, sai aka hanga waje mai motar Sarkin Sirika ya zo. Aka dakata ya shigo, ya faɗi gaban Sarkinsu, ya ce, ''Allah ya ba ka nasara, ai taskarka ta buɗe, yau ba sauran

ko kwabo ciki. Jiya da dare ɓarayi suka tafi ɗakin uwargidan suka sato mabuɗanka da ke gare ta duka, suka buɗe taskar suka yi mata ƙat. Tun da safe da aka gani wakilin gari ya sa 'Yan Doka da Dogarai da 'yam barga suka hau suka watsu cikin ƙasa gabas da yamma, kudu da arewa, ana ta nema har kusan azahar ɗin nan, ba a ji ko motsinsu ba. Da Wakilin gari ya ga haka, ya ce in hawo maza in gaya maka, don ko za ka koma ka gani."

Mutane suka yi tsit da suka ji wannan labari. Sarkin Sirika ya ce, "To, in tafo in ga me? Ni kaɗai ina da ikon in aikata abin da mutanen nan da aka baza ba su aikata ba? Sai ka koma ka ce wa Wakilin gari a tsananta nema, ni kuma ina tafe in Waziri Aku ya ba da labaransa."

Sarki Abdurrahman ya dubi Waziri Aku, shi kuma Waziri Aku ya dubi Sarkin Sirika, ya ce, "Allah ya ba ka nasara watau da na ce a aika maka ka zo da mabuɗan taskokinka, ƙin bin maganata ka yi?"

Sarkin Sirika ya ce, "Wallahi mayarwa na yi kamar ba'a ka ke yi."

Sarki Abdurrahman ya ce, "Abin da na gaya maka batun Wazirin nan nawa ya fi kyau ka yarda. Ni na san abin da na ajiye a nan. Banza ba ta kai zomo kasuwa." Ya dubi Aku, ya ce, "Don Allah Waziri, kada ka yi fushi, ka ƙara taimakommu kuma da abin da ya kamata."

Waziri Aku ya ce, "To, ba kome Allah ya taimake mu. Amma dai ina mamakin yadda Sarkin Sirika ke raina maganganuna haka, kamar bai sani ba ajiyar Allah yawa ke gare ta."

Sarkin Sirika ya rasa abin da zai ce, ko fushi ya ke, ko mamakin aku ya ke ba wanda ya sani. Can Waziri Aku ya dubi mai motar da ya zo, ya ce, "Koma maza Sirika, a sami wani yaro ko ɗan wane ne wanda bai yi bante ba, a tasa shi gaba a ce masa mu je unguwa, a yi ta binsa, kc ina ya karkata kada a ce masa bi nan. Ƙofar gidan duk da ya gaji ya tsaya a bakinta, dogarai su kewaye gidan. Ɓarayin nan, ba su fita gari ba tukuna." Mai mota ya hau nan da nan ya koma. Mutane suka yi ta duban Waziri Aku. Haziƙ na kaikaitar idonsa yana yi masa dariya.

Sarki Abdurrahman ya dubi Sarkin Sirika, ya ce, "Sai a tashi hakanan, in hankali ya kwanta a ci gaba."

Sarkin Sirika ya ce, "A tashi? Tun da ka ga na kasa komawa Sirika don dai in tsaya in ji ƙarshen waɗannan labarai, ai ka san ba na iya tashi ba a ƙare su ba. "Ya dubi Waziri Aku, ya ce, "Don Allah bismilla. Abin da Allah ya ƙaddara yana da makawa ne?"

Waziri ya ce, "Gaskiya ne, Allah ya ba ka nasara." Ya gyara tsugunni, ya soma:

# Labarin Ja'iru Ɗan Sama Jannati

Wani ɗan Sama Jannati ne ya gaji da irin zamansu na rashin more wa duniya, yadda na gaya muku ɗazu, ya ga abin ba wani abin tsishi su ke yi ba, wauta dai ce da ɓatan basira. Saboda haka ya rabu da su, ya shiga duniya abinsa, har ya kai wani gari wai shi Ƙukoki. Sunan mutumin nan na sosai Ja'iru, amma ko da ya rabu da garinsu sai ya ce shi sunansa Kowa-tasa-ta-fisshe-shi. Mutane suka yi ta kiransa haka, don taƙaitawa har suka riƙa kiransa Kowa kawai.

Watakila abin ya ba ka mamaki yadda wannan Bafillace ya lalace gaba ɗaya da shigowarsa cikin mutane, ga shi da na gaya muku sun mai da kome bidi'a. To, amma ka ga ko da Kowa ya shigo cikin mutane sai ya fi mai kora shafawa. Sannu sannu har ta kai ga ya zama in ka tashi neman ja'iri ka ga Kowa-tasa-ta-fisshe-shi sai ka koma gida, bukatarka ta biya. Ka san Bafillace a kan zuciya da hushi, amma ko zagin uwar Kowa ka yi ba ya ko dubanka, sai ya yi dariya. Karya kuwa a bakin Kowa, abin har da na kai kasuwa. A Kukoki da fari fadanci ya soma, cikin wata guda ya yi ƙarairayin da suka sa Sarkin ya fid da hakimai huɗu daga sarauta. Idonsa idon mata kuwa sai ka ce kare. Yatsun hannu ma tara gare shi, gudan wajen shige aka koro shi har aka kai masa sara, ba a same shi sosai ba, aka yanke wannan yatsan da takobi. Abin da na tabbata kuwa a halin Kowa, ko uwarsa ta ba shi amana, ya ci.

Sarkin Kukoki da ya gaji da kawo masa ƙarar Ja'iru kan cin amana, sai ya sa aka yi yekuwa kowa ya ba shi wani abu, in ya ci amanarsa kada ya ce zai yi ƙara, ya kuka da kansa. In kuwa batun tsafi ne, ko Sarkin Tabuka ya san da shi. Kai, har ma Danko gare shi. Mutane na zuwa yana yi musu ƙarairayi wai Danko ke magana, wanda ma ke wa kansa kirari yana cewa sai shi Jatau jikan Kisira! Duk inda ya ke ƙara ba mutane haushi sai ta wajen roƙo da rowa, ko na goye ya san da shi. Shi ne aka samu wanda bai ji abu ba, bai ko gani ba, amma idan aka tambaye shi sai ya kanannaɗe ya ce shi ya ji ya gani. Ya tsuguna yana ta rantse-

rantsen ƙarya, ya kwaɗa shaidar zur. Da ko ka ba shi sule talatin ya yi maka shaidar gaskiya, gwamma ka ƙyale shi ya yi ta ƙarya a karin banza da wofi. Wanda ya yi wa shaidar zur ya sa aka kashe, Allah ya yi yawa da su. In ko batun gama masoyi da masoyi ne, wannan har ya zama jiki gare shi, har ma ran da bai gama waɗansu husuma ba, ba shi da sukuni. Wanda ke shiga tsakanin ɗa da mahaifi ya sa su ɓata, ya raba mata da mijinta! Da ya zauna sai ka ce Ibilis, ban da munafunci da kitiko da kissa da annamimanci, ba ya ƙulla kome tsakanin mutane. Da yawa ya kan shiga cikin ɓarayi, a je a yi sata, ko fashi, ko kisan kai. Kai, Allah ya ba ka nasara, ta kai ma har sufurinsa a ke yi ya je ya yi kisan kai, a biya shi lada. Da ran mutum da na ƙuda, duk ɗaya ya maishe su. Duk'abin da za a yi a ce tir, to, Kowa-tasa-ta-fisshe-shi shi ne gaba a wannan wuri. Kai, in na ce abin in tsaya ne in bayyana maka halayen Kowa sosai sai ka ce lalle da zamanin da ne, kafin Annabi ya bayyana, in aka sami kamarsa huɗu a gari sai a kife garin domin saɓon nasu ya yi yawa.

Ana nan ana nan, da ya addabi mutanen gari sai suka game masa kai, suka hana masa ko ruwan sha. Ja'irin naka da ya ga haka sai ya riƙa zuwa kasuwa yana ƙwace, duk ya dami mutane. Da Sarki ya sami wannan labari, sai ya sa dogarai su tambaye shi ƙofar da ya ke so, su raka shi ya fita ya bar garin.

Da aka kore shi, ya shiga daji, sai ya ce, "Af, da ma in tafi wani gari, ba gwamma in koma garimmu ba, in ma hore su su san al'amuran duniya?" Sai ya karkata ya nufi garinsu na Sama Jannati.

To, bayan wannan babban laifi da ya yi na rabuwa da addinin Sama Jannati, 'yan'uwansa kuma sun ji labarin abubuwan da ya ke aikatawa duka a Kukoki, waɗansu ma har sun tafi sun gano da idanunsu. Da suka yi tsammani abin da a ke faɗi ba gaskiya ba ne. Saboda haka da ya isa gidansu sai 'yan'uwansa suka ce su ba su zama da shi. Suna shirin korarsa, ran nan sai ya kwanta masassara. Abu duk ya dame su, suka kai shi can wata bukka a bayan gidansu suka kwantar. Da farko yana iya tashi, amma daga baya ya zama sai a kwantar, a tayar.

Abin duniya fa duk ya taru ya cuɗe wa 'yan'uwan Ja'iru, ya zama musu alaƙaƙai ƙadangaren bakin tulu. Su ba abin su ƙyale shi ya mutu ba, a ce sun kashe ɗan'uwansu, su ko bai kamata ba su zauna suna mlillika da kafiri, wannan ko babban zunubi ne ga addininsu. Da abin ya dami masu gidan, sai suka taru a bayan bukkar da Ja'iru ya ke kwance, suna shawarar abin da za su yi masa. To, duk cikinsu Ja'iru ba shi da wani muhimmin ɗan'uwa, ubansa dai ya mutu, uwarsa ta mutu, ba shi da wa, ba shi da ƙane,

ba shi da ɗa, ba shi da jika, sai aukin 'yan'uba da kawunnai maza da mata. Da suka fara shawaran nan waɗansu suka ce, "Yanzu dai in mun kai shi daji mun yar wannan abin kunya ne a gare mu, domin fa ɗan'uwammu ne. Idan mutane suka ji haka, lalle mun shiga uku. Kuma idan muka bar shi ya mutu nan, lalle mun ƙare ganin baƙin ciki, don ba wanda zai taho wajen jana'izarsa. Dole sai mu haƙa rami sa'an nan mu jefa shi, domin fa in Liman bai yarda ba, wa ke da ikon yi masa salla, ya bi shi a banza? Kai, Allah dai wadan naka ya lalace!"

To, ashe duk abin da su ke faɗi kan kunnen Ja'iru ya ke, yana kwance yana ji ko da ya ke rai ga Allah. Da ya ji abin da suka ce, sai ya amsa musu ya ce, "Duk na ji abin da ku ke faɗi, na sani ko gaskiyarku. Amma don Allah kada ku ta da hankalinku a banza bisa kan wannan. Yanzu abin da na ke so da ku, sai ku tafi ku kira mini Liman, ya zo in gaya masa zunuban da na aikata tun daga haihuwata har yanzu. In ya ga mai zunubai irin nawa ya cancanci ya yi masa salla, ya yi mini. In ya ga kuwa ba ya taɓa irina, sa'an nan sai ya gaya muku abin da za ku yi da ni ku yi, kun ga ku kun fita zargi ke nan."

Da 'yan'uwan nan na Ja'iru suka ji haka sai suka yi murmushi suka ce, "Da mu yi wa kammu wannan tonon silili, ba gara mu ƙyale ka ba, in ka mutu sa'an nan mu san dabara? In muka kuskura muka bari Liman ya ji irin halayenka, bari ta kai da ka aikata su, ko mu da muka gama dangantaka da kai ma ƙara shan ruwa garin nan, in suka kafa mana tsana?"

Ja'iru ya dame su da su kira masa Liman dai, su kira masa Liman. Da ya ga mazan sun yi biris da maganarsa, sai ya gaya wa wata ƙanwar uwarsa ta tafi ta kira Liman.

Da zuwan Liman sauran 'yan'uwan Ja'iru suka tashi suka maƙe a bayan bukka, don su ji abubuwan da Ja'iru zai ce ya yi. Liman ya zauna a bakin gadon da Ja'iru ya ke kwance, ya gai da shi, ya tambaye shi yadda ya ƙara ji.

Ja'iru ya amsa, ya gaya masa kuma abin da 'yan'uwansa suka ce duka, da kuma shi abin da ya ke so Liman ya yi masa. Liman ya ce. "To, gaskiyarka." Ya fara tambayarsa ya ce, "To, kai da fari ma, me ya sa ka rabu da iyayenka, ka fita daga addinin da ka gada kaka da kakanni? Tun da ka aikata wannan mugun abu, ai ka san kome 'yan'uwanka suka ce lalle suna da gaskiya."

Ja'iru ya dubi Liman da wutsiyar ido, ya ce, "Lalle ni dai na yi kuskure, shugaban addini. Amma ƙuruciya da kuma gudun jin kunya daga baya, su suka sa na ƙi gaya muku dalilin da ya fid da ni gida. Amma na rantse har da girman da ke gare ka wajen wannan addini, da ɗaukakar da ke gare ka wajen wannan ƙoƙari

naka, ko da na rabu da ku addinin Sama Jannati na ke yi. Idan lokacin tashi ya yi ko wace shekara, sai in tafi daji in tsaya gindin wani itace ina tuna abubuwan da ku ke yi a lokacin. Abin da ya sa kuma na rabu da ku, don da so na yi in je cikin Musulmi in ga irin ɓatan da su ke ciki, in zo in gaya maka, mu shirya mu'je mu fara jihadi da su. Domin bai kamata ba kamarka na duniya a sami mutane da yawa haka cikin ɓarna. To, ga shi yanzu ba na cikin sukuni, balle mu san shawarar da mu ke ciki."

Liman ya shafa kan Ja'iru, ya ce, "Ai wannan niyya da ka yi ita ce a ke so ga addinimmu, rashin yawa shi ya hana mu motsa kome. Ai wannan tafiya taka lalle da gangan mu ke zarginka a kanta. Ladanka daidai ya ke da wanda ya yi hajji. To, bayan wannan in ji ba ka taɓa kisan kai ba?"

Tsaya ka ji lalataccen naka wanda ya ke har hayarsa a ke yi a ba shi kuɗi, a sa shi ya je ya yi kisan kai! Sai ya ce, "Ba na cewa ban taɓa yi ba. Don wata rana wani ɗan fashi ya tsare farke, ya kama farken ya kayar, ya zaro wuƙa zai yanka shi ya kwashe kayan, sai Allah ya sa na faɗo wurin na yi masa bararan nan tawa, ya zabura da gudu. Abin tsautsayi, sai ya faɗa wani rami sa'ad da ya ke waiwaye ko ina biye da shi. Da na ga bai tashi ba sai na tafi in duba ko ya ji ciwo, sai na tarar ashe faɗuwan nan da ya yi ya karye wuya. Na cicciɓe shi, ashe har ya riga mu gidan gaskiya. Ka ji inda na yi kisan kai."

Liman ya ce, "Wannan ai ba ka da laifi a ciki, alhaki ne ya kama shi. Wannan ba laifi ba ne. Sai dai ina son in ji ka taɓa yin ƙarya?"

Ja'iru ya ce, "Ba sau ɗaya ba, ba sau biyu ba, sai dai Allah ya yi mana gafara. Don wata rana wani abokin tafiyata da ya ga ba na Addinin Musulunci ya tsegunta wa wani Sarki, don a musuluntad da ni. Gudun haka ya sa na ce wa Sarkin ni da ma Musulmi ne, ka ji ƙaryar da na yi ɗaya. Wata rana kuma na yi shaidar zur ga wani maƙwabcina. Shi ko abin da ya sa, kullum dare ni ban san ɗalili ba sai in ji yana ta dukan matarsa. Ran da kuma ya yiwo sha, in ya kama ta da duka sai ka ce ba zai bar ta da rai ba. Saboda haka ran nan da na ga abin ya wuce kima, na gaya wa mai unguwarmu ya tsawata masa. Na ce ita ke da gaskiya, ba shi ba, ko da ya ke ban san hakikanin abin ba."

Da Liman ya ji haka sai ya riƙe baki, ya ce, "Ai kai, waɗannan irin halaye naka nan duniya ba mai irinsu. Waɗannan ai ba laifi ba ne." Ya dafa shi, ya ce, "To, yaya wajen sha'anin mata da shaye-shaye?"

Ja'iru ya kau da kansa, ya ce, "Wannan ina jin kunyar in gaya maka al'amarina game da su."

Liman ya ce, "Ai ba wani abin jin kunya tsakanimmu da kai. Kome munin zunubin da ka yi, in muka sa baki ga roƙo sai ka ga abin ya kyautu."

Ja'iru ya ce, "Ai ko wajen tafiyar da na yi na ga alamar haka. Ko wane abu ya rikice mini, in na faɗi sunanka sai in ga hasken abin."

Liman ya yi murmushi. Ja'iru, wanda ba shi da ko ruwan sha sai giya, ya kaikaita da kansa ya yi masa gwalo, ya dube shi, ya ce, "Bara da watan tashi sama ya tsaya sai na yi ta ibada ba dare ba rana, ina ta roƙon ka sami sa'a mu tashi. Ba na ko cin abinci, ba na ko jin yunwa. Ranar ashirin gare shi da magariba aka kawo mini sadakar kifi, ina ɗan ci sai ƙayar ta sarƙafe mini a wuya. Mutanen gidan da na ke da suka ga zan halaka suka ba ni giya na kurɓa, ashe wai ita ce magani, ni ma ban san giya ba ce sai da ya wuce na warke sa'an nan suka gaya mini, duk raina ya ɓaci. Wannan shi zai hana ni rantsuwa in ce ban taɓa shan giya ba." Liman ya dube shi, ya kaɗa kai.

Ja'iru ya ce, "Wajen sha'anin mata kuwa ba na cewa ban taɓa ƙauracewa da wata ba. Domin cikin yawon da na yi da na sauka wani gari mutanen garin suka ga yadda na kame kaina, ba wani wasa sai addini, sai suka fara tasam ma sa ni girman kai. Suna cewa wai ni irin waliyyan nan ne da ba a sani ba, saboda haka suka yi ta girmama ni. In abinci na ci sai a wawashe, wai ana neman tubarraki. Kowa wani abu ya same shi sai ya zo in yi masa roƙo, in ko na yi sai ka ga abin ya samu. To, da na ga za su sa ni fariya, su hana ni bautata, sai na gama kai da wata, na ce ta zo ɗakina, don in mutane sun gan ta ciki sai su yi tsammani ni ja'iri ne, su watsad da ni in yi ta ibadata. Ka gani kuwa ko da na yi hakanan sai na sami lafiya, Allah ya ba malam sa'ar tashi bana! Ka ji hana rantsuwa."

Ko da Liman ya ji haka, sai hawaye suka zubo masa don tausayi. Ya tashi ya rungume shi ya ce, "Ai mutanen nan ba ƙarya su ke yi ba. Allah ya maishe mu danshinka, babu sauran abin da za a zarge ka kansa."

Ja'iru ya ce, "A'a, ƙara tambaya dai." Ya kaikaici idonsa ya yi masa gwalo. Ya ce, "Ina da waɗansu laifuka biyu da ban gaya maka ba don kunya."

Liman ya ce, "Haba, cikin irin laifofinka ai ba na jin kunya, ko mu da aka shaida mu ɗahirai ne, in muka samu hali irin naka ai mun gode. Faɗi mu ji."

Ja'iru da na gaya maka tun farko kowa ya san shi kan cin amana, wanda ko uwar da ta haife shi ta ba shi amana ya ci sai wai ya ce, "Na farko, na taɓa cin amana sau ɗaya. Shi ko dalili,

bara waccan ne cikin watan tashi na sami sule, na tafi kasuwa, na yiwo canji don in zo in ba da sadaka, ina rokon Allah ya ba ka sa'ar tashi, don na ga duniyar ta lalace, dauɗa ta yi yawa. To, cikin kuɗin da na yiwo canji, da na zo na ƙidaya, sai na ga anini ya hau. Na koma kasuwa na yi neman mutumin da na yi canjin wurinsa, ban gan shi ba. Na yi nemansa har shekara guda. Da dai na ga ba zan gane shi ba, sai na yi masa sadaka da aninin. Ka ji babbar cin amanar da na taɓa yi."

"Na biyu, na taɓa tsegumi sau ɗaya. Wannan kuwa, wata rana ne na sauka wani gida, ashe gidan ɓarayi ne. Can da tsakad dare sai na ji suna shawara wai gobe, in dare ya raba, gidan Limamin garin za su yi wa tsinke, su kashe shi, su washe gidan sarai. Da na ji haka, sai duk tausayi ya kama ni, na tuna da yadda ka ke, ga shi za a kashe maka ɗan'uwa, ko da ya ke shi hanyar ɓata ya ke jan mutanensa, ba kamar kai ba. Duk da haka sai na tashi, da gari ya waye na tsegunta wa Sarki, aka aika da Dogarai a asirce, suka maƙe gidan Liman. Inda Allah ya fid da ni, dare na rabawa sai suka zo. Dogarawan nan suka kama su, aka ɗaure. To, ka ji laifuffukan da na yi ina jin kunyar gaya maka."

Sai Liman ya ƙara matsa shi a jiki, yana cewa, "Ba shakka kai waliyyi ne. Allah ya ba mu albarkacinka, ya sa mu bisa kan tafarkinka!"

Ja'iru ya kaikaici idonsa, ya yi masa daƙuwa, ya ce a ransa, "Da kun ƙara lalacewa! Ko ban kashe mutum ba, ɗai ɗai ai na kashe ɗari. Tsegumi kuwa bakina, ai ko tsohuwar da a ke wa kirari 'Fasa gida gyara kasuwa' na sha kanta."

Liman ya dafi kafaɗar Ja'iru, ya ce, "Af, na manta da in tambaye ka babban abu, na ce ko ba ka taɓa yin tsafi ba?"

Ja'iru ya tofad da yawu tuf, ya ce, "Tir, tir, tir! In aka ce kamata ya yi tsafi, wanda ya fita neman jihadi, ai abin ya ~~ba da~~ tsoro. Allah ya tsari 'Yan Sama Jannati da wannan, tir!" Ya zunɗi Liman da baki, ya ce a ransa, "Tsafi duk ya fi abin da ku ke yi? Cikin wane littafi kuka sami wannan addini, wai wani abu Sama Jannati? Sai fa cikin littattafan Shaiɗan. 'Yan nema ɓatattu, da ni da ku ai raɓa ke raukar raɓa!"

Liman ya ce, "Madalla! Tun da ba tsafi dai, ai kome ya yi kyau."

To, da ma abin da ja'irin ke fama da shi ciwon ciki ne da masassara. Ka san halin ciwon ciki murɗe-murɗe ne. To, yana ƙare wannan magana sai ciki ya murɗe shi, ya yi ta juye-juye yana nishi, yana kuka don zafi. Da Liman ya ga haka, sai hankalinsa ya tashi, ya ce, "Malam, lafiya?"

Bari ka ji aikin jairin naka, duk da wannan azaba da ya ke sha,

sai ya ce wai ya tuna ani zunubi ne da ya yi mai girma, shi ya sa shi kuka.

Liman ya ce, "Ai kai, ba ka da wani zunubi. Irin waɗannan ayyuka naka, ai kai har yanzu salihi ka ke, kamar yadda aka haife ka. In ka cika cikin wannan ciwo, ai ba mu san abin da za mu kira ka ba. Amma faɗi mu ji abin da ka tuna."

Kafirin naka wanda ko burgu ya san da shi a kan sata, sau biyar ana ɗaure shi, sai ya ce, "Duk gudun duniyan nan nawa wata rana sai da ta kai ni da yin sata. Abin da ya sa kuwa, wata rana da maraice na fita yawon ya da rana, kamar yadda na ke yi in na gaji da wuridi, sai na tarad da wata kasa ta laɓaɓo tana cin abincin da waɗansu fatake suka ajiye sun kuwa tafi cikin gonaki su yiwo wa jakunansu kara. Ko da na ga haka sai hankalina ya tashi, na yi ɗuban ko na gan su in gaya musu kada su ci abincin, ban gan su ba. Sabo da haka da na ga kasan nan ta wuce sai na je na sace abincin, na kai wani rami na rufe, na wanke musu kwanonsu na mayar musu, don tsoron kada in wuce su zo su ci abincin nan su mutu. Ka ji wannan laifin da na yi na sata. Kullum yana raina, in na tuna shi sai in rasa abin da ke mini daɗi, har in yi ta kuka."

Liman dai bai sami ta cewa ba, sai ya rungume shi kawai yana sumbantarsa yana cewa, "Ni dai don Allah ka yi mini addu'a bana in sami sa'ar tashi. Addu'ar irinku ai ita ce abin nema?"

Makirin naka sai ya kaɗa kai, ya ce a ransa, "In dai ga addu'ata ka ta'allaƙa, bari wata marairaicewa, bana ƙaton kan nan naka sai ya sha ƙasa!"

Sai Liman ya fita ya tafi wajen mutanen gida, ya gaya musu su zo su ɗauki Ja'iru, daga nan su mai da shi cikin gida. Ya ce musu waliyi ne, su lura da shi, ko sa sami albarka. Nan da nan aka yi abin da Liman ya ce.

Da ma duk abin da su ke faɗi na gaya maka a kan kunnensu ya ke, domin suna maƙe suna ji. Suka yi ta mamakin Ja'iru, suna cewa, "Don Allah dubi yadda kafiri ya kalallame Liman da ƙarairayi da daɗin baki, har ya sa muka kawo shi gidammu. Yanzu mu ba abin mu je mu gaya wa Liman ƙarya ya ke yi ba, a ce hassada mu ke yi. Ba abin da ya fi sai mu rufa wa kammu asiru mu ƙyale, ai akwai ranar ƙin dillanci!"

Da ma ciwon ashe abokin tafiyar Ja'iru ne. Gari bai waye ba ya haure. Kai, Allah ya kiyashe mu da jahilci! Nan da nan sai aka kira Liman ya zo. Liman ya zo kirin-kirin, ya sa aka yi yekuwa gari kowa mai neman albarka ya zo wajen jana'izar waliyi. Da aka taru makil (da ma al'amarin jahilai) aka yi masa ayyukan jahilci, aka binne shi. Liman ya sa aka gina ƙatuwar shigifa

kewaye da kabarinsa. Aka samo rairayi irin mai farin nan na kogi, aka zuba.

Daga nan fa sauran al'amura na bar muku sani. Shaiɗan ya shiga gaba, ya yi ta jansu zuwa ziyarar ja'iri. Kullum sai a yi ta kai sadaka, ana zuwa roƙo. To, ka ji yadda wannan mutum wanda duk cikin ransa ba wanda ya fi shi shegantaka, bayan da ya mutu ya zama babban waliyyi a wurinsu.

Kai, muna roƙon Allah ya kiyashe mu da irin halayen Ja'iru! Dubi, don Allah, sa'ad da mutane ke neman su samu Allah ya ba su damar tuba da yin kalmar shahada, ja'irin naka sa'an nan ya ke gwabɗa wata ɗanyar. Allah ya kiyashe mu da halin Ja'iru!

To, da aku ya ƙare wannan labari, sai gargaɗin nan da ya yi ya ba shi sha'awa, ya yaba wa kansa hikima. Sai ya tuma, ya karkace kai, wai zai cika labarin da waƙa. Bai san ba ko da ya ke yana da hikima wajen ba da labaru, muryarsa ko kare ba ya ci ba wajen waƙa. Ko da ya fara sai tsuntsaye da kajin gidan suka yi ta kansu, suna tsammani korarsu a ke yi. Gogan naka kuwa sai karkata kai ya ke yi wai shi mai daɗin murya, yana cewa:

Ya Allah, ka yi mana gafara,
  Ka tsare mu ga sharrin tasari!
Domin alfarmar Annabi,
  Da sahabbai kai mana agaji!
Mun kama ƙafa da Muhammadu,
  Da Halilu, da Isa adali.
Kome muka ce kan kuskure,
  Mun tuba gare ka, Maɗaukaki.
Karya, zunɗe, gulma, raɗa,
  Aikin ke nan sai tallahi.
In ka ɗebe gare ka, Ubangiji,
  Ba mai baiwa sai izgili.
Mun nutse kan saɓo, ba mu ji,
  Taimako na hannun Dahiri!

Sarkin Sirika ya fashe da dariya, ya ce, "A'a, ashe har ka iya waƙa! Wannan murya taka ba abin da ya fi ta daɗi."

Waziri Aku na tsammani da gaske ya ke yi, sai ya tuma, ya ce, "Ai wannan cikin gaggawa ne na yi ta. Kuma da na san waƙata na buɗe ku, ai da na riƙa ƙare labaruna da ita!"

Sarkin Sirika ya ce, "Ni dai labarin mutanen nan ya fi shero ni da kome."

Waziri Aku ya ce, "Don ma na ƙetare maka labarin waɗansu 'yan kama da suka tarad da Filanin nan sun taru maƙil a masallacinsu, sa'ad da na ce muku an kai gawar Ja'iru can za a rufe."

Sarkin Sirika ya ce, "Me ya sa ka ƙetare shi? Don Allah ci gaba mu ji."

Waziri Aku ya ce. "A dai bari sai gobe, Allah ya ba ka nasara, ga shi la'asar ta yi, a je a ba da farali."

Sarkin Sirika ya ce, "Gaskiyarka, amma gobe in Allah ya so daga kansa za a fara." Mutane suka watse ana ta mamaki.

Kashegari, yau, ko da azahar ta yi Sarkin Sirika ya fara zuwa, sa'an nan aka aika Sarki Abdurrahman ya fito. Sauran 'yan Sarakunan gari kuma nan da nan suka cika ƙofar fada.

Sarkin Sirika ya dubi Waziri Aku, ya ce, "Kai za ka fara, ka ƴar mana da labarin Sama Jannati."

Waziri ya ce, "Allah ya ba ka nasara." Ya gyara, ya shiga aikinsa.

# Labarin Waɗansu 'Yan Kama Da 'Yan Sama Jannati

To, na gaya maka Filanin nan sun taru a masallacinsu sa'ad da aka kai gawar Ja'iru can za a rufe, kowa na ƙoƙarin ya taɓa shi wai ya sami albarka, yadda Liman ya sa aka yi yekuwa. Makafi da guragu da marasa lafiya suna ta zuwa don su taɓa jikinsa wai ko albarkacinsa ya sa su warke.

Mutanen garin nan suna cikin wannan hidima sai ga waɗansu 'yan kama su uku sun iso garin nan. Guda ana ce masa Karɓi, guda Ungo, guda Amshi. Da suka tarad da garin kamar ana wani biki, sai mutane ke ta taruwa a masallaci ana kaiwa ana komowa haja-haja, suka ga wani yaro suka tambaye shi, ya gaya musu abin da a ke yi. Sai suka koma gefe guda suna shawarar yadda za su yi su ga gawan nan, don in sun koma su sami abin ba da labari. Da farko suka rasa yadda za su yi, don mutane sun faye yawa. Daga baya Karɓi ya ce ya san dabara. Sai ya nannarke wai shi ba ya lafiya. Sai suka matsa. Da suka yi kusa Karɓi ya tsaya, da Ungo da Amshi kowa ya kama hammatarsa guda, kamar ba ya lafiya da gaske. Suka tafi da shi suna tarairaya, suna ce wa mutane, "Ku buɗa mana don Allah!"

Ko da mutane suka ga yadda Karɓi ya langaɓe, sai suka ji tausayinsa suka buɗa musu hanya, suka kuma taimake su da gaya wa mutane da ke gaba su ba da hanya, ga wani bawan Allah nan tafe. Suka yi ta ketawa da shi a hannu har suka isa inda Ja'iru ya ke kwance, suka zaunad da Karɓi kusa da shi kamar ba ya iya tashi. Ya miƙa hannunsa kamar da ƙyar ya taɓa jikin Ja'iru, sai ya miƙe wannan hannun da ya taɓa jikin Ja'iru, da shi wai ya warke. Ya sake miƙa hannun guda da ƙyar ya taɓa shi, sai kuma ya alamta wannan hannun kuma ya miƙe. Filani sai kallo su ke yi, abin na ba su sha'awa wai waliyinsu Ja'iru dai ashe ko waliyyi ne da gaske. Ga shi daga Karɓi ya taɓa shi duk hannuwansa sun miƙe. Sai Karɓi ya kwanta ya rungume gawar Ja'iru, jim kaɗan ya yi wuf ya tashi ya yi tsalle, wai ya warke. Da Filani suka ga haka suka yi ƙuwwa gaba ɗaya, suka yi guɗa wai Ja'iru ya zama waliyyi tabbas.



Ashe akwai wani ɗam bojuwa wanda ya san Karɓi tun Kano ɗan kama ne, don ko a birni su a ke shayi kan ja'irci. Da farkon shigowarsu ɗam bojuwan nan bai gane shi ba, don mammalƙwashewar da ya yi da gangan wa shi Inna ta shanye shi. Amma sa'ad da ya ce wai ya warke har ya miƙe tsaye sai ya gane shi. Abin ya ba shi mamaki, bai san sa'ad da ya bushe da dariya ba. Ya yi salati, ya ce, "Ho ɗan nema, Karɓi akwai ja'irin ɗan kama! Duk wanda ya ga sa'ad da ya shigo nan sai ya rantse da Allah ba ya lafiya ne kuwa da gaske."

Wani Bafillace da ke kusa da ya ji wannan batu sai ya dubi ɗam bojuwan nan, ya ce, "A'a! Da ba da ciwo ya zo nan ba, yanzu ne ya warke?"

Ɗam bojuwa ya ce, "Da ciwon wa? Garau ya ke, yadda kowa ya ke nan. Ku ne nan ba ku san shi ba. Ko a Birnin Kano ɗan kama ne. Sunansa Karɓi. Waɗanda suka kawo shi kuwa gudan sunansa Ungo, guda kuwa Amshi. Haka su kan yi ta yawo kasuwar Kano, da sun ji wani ya kira ɗan'uwansa zai ba shi wani abu, in ya ce, 'Amshi,' ko 'Karɓi,' ko 'Ungo,' sai wanda ya ji an ambaci sunansa cikinsu ya yiwo zumbur ya fito ya ce, 'Ga ni!' Ka

da ka ambaci sunan nan nasa ba ku rabuwa sai ka ba shi kwabo ko sisin kwabo."

Ko da Bafillacen nan ya ji haka sai ya yi kuwwa, ya gaya wa sauran abin da Karɓi ke ciki. Da suka ji haka suka ga watau yana wa waliyyinsu shakiyanci ke nan, sai suka aukam masa da duka kamar ba za su bar shi ba. Ya yi ta kuwwa yana cewa, "Na tuba, na bi Allah, na bi ku! In kuna ƙaunar Allah ku ji ƙaina!" Af, duk a banza, sai ma waɗansu mutane ke kawo gudummuwa da kulake.

Da Ungo da Amshi da suka ga haka suka rasa yadda za su yi. Su ba damar su fito fili taimakonsa a gama da su, su kuwa su gudu su bar shi sun yi abin faɗi. Da ɗa kuwa ya yi abin faɗi, gwamma ya yi abin da zai halaka shi. Sai Amshi ya ruga wajen Liman, don shi ne mai gari, yana kukan ƙarya yana cewa, "Allah ya ba ka sa'a, taimakan ni! Wancan mutumin da a ke bugu ɗan sane ne, yanzu-yanzu ya yanke mini kuɗi fam biyar a aljihu da na zo sayen shanu."

Da Liman ya ji haka sai ya ce, "Ana wata ga wata, ana kuɗin ƙasa gari ya watse! Ina ladan? Je maza ka watsa mutanen nan, ka zo mini da ɗan sanen." Ladan ya ruga ya nufi can. Da mutane suka gan shi suka watse, ya zo da Karɓi.

Da Filanin nan suka ji ashe ma Karɓi ɗan sane ne, suka ga ba su ƙare morewa ba, ga shi an raba su, sai waɗansu suka bi, wani daga cikinsu ya ce shi ma an yanke masa fam biyu jiya, wani ya ce shi ma an yanke masa sule goma. Suka dai yi ta sharara ta nan, don wai su sami dalilin da za su sa a ɗaure Karɓi.

Sa'ad da Liman ya ji haka sai ya tabi Ƙarɓi in ya san wannan magana. Karɓi ya tsaya allambaran shi bai taɓa sane ba. Su ladan da suka ga yana mutsu-mutsun bai taɓa satar kayan kowa ba, sai suka shiga zuga Liman ya sa samari su tambaye shi. To, da ma ka san an ce ba a mugun Sarki sai mugun bafade. Liman ya yarda da jawabinsu, ya sa samari suka yi ta tsala masa fatar dorina yana ihu.

Can da Amshi ya ga dabararsa ta ƙi fita, an yi gudun gara an faɗa zago, sai duk al'amarin duniya ya taru ya caɓe masa. Shi ba abin ya ce ƙarya ya ke ba, Liman ya ce ya yi masa shakiyanci ya sa a gama da shi. Ga shi kuma in ya ƙyale, ɗaure Karbi Liman zai sa a yi.

Ungo na gefe guda, shi kuma ya kasa zaune ya kasa tsaye don tausayi. Sai wata dabara ta faɗo masa, ya ruga yana matse-matsen hawayen ƙarya, ya nufi gidan da Hakimin ƙasa ya sauka, don da ma ya zo nan yana kallon jana'izar Ja'iru. Ya yi gaisuwa, ya ce, "Allah ya ba ka nasara, ga wani ɗan fashi can wai shi

Karɓi, shekaranjiya ya tare ni a daji da zan shigo garin nan, muna tafe da ni da wani ƙanena, ya kashe ƙanen nawa ya kwashe kayan da muka zo da su muka sayar nan, ya gudu. Na biyo shi, yau na iso, ga shi na tarad da shi ya yi sane kuma, yana can zauren Liman ana shari'a da shi a kan haka."

Da Hakimin ya ji, nan da nan sai ya ta da wani, aka je zauren Liman aka gaya masa abin da Karɓi ke ciki duka. Liman ya riƙe baki, ya ce, "Yau fa tana ƙasa tana dabo, an ƙidaya kuɗi ga mai su ya taho!" Sai ya sa dogarai suka cafe shi, sauran masu da'awar ya yankam musu kuɗi kuma, har da Amshi, duk suka ɗunguma suka bi zuwa masaukin Hakimin nan.

Da suka isa, Hakimin ma bai ko koma ta kan masu da'awar an yankam musu kuɗi ba, don in ana ta kai ba a ta kaya. Sai ya juya wajen Ungo ya ce ya sake faɗin abin da ya gudana tsakaninsu da Karɓi. Ya gyara zama, ya sake faɗin abin da ya gaya wa Hakimin nan da farko.

Mutane da ke biye kuma da suka ji haka sai suka ce, "Allah ya kyauta maka, ba shakka wannan shi ne Da'u Fataken Dare." Wani ya ce, "Af, in ko shi ne Da'u, ashe Allah ya ɗaukake ka, shi ne ya kashe mini ƙanwa." Wani kuma ya ce, "In haka ne ai ni ma shi ya kashe wana." Kowa kuma ya shiga takalo abubuwan da a aka taɓa yi masa fashi kansu, da waɗanda 'yam fashi suka taɓa kashewa cikin 'yan'uwansa, don dai su samu a kashe Karɓi. Waɗansu ma har ɓarnar da iyayensu suka ba su labarin an yi musu ta tun cikin lokacin Jihadi, duk suka yi ta kawowa suna mallaƙawa a kan Karɓi.

Da Hakimin nan ya ji haka sai ya ce, "To, na ji abin da kuka ce duka, amma abin da ya fi yanzu sai kowa ya tsaya a zo ɗai ɗai mu ji abubuwan da ya ƙwata, da mutanen da ya halakar duk mu ji su, magatakarda ya tsara su kaf, sa'an nan mu bincike shi mu gani in ma sami waɗansu abu daga ciki, mu rage wa waɗanda ke ƙararsa kan dukiya. Waɗanda ko ke bin jinayen 'yan'uwansu mu aika da su birni gun Sarki, kowa ya huta. Wanda ya kashe wani fa akwai abin da za a yi masa ban da kisa? Ya dubi Ungo da Amshi, ya ce, "Ku ne kuka fara ƙara, ba sai ku fara lissafa mana abubuwan da ya ƙwace muku ba sa'ad da ya kashe muku 'yan'uwa? Sa'an nan mu koma ga 'yan gari."

Suka yi shiru, suka rasa abin da za su ce su kuɓutad da ɗan'uwansu, ga shi Ungo ya jawo shi daga ramin kunama ya jefa shi a na maciji. Can sai Ungo ya naƙalci wani abu ya ce, "Allah ya kyauta maka, sa'ad da ya tsare mu da ni da ɗan'uwana, bayan ya kashe shi yadda na gaya maka sai ya ƙwace mini wata jaka da ke aljihuna. Jakan nan kuwa na rantse har da alkawarin da ke

tsakanin hura da nono akwai kwabbaina metan ciki, da gwangwanin sigari ashirin da biyar, da riguna hamsin, da wanduna tara, da hula ɗaya ta dara. Ka ji iyakar abin da ya ƙwatar mini ke nan. Allah ya kiyashe ka da sharrin kaji!"

Hakimin da ya ji maganar ba kai ba gindi, ya dubi Ungo ya ce, "Duk waɗannan cikin aljihunka su ke?"

Ungo ya ce, "Ciki su ke, a aljihun 'yar cikina. Ka san ai wargi wuri ya kan yi."

Hakimin ya dubi magatakarda, ya ce, "Ka rubuta waɗannan duka?"

Magatakarda ya ce, "I, na rubuta hakanan, Allah ya ba ka nasara."

Hakimin ya juya ga Amshi, ya ce, "Kai kuma me ya yanke maka cikin aljihu?"

Amshi ya ce, "Allah ya tsarshe ka da sharrin damana, wata 'yar jaka gare ni cikin aljihu da kuɗi tsaba sule ɗari, da tufafi, da alkyabbu, da ɓera, da kare, da kyanwa biyar, da wani ɗan jirgin ƙasa, da wata makaranta ta elementare a ciki, da yara uku, Barau da Malami da Ɗalha Mashi. Ko su ka tambaya sa gaya maka abin nan da na faɗi gaskiya ne."

Ungo ya amshe ya ce, "Allah ya yi maka tsari da sharrin cin wake ba ruwa. Jaka biyu ya sace mini fa. Ɗaya wadda na kan sa cikin aljihun babbar rigata, kowa garimmu ya san ni da ita. Ba waɗansu kaya da yawa cikinta, sai fa waɗansu littattafai, da waɗansu 'yan Soja suna yaƙi a ciki, da namun daji, da bakan gizo, da tayukan tsakuwa, da wata kwalabar yasimi, da Dala da Goron Dutse, da Kogin Kwara, da wani ofishin talifi, da babban



malamin ofishin, wanda ya ba ni wuƙaƙe dubu don in yanke kunnen wanda ya ƙaryata abin nan da na faɗi.''

Hakimin da mutanensa duk suka buɗe baki suna tu'ajjabi. Can abin ya miskili Hakimin, ya dubi Ungo da Amshi, ya ce. ''Waɗanne irin mutane ne waɗannan? Kanku lafiya, ko kuwa kun haukace ne?''

Sai su duka uku suka yi wuf suka tashi, suka zaro 'yan gangunansu na 'yan kama suka fara kiɗa. Karɓi na ba da waƙa saura na amsawa. Yana cewa,

> ''Mai ƙasarmu, kar ka yarda da shan tsari,
> Kyaun fura a sa mata-nono,
> Iye ayye dawo.
> Kai Karɓi, nan fa ba a ƙarya,
> Ko babu nagge ma sha nono,
> Iye ayye dawo.
> Kyaun babba duk ya lashe suɗinai,
> Zaƙi yana ga mai suɗe ƙwarya,
> Iye ayye dawo.
> Haba Karɓi, kar ka sa su ƙaranta,
> Su dai su dinga tsamen nama,
> Iye ayye dawo.
> Tsamen dawo yana sa ƙarfi.
> Kowa ta kansa ne dattijo,
> Iye ayye dawo.
> Wannan batunka shi ne dahir,
> Ƙwas sami ci ya komo saƙo,
> Iye ayye dawo.''

Sai suka yi wuf suka faɗi gaba ɗaya suna ƙugi, Wayyo Allah, ciwon yunwa, yunwa ta kama mu! Ba magani kuwa sai wani dunƙulallen abu da a ke sayarwa a kasuwa, ana kiransa ɗan wake. Mai ƙasa ka yi agaji, kada mu mutu zaurenka!''

Da Hakimin nan da mutanensa ko da suka ga haka duk sai suka bushe da dariya. Kowa ya kama gabansa, suna cewa, ''Allah wadai! Ashe da ma duk 'yan kama ne mu ke wahal da kammu kansu a banza.'' Hakimin ya sa aka kawo musu hura suka sha. Ya tambaye su, suka gaya masa yadda abin nan ya faru duka, har mutanen gari suka ba Karɓi kashi. Ya kawo kuɗi ya ba su, ya sallame su.

Da za su tashi Karɓi ya ce wa jama'a, ''Ku karɓi addu'a, mu yi wa mai ƙasarmu roƙo sa'an nan mu tashi.' Sai ya kama irin addu'arsu ta 'yan kama yana cewa, ''Ya Allah ka kiyashe mu

daga sharrin mace mai riga mijinta tsame nama. Kada Allah ya gama mu da namiji mai kunyar suɗin tunkunya. Allah ya tsare mu da mugun ji da mugun gani. Mugun ji dai kana zaure ka ji an ce kaza ta zubar maka da fura. Mugun gani kuwa a sa sanwar tuwo gidanka, a fara talge, tukunya ta fashe. Allah ka sa mu mutu muna rayayyu. Wanda ya sha gara har ta zama ita ce ajalinsa, wannan shi ya cika yana da rai, amma wanda yunwa ta kashe, wannan shi ya mutu yana matacce. Allah ya kiyashe mu da irin wannan mutuwa! Fatiha, amin."

Mutane suka ɗauki tafi raf raf raf don murna. Sarkin Sirika ya ɗauko fam hamsin ya ba Waziri Aku don daɗin labarin nan da ya bayar. Ko yaushe ya dubi Waziri Aku ya tuna da wannan labari sai ya fashe da dariya shi kaɗai.

Da aka natsa, Sarki Abdurrahman ya dubi Hazik, ya ce, "Kai kuma ba mu irin naka mu sha."

Hazik ya gyara murya ya fara, "Labarin Sarkin Farisa da wani Bahindi."

Waziri Aku ya yi murmushi ya ce, "Bahindi mai dokin ice ko?"

Hazik ya ce, "Ka ga fa abin da ba na so mutum zai fara ba da labarinsa a kwaɓe shi. In kai ka san shi, sauran mutanen da ke nan sun san shi ne?"

Sarki Abdurrahman ya ce, "I, gaskiyarka fa."

Waziri Aku ya ce, "To, duk labarin da ya ke bayarwa na san su, abin da ke hana ni magana kawai ke nan."

Hazik bai dai ce kome ba. Zai ci gaba da labarinsa, sai Waziri Aku ya ce, "Tsaya, tsaya! Ina jin ziza-ziza kamar ta motar Sarkin Sirika." Aka yi tsit ana saurare, ba wanda ya ji motsin kome. Sai Sarki Abdurrahman ya ce, "Haba ci gaba Hazik, iska ce Waziri ya ji, ka san ya fara tsufa.

Waziri ya ce, "Yanzu ku ba ku ji zizar mota ba? Wannan, lalle ba ta zama iska, ku dakata dai mu ji." Aka yi shiru sai can aka ji zii. Waziri ya ce, "Haba, da ma na gaya muku."

Jim kaɗan ta iso. Mai mota ya sauka ya shiga, ya yi gaisuwa, ya ce wa Sarkin Sirika, "Allah ya ba ka nasara, na rantse har da rawaninka al'amarin Wazirin nan sai a kyale. Ai ina kaiwa gida, can zuwa faɗuwar rana na tara katta, muka tasa Sanda ɗan Sarkin Zagi gaba, ya yi ta yawo mu ko muna biye kamar sakarkaru, wata sa'a ya bi hanya da mu, wata sa'a kuwa in ya hangi yara na wasa ya nufa da mu can. Ya dai yi ta sangartad da mu tun abin la'asar har zuwa rana faɗuwa, sai ga mu har unguwar marina. Yana zuwa kofar wani gida sai ya tsaya, yana ta

kuka, wai shi sai a ɗauke shi, ya gaji. Da ganin haka sai na sa aka kewaye gidan, waɗansu suka kutsa kai ciki. Mu da ke waje sai muka ji na ciki na cewa, "Ku kawo mana gudummuwa!" Waɗansu daga cikimmu suka faɗa. In dai gajarce maka labari, aka kama ƙatta goma sha ɗaya cikin gidan nan suna tare, suna caca. Ashe su goma sha biyu ne, gudan kuwa da ya ga an rutsa su ashe ya sulale, ya nufi wajen masai ya taka ya haura, sai waɗanda muka bari can maƙe daga baya suka buge suka ɗaure, yanzu su duka goma sha biyu suna nan an sa kurkuku. Kaya kuwa, abin da muka ƙidaya jakar Sarki ɗari da hamsin da bakwai. Sun zuba cikin wata tsohuwar rijiya, sun cike da ƙasa. Mun tambaye su abin da suka taɓa, suka ce ban da sule goma sha biyu ba su taɓa kome ba ciki."

Sarki Abdurrahman ya ce, "Alhamdu lillahi! Mutanen nan kuwa na ƙasar ne?"

Waziri Aku ya karɓe, "A'a, ai Sarkin Sarai ya aiko da su su yi haka."

Mutane suka dubi Waziri, mai motan nan ya ce, "Wallahi gaskiyarsa, mu ma da Wakili ya sa aka lallasa su, hakanan suka ce mana."

Mutane suka dubi Waziri Aku, aka yi tafi gaba ɗaya, "Alo, alo Wazirin Wazirai!" Sarkin Sirika ya ɗauki Waziri Aku ya sa a ƙafarsa, ya rasa ma ta cewa don murna da mamaki.

Sarki Abdurrahman ya dubi Sarkin Sirika, ya ce "Ka ga aikin Waziri ko? Kaɗan ke nan ka fara gani a cikin al'amuransa. Sai ka yi shiri ka koma gida yanzu, a san yadda aka yi da waɗannan tukun, don hankali ya kwanta."

Sarkin Sirika ya ce, "Ai hankali ya gama kwantawa tun da aka kama su aka kuma ga kuɗin. Bari Haziƙ ya ƙare wannan labari da ya fara, sa'an nan mu san abin da mu ke ciki."

Sarki Abdurrahman ya ce, "Hakanan ne. Haziƙ, ci gaba da labarin Sarkin Farisa da ka fara."

Haziƙ ya ce, "To."

# Labarin Sarkin Farisa Da Wani Bahindi

Wata rana wani Sarki na Farisa ya tafi **cikin** lambunsa shan iska, sai wani Bahindi ya zo masa yana ɗauke **da** wani dokin ice wanda ya sassaƙa da hannunsa. Ya durƙusa ya yi gaisuwa, dogarawa suka ce, "Sarki ya gaishe ka."

Bahindi ya ce, "Ranka ya daɗe, tun daga Hindu na kawo maka tallar wannan doki."

Sarki ya ce, "Ka ko sha wahalar kaya a banza, ni dai ba na muradinsa, don ko masassaƙan ƙasata sa iya sassaƙa mini wanda ma ya fi wannan armashi, in na yi bukata. Da ya ke dai ka wahala, dakata mu koma gida in sallame ka."

Bahindi ya sake durƙusawa, ya ce, "Allah ya ɗaukake ka, ai kama da Wane ba Wane ba ne. Yadda ka faɗi dai gaskiya ne, masassaƙan ƙasan nan sa iya sassaƙa dokin icen da ya fi wannan kyau a fuska, amma duk da haka, Sarki, ya yi mini gafara, ko an kwaikwayi waƙar Wance gun rawar a ɓata. Wannan dokin na sihiri ne, yanzu in na hau shi duk ko wace ƙasa na ce ya kai ni, sai ka ga ya tashi kamar tsuntsu ya nufi da ni can."

Sarki ya dubi Waziri, ya ce, "Da jin abin da ke yiwuwa ai an sani. Kai Waziri, ko a hankalin kanka abin nan da ya faɗi ya shige ka?"

Waziri ya ce, "Ko da fari, Allah ya ba ka nasara. Amma tun da ya ke haka, ya gwada mu gani, ai daɗai ta malam ba ta wuce amin ba."

Sarki ya dubi Bahindi, ya ce, "Bismilla." Sai Bahindi ya ɗare doki, ko da ya taɓa wani abu sai ga shi yana tashi kamar jirgin sama, amma shi ba ya damuwar mutane da ƙara. Da ya gaji da yawo ya sauko.

Sarki ya ce, "I, lalle abin da ka taɗi ba ƙage. Amma, to, nawa za ka sayar mini da shi?"

Bahindi ya ce, "Allah ya ɗaukake ka, in dai kana kan sonsa da gaskiya, to, ni ba zan sayar da shi ba don kuɗi, ko fam nawa ne."

Sarki ya ce, "Af, tun da ka san sha'anin haka ya ke, me ya sa ka kawo mana gari ya gari? Ka ko san an ce, 'Ba na sayarwa ba ne, ya gagari Kundila."

Bahindi ya ce, "Na sayarwa ne fa, da ba na jin sayarwa na kawo maka? Amma dai ba na kuɗi ba ne. In kana so sai ka aurar mini da 'yarka maimakonsa."

Ɗan Sarki ya harari Bahindi ya ce, "Yau ga mutumin banza, a aura maka 'yar Sarki don wannan ice?"

Bahindi ya ce, "Daudu, ba ka san daɗin dokin nan ba ne, hau shi ka ɗanɗana ka ji, in kana so."

Ɗan Sarki ya ce, "To," Sarki dai na kallonsu, kamar an rufe masa baki. Yaro ya hau, ya taɓa ƙusar da ke sa shi tashi, doki ya yi sama da shi. Tun ana ganinsu har suka ɓace. Can ɗan Sarki ya yi shawarar ya komo, ya taɓa wata ƙusa sai ya ga dokin ya ƙara yin sama da sauri. Ya firgita ya sake taɓa wata, doki kuma ya ƙara sauri kamar iska. Sai ɗan Sarki ya yi salati, ashe ya manta ya tambayi Bahindi inda za a taɓa dokin ya sauka. Suka yi ta tafiya ɗan Sarki na bin ƙusoshi dabam dabam yana taɓawa, har Allah ya sa ya yi dace. Sai ya ga doki ya rage sauri, ya yiwo ƙasa ƙasa. Ɗan Sarki ya yi shukura da ya kubuta.

Ga shi cikin dare, bai san inda zai faɗa ba, ko a ruwa, ko a daji, ko a ƙaya. Duk da haka bai kula ba, shi dai ba burin da ya ke yi illa ya ji ya taka ƙasa. Yana cikin sauka sai ya ji ya sauka bisa wani abu kamar rufin gida. Ashe ba kama ba ce, bisa rufin gidan Sarkin Bangol ya sauka. Ya nemi hanyar da zai gangara ya rasa Sai ya kwanta nan.

Da gari ya waye sai Sarki ya ga mutum bisa rufin soronsa. Ga shi tsamo-tsamo cikin gida, Sarki ya yi tsammani mahaukaci ne, ya ga ko mahaukacin ne ba ta inda zai bi ya hau. Ya sa bayi su tambaye shi wane ne shi, suka tambaye shi, ya ce su tsaya ya sauko, ya hawo dokinsa ya taso kamar tsuntsu sai ƙasa. Ya gane abin da a ke kamawa a tashi, da wanda a ke kamawa a sauka.

Ya fara tambayar abinci aka ba shi ya ci, sa'an nan ya kwashe labarinsa duka ya gaya wa Sarki. Sarki ya yi al'ajabi. Ya zauna nan garin kwana kamar bakwai. Sai 'yar Sarki ta tsaya ita ban da ɗan Sarkin nan ba ta auren wani. Ta rantse in an ƙi yarda ta aure shi ita ko ba ta aure har abada. Ka ji labarin ɗan Sarkin da dokin ice.

Amma Sarkin Farisa da ya ga ɗansa ya tafi bai dawo ba sai ya ce a ɗaure Bahindi. Aka cafe shi aka gama shi da fursuna, ya yi ta aikin wahala.

Sarki ya ce, "In ɗana bai dawo ba bayan wata guda zan sa a yanka ka. Da ma in ka bi sawun al'amarin ka tarar gama kai aka yi da-kai, don ka zo ka raba ni da ɗan ɗana."

Ana nan bayan kamar ƙwana bakwai, yadda na gaya maka, yarinya dai ta kangare sai shi za ta aura. Sarki ya ce mata, "To,

na yarda, amma sai da ke da babban bawana ku bi shi, ku gani in gaskiya ya ke yi shi ɗan Sarkin Farisa ne. Sa'an nan ku dawo, mu yi shawara da ni da ubansa a yi aure.

Ya kira bawan kuma dabam, ya ce masa ya lura da abin da ɗan Sarkin nan ke ciki duka. Ya tafi da takobi, in ya ga ƙarya ya ke yi, so dai ya ke ya sace Zuhairatu, ya kashe shi ya dawo masa da 'yarsa. Suka sallami Sarki, suka hau dokin iccen.

Ɗan Sarki ya taɓa ƙusa, bawan nan na lura, doki ya shiga aikinsa. Suna nan suna ta yi, har can zuwa rana tsaka Allah ya sa suka isa Birnin Farisa. Ɗan Sarki ya tasar wa lambu, watau inda ya hawo shi, ya sauka ciki, ya shimfiɗa wa 'yar Sarki kilisai a wani ɗaki nan lambun, ta kame bisa. Shi ko ya ce za shi ya gaya wa Sarki, don a sawo mutane su zo a shiga da ita a kambame.

Ashe cikin lambun nan akwai 'yan jarun suna aiki, har Bahindin nan na cikinsu. Yana lura da abin da ɗan Sarkin ya yi, amma saura na can cikin ganyaye ba su san ma ya zo ba. Da Bahindi ya ga ya wuce, sai ya laɓaɓo ya rabu da dogarawa, suna can sake da baki ba su sani ba. Ya sami wata farar riga ta wani dogari, ya sace ya sa. Ya zo inda Zuhairatu ke zaune na jira a zo a tafi da ita. Ya durƙusa, ya ce, "Allah ya ba ki nasara."

Bawan nan na tsaye bisa kanta da takobi, ko ƙuda ba ya bari ya taɓa ta. Ya ce, "'Yar mai duniya ta gaishe ka."

Bahindi ya ce, "An ce, in kin yarda, in zo in shiga da ke gari."

Bawan nan ya ce, "Duk garin nan a rasa wani mutumin kirki da za a aiko ya je da ita, sai kai yaro-yaro haka, ba ko wando, kai ba hula? Haka sarautar taku ta ke da ku ke ba da labarinta? Allah ko wadan wannan irin sarauta taku!"

Bahindi ya ce, "Ai mutane na can sun cika ƙofar fada inda za ta sauka. Ni bawa ne, to, ina ruwana da ado? Abin da ya sa ko aka aiko ni, don ni kaɗai na san yadda a ke tafiya da wannan dokin icen. Sarki ya ce in zo in kai ta a bisa don ya fi raƙumi daɗin hawa, ga kuma sauri."

Bawa ya yi tsaki, mts. Zuhairatu ta tashi ta haye. Kafin bawan nan ya naɗo tabarmin da ta ke zaune ya zo shi kuma ya hau, sai ya ga doki ya yi sama ya tafi. Bawa ya yi salati, ya rasa inda zai sa kansa, ya ce, "Allah wadan zaɓen da Sarki ya yi mini. Ga shi ina gani an yaudare ni. To, ni yanzu in koma Bangol in ce wa Sarki me? Kome dai na gaya masa na san ba abin da ke hana ya yanka ni." Yana nan yana jifan doki da dutse a banza, yana ihu kamar mahaukaci, sai ga mutane ɗakaka, an zo ɗaukar amarya.

Da aka tarar da abin da ya faru, sai suka koma, masoyan Sarki na baƙin ciki, maƙiyansa kuwa na dariya a ciki. Sarki ya sa aka ɗaure dogaran nan da suka yi sakarci har Bahindi ya gudu. Ɗan

Sarki da bawan nan suka ce su duk inda ta tafi nan duniya sai sun samo ta, sai fa su mutu garin nema. Suka yi shiri suka rangaɗa. Ka ji inda waɗannan tasu ta kwashe.

Amma Bahindi ya sakar wa doki iyakar saurinsa, ya yi ta tafiya, wuce wannan gari, ƙetare wannan rafi, zarce wannan dutse, tun safe har la'asar. Da la'asar ta yi ya kai Birnin Kashmir. Ya sauka daga bayan gari, ya shiga ya sayo musu abinci. Zuhairatu na nan zaune bisa doki, sai ga waɗansu masu dawaki su kamar ashirin suna kilisa. Ko da ta gan su sai ta ce, "Bayin Allah, ku wa Allah, ku wa Annabi, ku taimake ni! Mutumin da ya zo da ni nan sato ni ya yi. Ni 'yar Sarkin Bangol ce."

Ashe abin ya zo kan kari, masu dawakin nan Sarki ne da mutanensa ya ke shan iska. Da ya ji haka sai ya ce mata ta ƙyale, shi ko ya sauka ya zauna. Can sai ga Bahindi ya dawo da ɗan ƙosai da tsire da waina. Da isowarsa Sarki ya ce, "Ina ka gangamo da wannan yarinya?"

Bahindi ya ce, "Ina na gangamo da ita? Mutum da matarsa a yi masa wannan irin tambaya?"

Zuhairatu ta ce, "Wallahi ni ba mijina ba ne, sato ni ya yi." Ta kwashe labarinta ta sake faɗi. Sai suka ga Bahindi ya zabura zai haye doki. Zuhairatu ta ce, "Zai tashi, zai tashi, ku yi agaji!"

Sarki ya dubi dogarawa, ya ce, "Ku yi da shi!" Kafin ya kai ga zama bisa dokin sai ga kansa a ƙasa, haƙora na cizon ƙasa. Sarki ya sa aka tafi da Zuhairatu gidansa, ya sa kuma aka ɗauki dokin icen a ka, aka tafi da shi gari. Duk ba wanda ya san amfaninsa. Aka sa a taska aka kulle.

Da aka natsa, ya sa a yi yekuwa a gaya wa mutane zai auri Zuhairatu 'yar Sarkin Bavol. Da yarinya ta ji haka sai ta yi ta kuka, ta ce a ranta, "Da ina tsammani Sarkin Kashmir mutumin ƙirki ne, zai mai da ni gida, ashe ba haka ba ne. Yanzu ko in na ce ba na sonsa lalle kashe ni zai yi. Abin da ya fi sai in ce na yarda, amma ba na lafiya yanzu, sai na samu sauƙi a yi biki." Saboda haka ta kira Sarki ta gaya masa ta langaɓe kamar ba ta da lafiya. Ta warke yau ta warke gobe, ciwo sai ya yi ta yin gaba-gaba. Sarki ya aike ƙasashe a nemo masa magani, suka yi ta zuwa suna ɗirka mata sayu da ganyaye da kauci, duk a banza. Ka ji labarin waɗannan.

Amma ɗan Sarkin Farisa yana nan suna tafiya, suna ta tambayar labari, babu, sai ran nan suka ji waɗansu fatake na cewa, "Kai, ai ko watan jiya an kawo wani irin doki na ice a Kashmir mai ban mamaki, har da wata 'yar Sarki a bisa."

Can Sarki ya matsa, ya ce, "Ina aka gan su, ko aljannu ne?"

Falke ya ce, "Aljannu fa ina? 'Yar Sarkin Bangol ce wani

Bahindi mai sihiri ya sato ya ɗauko bisa doki. Dokin ma tashi ya ke kamar tsuntsu."

Ɗan Sarki ya ce, "Ba dokin ice ba ke nan, ce mini dokin aljannu. To, ina Bahindi?"

Falke ya ce, "Af; tun ran da suka zo Sarki ya sa aka kashe shi. Shi ko yana nan zai auri 'yar Sarkin, amma ba ta lafiya, wai ko sai ta warke za a yi auren."

Ɗan Sarki ya ce, "Ina sunan 'yar Sarkin?"

Falke ya ce, 'A'aha! Yau Allah ya gama ni da mutum da ťambayar, 'Yaya aka yi aka haife ka'. In so ka ke ka ƙure ni, je ka, ƙarya na ke yi "

Ko da ɗan Sarki da bawan nan suka ji haka, sai zuciyoyinsu suka koma kamar takarda, suka shiga cin zango suka tasar wa Kashmir, kwance tashi har Allah ya kai su. Ɗan Sarki ya sami wani kwando ya cika da ganyaye da kaucoci da sayu, ya ba bawan nan ya ɗauko. Suka isa wurin Sarki. Bayan sun yi gaisuwa ya ce shi boka ne, ya jiwo labarin ana neman masu magani, shi ya sa ya taho.

Sarki ya ce, "Irinku ko mu ke nema." Ya sa aka kai shi inda Zuhairatu ke jiyyar ƙarya. Ko da ta gan shi sai ta yi kamar ta ce yaya don murna. Ta dai kanne, kada a gane. Ɗan Sarki ya ɗebi waɗansu sayu ya ba ta ta sha, sai ta yi wuf to miƙe tsaye. Aka je aka gaya wa Sarki Zuhairatu ta warke. Ɗan Sarki ya ɗebi waɗansu ganyaye, shi ma bai san ko na mene ne ba, ya sa ta yi turare.

Da Sarki ya zo ya ga Zuhairatu ta warke, sai ya yi kamar ya ɗauki ɗan Sarkin nan don murna. Ya tambaye shi ƙasar da ya fito. Ɗan Sarki ya ce daga Sudan. Ka ji ƙarya ba? Ya ce kuma wai shi ne Sarkin Bokayen mutanen Sudan, aljannu suka gaya masa ya zo nan ya yi taimako, kada ta halaka. Aka kai shi masauki, ya sauka.

Da gari ya waye ɗan Sarki ya ce, "Jiya uwargijiyata da na yiwa magani ta gaya mini yadda ciwon ya same ta, da yadda Bahindi ya kawo ta nan. Da ta gaya mini na san ba kome ba ne, iskoki ne, ba su rabu da ita ba tukun har yanzu, don za su rika bugunta wata wata, sai fa in an ƙara ƙoƙari. Abin da ya fi yanzu sai a fid da ita da dokin icen nan a kai su can inda aka fara tarshe su, in yi musu turare gaba ɗaya, in yi wa wurin turare kuma. Im ba haka aka yi ba, ba ta rabuwa da aljannun nan gaba ɗaya. In ko ka ga don su buge ta wata wata ba kome, to, shi ke nan na huta.

Sarki ya ce, "A'a! Ba kome fa ina? Ai gwamma kome za a yi a yi shi a gama tun kana nan, ina za mu yarda mu sake ka ka bar mu da jagade-jagade daga bisani?" Sarki ya sa aka kai dokin ice can.

Aka sa ƙakumi kuma ya ɗauki Zuhairatu bayan ta kwashe duk 'yan abubuwan da su ke na halalinta, ta ɓoye bisa raƙumi. Aka kai ta filin nan aka ajiye.

Ɗan Sarki ya ce mutane su tsaya daga nesa kaɗan, shi kuwa ya sa aka kai dokin ice kamar yadi ashirin daga mutane aka ajiye. Ya sa aka hura wuta kusa da dokin, ya ce wa Zuhairatu ta hau dokin, ta haye. Shi ko ya ɗauki sanhon maganin nan ya jefa cikin wuta, mutane na kallonsa. Sai ya yi farat ya ɗare doki, bawansa kuma ya kama kuturi, ya lalabi ƙusar tashi, suka yi sama.

Sarki ya dubi mutanensa, ya buga musu tsawa ya ce, "Kada su kai!" Mutanen suka yi ta ɗaukan duwatsu suna jifarsu. Af! Ko kusa da su akwai dutsen da ya kai? Na gaba ya yi gaba ko, na baya sai tsintar hula. Yana ta. . . ."

Waziri Aku ya katse masa hanzari ya ce, "Ina za ka? Ai labarin ya ƙare ke nan."

Haziƙ ya ce, "Ni yadda na ji bai ƙare ba tukun, zan bayyana yadda ya aure ta."

Mutane suka ce, "Gaskiya fa ne Haziƙ, ina za a ce labari ya ƙare a nan, ai ko kusa."

Waziri Aku ya ce wa Haziƙ, "Labari ne kawai ka ke bayarwa, ba tarihi ba. To, mene ne na damuwa da faɗin wani abin da ya kamata ya faru? Mutane ba su san inda ya kamata labari ya ƙare ba, sai su yi ta zuba su kawai, sai ka ji labari mai daɗi wurin ƙarewa ya yi cikas. Yanzu kana ƙara kalma guda wurin labarin nan ka ɓata daɗinsa."

Alƙalan nan suka ce, "Watau ƙarewar da ya yi nan shi ka ke tsammani zai sa labarin daɗi ko?"

Waziri aku ya ce, "I, in ya bar labarin nan inda na ce ya tsaya, ai in ka ɗebe na Alti da aljani, duk cikin labarun da ya bayar ba wanda ya fi wannan daɗi."

Alƙalan nan suka yi tsaki, "Mts, ka tsai da shi a banza. Tun da mu ke jin labari ko irin na yara na gizo da ƙoƙi, ai ba mu taɓa jin mara daɗi irin wannan ba, in an bar shi a nan. Kare, kare, zo ka ci labari!" Mutane suka watse suna dariya.

Da mutane suka watse Sarkin Sirika ya ɗauki Waziri Aku ya rungume shi, yana neman gafararsa bisa ga wulaƙanta shi da ya yi da fari. Waziri Aku ya durƙusa, ya ce shi ma ya gafarce shi. Sarkin Sirika ya sake duban aku zugum, ya dubi Sarki Abdurrahman, ya ce, "Wannan Waziri naka, da ba ka da ɗa, in ka mutu aka naɗa shi, kowa ya yi jayayya da shi ya isa abin a kashe. Ajiyar Allah yawa gare ta." Ya sake dubam Waziri Aku, ya

ce, "To, yanzu kuma yaya ka gani za a yi da ɓarayin?"

Waziri ya ce, "Sai a bar su nan gidan sarƙa, sai ka koma duk abin da ka ga dama ka yi musu."

Sarkin Sirika ya ce, "Yaya batun Dogon Yaro da ka ce?"

Waziri ya ce, "A'aha! Wane batu? Ashe watau shi ma ba ka kore shi ba? To, in mai motan nan ya koma, a zo da Dogon Yaro a ɗaure, ka ji abin da ya ke ciki da ya sa na ce kada ka saki jiki da shi." Aka sallami mai mota ya koma.

Sarakuna kuma kowa ya koma gida. Mutanen Sirika na ta al'ajibin al'amuran Waziri Aku. Mutanen ƙasar Sarki Abdurrahman in sun ji suna yabon Waziri aku sai su ce, "Haba, me kuka sani daga al'amarin Waziri? Mun dai sani in don shawara a ke yin Waziri, ba don ya shiga gaba ya yi wa mutane salla ba, kome muka ce wa Wazirinmu sai a ƙyale. Don dai waɗannan hardodi duk ba mu shakkar a gwada, da jin labarin ma ai ka san ba na jahili ne ba."

Mutanen Sirika suka riƙa cewa, "M! Ai kome kuka ga dama sai ku ce, labarin Wazirin nan naku mu dai ya nuna mana al'ajab a fili."

Yau da gari ya waye aka sake taruwa a ƙofar fadar Sarki Abdurrahman, sai Sarkin Sirika ya ce wa Waziri, "Da rashin sani shi ya sa muka ce mu zo jayayya, amma yanzu mu mun saki, sai dai kawai a yi labarai don nishaɗi. In ka bayar da ɗaya, Haziƙ ya bayar da ɗaya, har kafin a ƙare kwana ko uku ko huɗu, sa'an nan in tashi."

Waziri ya ce,"To, madalla." Ya dubi Haziƙ, ya ce, "Sai ka fara yadda muka saba yi."

Haziƙ ya ce, "To," Ya fara:

# Labarin Waɗansu Samari Su Uku

Wata rana waɗansu samari su uku suna yawo, sai suka gamu da wani ayari na alhazai za su Makka, su kuwa 'yan samarin nan ko wanne na da ɗan abin hannunsa. Saboda haka da suka ga jerin ayarin nan sai abin ya buɗe su, suka shawarci madugun in ya yarda suna so su shiga ayarinsa zuwa Makka.

'Madugu ya ce, "A'a! Me zai hana, ai da irinku masu niyya waɗannan suka yi yawa, in dai kuna da guzuri isasshe sai mu ɗunguma." Samari suka koma gida suka yi shiri. Bayan kwana biyu suka gama, suka sallami dangi, suka tarad da ayari, suka rankaya.

A kwana a tashi har suka shiga cikin Hamada. Madugun nan ya tara jama'arsa, ya ce, "Kada kowa ya yarda ya tsaya baya tun da muka shigo nan, wanda ya kuskura ya yi 'yar fitar ƙafa, lalle wannan ba shi ba."

Jama'a suka ce, "To, mun ji, Allah dai ya sawwaƙa." Suna nan suna ta tafiya dai, sai ran nan samarin nan uku da ya ke su kwanan nan suka gamu da ayarin, ba su saba da tafiya ba, suka gaji, suka tsaya baya su kaɗai, suka zauna wai don su ɗan saurara su ruga su tarad da ayari. Zaunawarsu ke da wuya ko wanne sai ya ɗan kishingiɗa, kafin a yi haka, barci ya share su. Can suka farka suka duba, sai suka ga ba ayari ba dalilinsa. Suka duba ko sa ga ma hanyar da suka bi, af, iska ta sa rairayi ya rufe wurin. Suka yi salati, suka tasam ma jihar da ayarin suka bi. Suna tafe, can sai suka hangi wani abu na motsi daga nesa. Suka yi tsammanin wani naman daji ne, suka kasada suka tasam masa. Da suka ƙara matsawa sai suka ga ashe mutun ne bisa raƙumi. Da suka gamu sai suka ga ya zare takobi, tsoro ya kama su, suka durƙusa suka ce masa, "Mai gida, barka da kwana." Bai ce musu kanzil ba, sai ya dubi kan samari biyu ya fille, suka yi shahada. Ya sauka ya ajiye takobin bisa sirdinsa, ya kama duba aljihun samarin nan matattu yana kwashe kuɗi.

Da saurayin na uku ya ga haka, ya san lalle shi ma bai tsira ba, sai ya yi wayo ya ɗauki takobinsa, kafin ɗam fashin ya ankara,



saurayin ya ɗauke kansa. Ya kwashe kuɗin da ɗam fashin nan ya ƙwace daga hannunsu, ya kama raƙumi ya haye, da takobin nan a saɓe a kafaɗarsa. Raƙumi ya mike tsaye. Ga shi bisa, bai san inda zai karkata akalar raƙumin ya bi ba. Ayari kuwa ya yi nisa, ga yunwa da ƙishirwa sai cinsa su ke yi. Ya mai da gaba gabas ya ce, "Ni Sufuyanu, yaya zan yi da kaina? Da ma na bari ya kashe ni na huta." Sai ya tuna kuma ya ce, "Af, to, in ni ban san hanya ba, ai raƙumin nan ya san gidansu, bari in bar shi ya kai ni can, kome ta tafasa ta ƙone." Sai ya sakam ma raƙumi akala ya buge shi. Raƙumi ya zabura sakataf, sakataf, sakataf, bai zame ba sai 'Yar unguwar nan da dam fashin ya fito.

Ko da mutanen unguwar suka ga Sufuyanu bisa raƙumin

ɗan'uwansu, sai suka taso masa kamar za su cinye shi ɗanye, suna cewa, "Ga wani Tukururu bisa raƙumin Farisa. Kai yaya ka sami wannan raƙumi? Ina mai shi kuma?"

Sai Sufuyanu ya ce, "Ku ba ni ruwa in sha tukun, sa'an nan in gaya muku labarin ɗan'uwanku." Suka shiga suka kawo masa ruwa ya kora, suka ba shi dabino ya ci, ya ƙoshi. Yana nan dai bisa, bai sauka ba.

Da hankalinsa ya kwanta, ya ce, "Ɗan'uwanku na can wajen ayarimmu, mun ɗaure shi. Dalili kuwa, tasam mana ya yi shi kaɗai, mu kuwa kamar ɗari da sittin, duk ya fatattaka mu, ya yi mana ɓarna mai yawa. Da muka ga in mun watse shi kaɗai zai iya halaka mu, sai muka taru muka yi masa sukuwar salla, muka kama shi, muka ɗaure. Da saura suka ce mu kashe shi mu rama, amma madugummu ya ce tun da ya yi jaruntaka haka a ƙyale shi. Amma ya biya diyyar waɗanda ya kashe cikimmu. Aka yi lissafin kuɗi suka tashi fam tamanin daidai. Madugummu ya ce in kuwa ba ya iya biya, mu kashe shi. Shi kuwa ya ce ya iya, amma sai a zo nan a karɓa. Aka nemi wanda zai zo cikimmu aka rasa, kowa na tsoro kada ya zo ku kashe shi. Da aka rasa mai zuwa ya karɓa, sai madugummu ya cira takobi zai sare shi, sai tausayi ya kama ni, na ce na sai da rai in taho. Na gaya musu in sun ga na kwana uku ban dawo ba sai su yi abin da su ke so da Farisu, ni kun kashe ni ke nan, an yi musaya. To, yanzu sai ku yi shawarar abin da ya fi muku, ko ku kashe ni, Farisu kuma a kashe shi, ko kuwa ku ba ni kuɗin in kai a sako muku ɗan'uwanku."

Da suka ji haka sai suka taru suna shawara. Suka ce, "Lalle maganar Tukururun nan gaskiya ce, don kuwa Sarkin Yawa ya fi Sarkin Karfi. Ba ya yiwuwa kuma mu yi tsammani wannan ɗan sullutun saurayi ya kashe shi."

Wani ɗan tsoho daga cikinsu ya ce, "Ku tambayi saurayin dai ku ji abin da ya sa ya kawo raƙumin, ya kuma ɗauko takobin, kada ku ce ba ya yiwuwa wannan ya kashe Farisu. Ku tuna fa ba kullum rana ta ke Jumma'a ba."

Suka juyo wajen Sufuyanu suka ce, "Kai kuwa, in abin da ka faɗi gaskiya ne, to, me ya sa aka kawo raƙuminsa, ka kuma ɗauko takobinsa? Ba wani raƙumin da za ka hau ne?"

Sufuyanu ya ce, "Af! In da na kawo wani raƙumi ba nasa ba, kome na faɗa muku ai sai ku ce ƙarya ne. Da raƙumin zan hawo in riƙo takobinsa don shaida, ya ce da ya ke ban san hanya ba sai in hawo wannan raƙumin, shi zai nuna mini. Ya ce ya kuma ƙara zama shaida bisa ga abin da zam faɗi."

Da suka ji haka sai suka dai yarda da abin da Sufuyanu ya faɗi duka, suka ɗauko fam tamanin za su ba shi ya tafi, sai ɗan tsohon

nan ya ce, "A'a, a yi haka? Ai sai mutum tara ko goma su hau."

Suka ce, "Gaskiyarka. Sufuyanu, ci gaba. Mu ma kai kuɗin da kammu, don mu yi wa madugun godiya bisa ga wannan alheri da ya yi mana. Wanda ya yi nasiha kamar haka, ai ya kamata a je a gode masa."

Sufuyanu ya ce, "Ai ni yanzu duk na ruɗe ban san inda hanyar ta ke ba. Sai wani daga cikinku ya shiga gaba ya nuna mana hanyar da ayari ke bi zuwa Makka."

Wani ya shiga gaba, suka yi ta zagarabtu. Inda Allah ya tashi kyauta wa Sufuyanu, sai suka faɗo daidai ayarin. Sufuyanu ya ce, "Ku tsaya nan, in je in gaya wa madugu kun zo, don kada su yi tsammanin waɗansu miyagu ne kuma."

Suka ce, "Gaskiyarka." Suka dakata. Sufuyanu ya zabura ya isa wurin madugunsu, ya gaya masa duk abin da ya faru tun daga farko har ƙarshe. Ayari ya tsaya, madugu ya ce wa 'yan'uwan Farisu su zo. Da suka zo ya sa aka kama su su duka, ya ce, "Farisu ya kashe mana mutum biyu. Da za mu ƙyale shi, muka ga dai rai bai fi rai ba. Saboda haka mu kuma muka kashe shi. Ina kuɗin da kuka kawo? Ku ba ni, su ne diyyar sauran mutum guda da ya kashe. Ku kuwa, ko dai ku rantse ba ku sake fashi daga yau, ko kuwa duk in yanka ku ɗai ɗai."

Mutanen nan suka ga dai ba mafita, sai suka rantse ba su sake fashi, suka ce, "Tun da ma aka kashe Farisu, ai ko ba mu rantse ba, ƙaryar fashi ta ƙare." Aka sake su suka tafi.

Sufuyanu ya ce, "Wannan raƙumi shi ne ladata, ba na ba su." Ayari ya ɗunguma zuwa Makka. Da suka komo suka kai wa iyayen waɗanda aka kashe fam tamanin ɗin nan diyyar 'ya'yansu. Duk mutane suka yi ta mamakin fasahar Sufuyanu.

Waziri aku ya dubi Haziƙ, ya yi dariya ya ce, "Hala ka manta sunansa ne ka sa masa Sufuyanu? Ai Zafranu a ke kiransa cikin labarin na sosai, ba Sifuyanu ba."

Sarki Abdurrahman ya yi murmushi ya ce, "To, Waziri, da ya ce Sufuyanu da ya ce Zafranu, ai duk ɗaya tun da dai labari ya fita."

Waziri ya ce, "Allah ya ba ka nasara, ba ɗaya ba ne, in an san labarin da za ka bayar sai ka ba da shi yadda kowa ya sani, don kada a ce ba ka riƙe sosai ba. In ko ba a sani ba, kai ka ƙaga shi da kanka kamar irin labaran da na ke bayarwa, sa'an nan kome ka ga dama sai ka ce, ba mai ikon ya ce maka a'a."

Sarkin Sirika ya ce, "Wallahi gaskiyarka fa, Waziri. Kai kuma ba mu guda mu sha."

Waziri ya ce, "Yanzu," Ya fara.

# Kama Da Wane Ba Wane Ba Ne

A ƙasar Nisau an yi wani babban Sarki wanda a ke kira Nasiru. Mutanen ƙasar ba wanda su ke so da gani kamar Sarkin nan nasu. Ga shi dai da kyau, ga fuska, ga haƙuri sai ka ce ƙasa. Wajen wayo da hankali kuma kamar a ce ya fi kowa. In ko fagen fama aka fita, ko Ɗanwaire ya san da shi.

Ana nan, ran nan sai ya yi shiri ya hau da 'yam mutanensa za shi farauta. Da shigarsa daji sai ga barewa. Sarki ya ce wa mutanensa, "Kada ta kai!" Su kuwa suka ce da wa aka gama su ba da ita ba? Suka saki dawaki suka bi ta kararaf kararaf kararaf kararaf, Sarki na gaba suna biye. Barewa kuwa sai tsalle ta ke tana zuba musu ƙura. Can 'yan ƙurran bayin Sarki suka gaza, sai suka bar ingarmar Sarki kaɗai ya yi ta yi. Amma duk da tsananin gudun nan nasa, sai da barewar nan ta yi masa ƙau. Can zuwa rana faɗuwa Sarki ya yanke ƙauna, ya zame. Ya yi shirin komawa, ya nemi hanya ya rasa. Ga shi kuma rana ta faɗi. Shi ya yi ligya-ligya, dokinsa kuma hakanan.

Ya sami bakin wata ƙorama ya kwanta, ya saki dokinsa yana kiwo, shi ko sai barci. Bai ko farka ba har gari ya waye. Da safiya ta yi ya tashi sai ya ga ya ƙara ruɗewa makuwa ta kama shi, ya rasa gabas ya rasa yamma. Ya kamo dokinsa ya haye, ya yi ta yawo har ya kai ga wani dutse, ya ce a ransa, "Watakila in na yi ƙoƙarin da na hau dutsen nan, na iya samun alamar gari." Sai ya kama dutse da hawa, bayan ya ɗaure dokinsa a ƙasa yana kiwo. Yana cikin hawa ya kusa kai ƙarshe, sai ya ga wani farmemen kogo ya ɗauki 'yar tsakuwa ya jefa wai ya ji iyakarsa. Sai kawai, ba shi da sanannen ciki, ya ga wani ya fito daga ciki ya ɗadume shi, ya yi ciki da shi. Ashe kogon Sarkin aljannu ne ya jefa dutse.

Da aka shiga da shi, ya tarad da Sarki ya kame bisa karaga, sai fita a ke masa. Sarkin ajannu ya dube shi, ya ce, "Kai wane ne? Kuma daga ina ka fito?"

Sarki ya durƙusa, ya ce, "Ni ne Nasiru Sarkin Nisau, farauta na fito jiya da azahar, na biyo barewa, ƙaddara ta rabo ni da mutanena har na faɗo nan."

Sarkin aljannu ya ce, "Ashe da har kai kanka Sarki ne, ka zo nan ka jefe ni? Watau kai taƙamar tsiwa ko? To, yau ka faɗa musu lahira da gumi!"

Sarki Nasiru ya marairaice nan yana tangwar Sarki ya yafe shi, yana cewa bai sani ba ne, ka san ko rashin sani ya fi dare duhu.

Wani bawan Sarkin aljannu ya ce masa, "In ba ka sani ba, ba ka gani? Ko kai makaho ne?"

Sarki ya ce, "Da fa na gani ne, me zai kai ni jifarku? Ai ka san hankali ke gani, ido gululu ne."

Sarkin aljannu ya ce, "Zan yafe maka, amma sai in za ka yarda da abu ɗaya. Tun da na ke ban taɓa zama cikin mutane ba, cikin aljannu aka haife ni, cikinsu ko na tashi har Allah ya nufa na gaji gidammu. Yanzu abin da na ke so sai ka ba ni kayan jikinka in sa, in koma Nisau yau kaɗai in ga irin sarautarku ta mutane. Kai ko ka zauna nan gidana har garin Allah ya waye, gobe in dawo. Ko kuwa ma me zai kai ni har dare? Da magariba ta yi yau kwa gan ni, don ba na iya cin irin abincinku."

Sarki Nasiru ya ce, "To." Ya tuɓe tufafin da ke jikinsa duka ya ba aljani, ya ɗauki waɗansu ya sa. Ya tuɓe rawani ya yi wa aljani naɗi irin nasa, shi ko ya gangara ya kama dokin ya haye, ya nufi gari.

Ko da Sarkin aljannu ya shiga gari, ya rasa hanyar da zai bi ya shiga gidan Sarki. Yana nan yana bin titi, mutane ko sai faɗuwa su ke suna gaisuwa sun ga Sarkinsu. Sai ya ga wani saurayi, ya ce masa, "Kai, ci gaba mu je ka kai ni gidana." Saurayi ya ci gaba har fada.

Da 'yam barga suka ga Sarki tafe sai suka yi caa, suka kama masa ya sauka. Dogarawa suka bi shi, "Takawarka lafiya mai duniya, gangare linzami, Sarkin musulunci!" Aka kai shi Majalisa ya zauna. Mutane suka yi ta zuwa suna yi masa barka. Shi ko sai cewa ya ke "Ingwayya." Bai dai san kowa ba, balle ya kira sunansu.

Da aka ƙare masa barka, Waziri na zaune na la'akari da Sarki, ya ga dai a irin shigar da ya yi kamar Sarkinsu ne amma ga shi a ɗabi'a da murya kamar ba shi ba. Ya yi ƙokari ya lura da fuskarsa ya kasa, domin duk ya sunƙaƙe. Ga shi kuma ya san muryar Sarkinsu 'yar ƙarama ce, ga ta yau ya ji ta buɗe. Saboda haka dai ya kasa kannewa, ya ce, "Allah ya ba ka nasara, waje ka kwana ne jiya? Na ji muryarka ta buɗe haka, kamar ta wanda sanyi ya kama."

Sarkin aljannu ya ce, "Haba, kai dai bari, ai jiya na sha wuya. Ka ga sa'ad da muka hau ɗin nan, kuna biye da ni. . . ."

Waziri ya ce, "Allah ya ba ka nasara, ai ni ban hau ba. Ba ni ka ce in tsaya in tsare gari ba?"

Sarki ya ce, "I, haka kuwa ashe kai na bari tsaron gari. Da su magajin gari muka je ko?"

Waziri ya ce, "Ai Magajin Gari shi ka ce ya tafi ƙasar Sarkin arewa, don ya taimake shi karɓar haraji. Su Turaki, da Shamaki, da Shantali, da Sarkin Zagi ai su suka bi ka."

Sarki ya ce, "Hakanan ne kuwa, a kira su mu ji yadda suka ƙare da muka rabu."

Waziri ya ce, "Ai ga su nan gabanka.'

Sarki ya ce, "Kai, ni fa duk na ruɗe, ko gani ban iya yi sosai." Ya dube su, ya ce, "Yaya kuka yi da muka rabu? Kai, jiya Allah ya gwada mini ƙatuwar barewa da gudu. Da saurin dokina sai da ta yi masa fintinkau."

Bayin Sarkin nan suka ce, "Mu da muka ga 'yan ƙurrammu, sun kasa, sai muka ja, muka komo gida. Mun san dai kai im ba ƙarar kwana ba, ba abin da mu ke shakka da kai. Amma mun ji ka ce barewar ƙatuwa ce. Ko wata ce ka bi daga baya? Mu wadda muka tayar da kai da farko 'yar 'ya ce."

Sarki ya ce, "'Ya fa ina? 'Yar 'ya ta yi wannan gudu. Ai kun san ni ke gaba, na fi ku kusa da ita, ribɗeɗiya ce. Da na sake dai ta tsere mini, na yi shiri in dawo gida, sai na ga ba dama, dare ya yi ga shi kuma da ni da dokina mun zama haihuwar guzuma, ɗa kwance uwa kwance. Sai na sami ruwa na ba dokina, na share wuri na kwana, dokina kuma ya taɓa ɗan kiwo, zuwa safe. Da gari ya waye yau sa'an nan na taho."

Mutane suka ce, "An dai yi barka."

Waziri ya ce, "Batun haraji da na yi maka jiya, ba ka ce kome ba kuka hau farauta."

Sarki ya ce, "An ƙare biya duka ne?"

Waziri ya yi murmushi ya ce, "An ƙare biya, Allah ya ba ka nasara? Abin da aka buga watan jiya a ƙare biya yanzu? Yau dai duk nishaɗi ka ke ji, ga shi ma duk cikimmu mutanenka kamar ba ka san kowa ba, har yanzu ba wanda ka kira sunansa. Kowa ya gaishe ka sai ka ce masa 'Malam.'

Sarki ya ce, "Ai ruɗewan nan tawa ta wuce kima. Yaya batun haraji da ka ce?"

Waziri ya ce, "Sarkin Yamma ya aiko mutanensa na ta watsewa, da ka ce a rika kama dabbobinsu ana sayarwa dole."

Sarki ya ce, "To, ma yi shawarar abin da ya kamata."

Magatakardan alƙali ya zo, shi ne ko babban ɗan Sarki Nasiru, ya yi gaisuwa, ya ce, "Na zo kan maganar Hasan Gulumbe da ya ci bashin Tanko na sule uku da sisi, har yanzu bai biya ba."

Sarkin aljannu ya ce, "Sai a ɗaure shi shekara saba'in."

Magatakarda ya yi dariya, ya ce, "Shekara saba'in, Allah ya ba ka nasara!"

Sarki ya ce, "Ko sun yi kaɗan ne, a ƙara masa goma?"

Magatakarda ya rasa abin da zai ce. Sarki ya ce, "Yi magana mana! Don me na naɗa ka Alƙali im ba don haka ba?"

Waziri ya bushe da dariya, ya ce, "Ai ba shi ne Alƙali ba magatakarda ne."

Sarki ya ce, "Af, mts, ni duk na ruɗe don kwanan da na yi a daji. Ka ce ina gai da Alƙali in ka koma. Ka gaya masa na dawo, me ya sa bai zo ba?"

Ashe Alƙali na nan gabansa, sai ya ce, "Allah ya ba ka nasara, ai ga ni tun tuni na ke nan, da ni da Waziri."

Sarki ya dube shi ya ce, "O, ai ni duk ban kula ba, ka san hankali ke gani ba ido ba. Ina Wazirin da kuka zo tare?"

Waziri ya ce, "Allah ya ba ka nasara, ai tun ɗazu da kai mu ke ta magana."

Sarki ya ce, "Na sani, tsammani na ke Waziri Ƙarami ya ke nufi. Kai fa ba tun ɗazun mu ke maganar haraji ba?"

Waziri ya ce, "Allah ya ba ka nasara, ba wani Waziri Ƙarami nan garin, ko an naɗa wani ne ba mu sani ba?"

Sarki ya ce, "Kai, ni fa yau duk kaina dim na ke jinsa, ko mutane ma biribiri na ke ganinsu."

Waziri ya ce, "Da alama, Allah ya ɗaukake ka. Ya kamata mu ƙyale ka, gobe in ka natsa a ci gaba da sha'anin mulki. Mun bar ka lafiya." Suka watse.

Sarki ya tashi ya nufi gida yana ɓace hanya, sai da aka nuna masa, ya je kuma ya tarad da bayi da mata, ya yi ta yi musu shirme yadda ya yi a Majalisa. Suka rasa kansa da gindinsa, suka yi tsammani motsuwa ya yi da ya kwana a dajin nan.

Magariba na yi sai ya kewaya bayan ɗaki, daga nan ko ƙasa ko bisa. Ya tafi ya tarad da Sarki Nasiru, ya ce, "Kai, yau na sha surutai! Sarautarku ta mutane ba abin da ya fi ta wuya, yini mutum ba ya rufe baki. Waziri ya zo maganar haraji, Magatarkarda ya zo batun shari'a. Jakadiya ta zo zancen abinci. Haba! Ba a dai barin mutum ya huta?"

Sarki Nasiru ya yi aminci da Sarkin Aljannu ya sa aljannu suka ɗauko shi suka mai da shi gidansa kafin ƙiftawa ba bismilla. Ya ba shi kuɗi masu zimma.

Da gari ya waye Sarki ya fito fadanci, mutane suka taru, kowa ya yi gaisuwa yana kama sunansa yana tambayarsa labari kamar na wanda dai ya saba sosai, ba irin jiya ba. Waziri ya ce, "Allah ya ba ka nasara, wane irin maganin mura gare ka haka? Jiya-jiya ka zo nan duk muryarka ta buɗe, ga shi yau ta koma kamar da.

Jiya fa ba ka sani ba Allah ya ɓa ka nasara, ruɗewa ka yi. Ko magatakarda ka kasa ganewa, balle wani. Tsammani mu ke ka motsu ne, har zuciyoyimmu sun ɓaci. Hasan Gulumbe da ya ci bashin sule uku da sisi bai biya ba, ka ce a ɓa shi shekara saba'in a kurkuku. To, da kisan kai ya yi fa?"

Sarki ya ɓingire da dariya, ya kwashe labarinsa da Sarkin Aljannu duka ya faɗa musu. Suka ce me za su yi kuwa ba dariya ba. Waziri ya ce, "Haba, Allah ya ba ka nasara, Wallahi na so in lura da haka, tsoro ya hana ni furtawa. Lalle ne duk wanda ya yi karambanin da ya rabu da inda Allah ya ajiye shi, ya jefa kansa wani wuri, ya kuwa jawo wa kansa jidali da taɓewa." Daga nan sai wani marok̃in Sarki ya ɗauka da kirari:

"Ga wani ya so kama da Nasiru,
Kama da Sarki wuya gare shi,
A fuska saura kaɗan ya dace,
Ga shi da zati, ga shi da kyawo.
Ya sa jabba, ya sa kubta,
Amma hali ya sha bamban."

Hazik̃ ya dubi Waziri Aku, ya ce, "Wace irin wak̃a ce haka ba tsawo? Ga ta kamar taɗi, ita ba taɗi ba, kamar wak̃a na rasa inda karinta ke faɗuwa."

Waziri ya yi murmushi ya ce. "Yaro dai yaro ne. An taɓa wak̃a haka? Ba ka ji da zam fara na ce kirari ne ba? Irin kirarin k̃asar ke nan, ba irin naku ba a yi ta kama sunan iyaye da kakanni."

Kashegari yau, ko da aka taru ak̃a ce Hazik̃ ya fara, sai ya yi shiru yana tunani. Can ya ce, "Labarin K̃amaruzzaman ɗan Sarki Sharuzzaman."

Waziri aku, ko da ya ji wannan kan labari, sai ya fashe da dariya har ya ɓingire. Sarkin Sirika ya ce, "Wannan dariya fa, Waziri, ta mece ce haka?"

Waziri ya ce, "Ina tsammani Hazik̃ dai labarai sun k̃are, na ji ya fara taɓo Alfu laila ne juzu'i na uku, shafi 1777. Zai kuma tuna haddar da ya yi."

Sarkin Sirika ya dubi Hazik̃, ya ce, "Gaskiya, na Alfu lailan kuwa ne za ka bayar?"

Hazik̃ ya ce, "I, ai suna da daɗi."

Sarkin Sirika ya ce, "Tun da ya ke dai nan ciki duk kowa ya san waɗannan, sai ka ba da wani."

Hazik̃ ya ce, "Allah ya ba ka nasara, in gaya maka gaskiya, ni dai Wallahi labarun da ke gare ni duk sun k̃are, ba na ɓoyewa."

Mutane da jin haka suka kò ɗauka "Haa!" Watau Wazirinsu ya ci k̃wallo. Sai suka ɗauki tafi gaba ɗaya raf raf raf.

Sarki Abdurrahman ya ce wa Hazik̃, "Sai ka ba mu labarin da ka fara hakanan, tun da ka soma shi lalle a bari ka iyar, mai ji ya ji, wanda ba ya ji ya bari. Nan taron dai, in ka ɗebe Waziri, wa ke iya ba da waɗanda ma ka yi?"

Hazik̃ ya ce, "Hakanan ne fa." Sai ya ci gaba da abinsa.

# Labarin Kamaruzzaman Dan Sarki Shahruzzaman

A cikin zamanin da an yi wani Sarki a nan gabas wai shi Shahruzzaman. Ga shi da arziki, abin har ba a magana. Cikin zamaninsa an hakikance ba a taba samun mai arziki irinsa ba. Abin zai ba ka tausayi in ka ji duk abin nan da Sarkin nan ya tara ba shi da mai gadonsa, sai fa 'yan'uba.

Abin ya bakanta masa ciki, kullum in ya yi zaune ba ya kome sai zulumi. Yana nan ran ran sai wani tsoho ya zo gunsa, ya ce, "Abin da na ga ya fi a cikin wannan al'amari sai ka sa a tara shaihunan malaman kasan nan duka a rokam maka Maiduka."

Sarki ya ce, "Gaskiyarka, malam. Ya ko ce rokan ni in amsa maka." Sai ya aika kasashensa duka, aka tattaro masa manyan malaman da ke can, suka taru. Sarki ya gaya musu bukatarsa. Ko wannensu ya duka ba barci har kwana arba'in.

Allah maji kan bawa, kwanakin nan arba'in ba su cika ba sai da wata daga cikin matansa ta dauki ciki. Bayan kamar wata uku ciki ya bayyana, duk gari aka yi ta murna a kan wannan.

Da ciki ya yi wata tara, matan nan ta haifi da namiji wanda sa'ad da aka haife shi don tsananin kyaunsa mutane na tsegumin ko ba mutum ba ne, aljani ne. Da ya cika kwana bakwai aka sa masa suna Kamaruzzaman. Ba mai iya bayyana farin cikin Sarki bisa ga wannan.

Yaro yana nan yana ta girma, har ya sami kamar shekara goma sha biyu. Da ubansa ya ga ya yi girma haka ya ce zai yi masa aure, shi ko ya yi murabus, ya nada dan tun yana da rai.

Kamaruzzaman ya ce, "Sarauta dai ya yi, amma aure har abada." Uban ya yi biris da maganan nan, sai da aka yi kamar shekara guda kuma ya tabi dan da maganar aure. Yaro ya ce, "Allah ya ba ka nasara, ai na gaya maka ni da aure faufau."

Da Sarki ya ga abin da gaske ne yaron ya ke yi, sai ya kira Wazirinsa ya gaya masa abin da ya ke ciki da yaro. Ya shawarce shi dabarar da za su yi su ciwo kansa.

Waziri ya ce, "Ba yadda za a yi sai in Hakimai da Sarakuna da Alkalan kasan nan duka sun taru da Salla, a kira shi cikin taro a

tambaye shi. Na san cikin waɗannan ba ya musaya mana ba."

Sarki ya ce, "To, shi ke nan, sai mun gani." Da aka taru da Salla, Sarakunansa suka taru suka tafi gai da Sarki, sai Sarki ya kira Kamaruzzaman ya tayar masa da wannan magana.

Kamaruzzaman ya duƙad da kai, ya ce, "Allah ya ba ka nasara, tun bara waccan ka ke tambayata, na ce maka ba na yin aure har im mutu."

Sarki ya husata, don yaro ya ba shi kunya cikin taro. Sai ya sa dogarawa suka kama shi, aka kai shi wani tsohon gida can kusa da wani rafi, aka tsare. Da mutane suka tashi, Sarki ya dubi Waziri, ya ce, "Tsohon banza! Ka ba ni ɓatattar shawara, ka sa ɗana ya ba ni kunya a cikin taro. To, sai ka faɗi abin da kuma ka ga ya fi a yi masa, mu ji."

Waziri ya ce, "Allah ya huci zuciyarka, sai a bar shi can bakin kogin nan mu gani, ko ya ji tsoro ya amsa shawararmu."

Sarki ya ce, "To." Aka bar yaro can tsare kwana da kwanaki, ba mai zuwa wajensa, shi ba a barinsa ya zo wurin wani. Sai bayan kwana bakwai Sarki ƙan zo da shi da Waziri su tambaye shi ya yarda a yi masa aure? In ya ce har abada ba ya aure, sai su fice. Ka ji labarin Kamaruzzaman.

To, ashe kuma a can ƙasar Sin akwai wata yarinya 'yar wani babban Sarki na Gayur, an yi an yi ita kuma ta yi aure, ta ce ba ta yi. Sunan wannan 'yar Sarkin Badura. A wajen Birnin Sin kuwa, tun da a ke ganin kyakkyawa ba a taɓa ganin kamar Badura ba.

Abin da ya sa ko ita ta ƙi aure, tana da ɗan dalilinta. Wata rana ne dai tana shan iska, sai ta iske tarko ya kama wani namijin gwara, ta ga matar ta duƙa tana tsuntsunke tarkon da bakinta mijin ya fita. Badura ta tsaya tana kallonta, tausayi ya kama ta, ta sa aka kwance gwaran aka sake shi.

Ran nan kuma abin kamar na ƙaddara, ta sake fita yawo sai ta tarad da wani tarko kuma ya kama wata macen gwara, amma mijin ko da ganin ta fara fakafaka sai ya gudu, bai tsaya ya taimake ta ba. Da Badura fa ta ga wannan abu, sai ta sa aka saki matar gwara, ta ce, "To, ashe haka halin maza ya ke? Har abada ko ba na yin aure." Ka ji nata dalili.

Da ubanta Sarkin Gayur ya ji haka, ya yi ta rarrashin yarinya, ta ƙi aure. Sai ya sa aka kai ta wani gida can bayan gari, aka tsare, wai ko ta ji tsoro ita kuma ta yarda. Tsakanin garin Sarki Shahuruzzaman da garin Sarkin Gayur tafiyar wata duniya ce mai nisa, ba wanda ya san abin da a ke yi a ƙasar wani. Ka ji labarin Badura.

To, wata rana da dare Kamaruzzaman na barci, sai wata 'yar Sarkin aljani da a ke kira Maimunatu tana tashi, ta shaƙi ƙanshin

jibda na fita daga cikin gidan ḍa Kamaruzzaman ke tsare. Da ta san gidan nan ba kowa ciki, sai ta sauka, ta nufi ɗakin da Kamaruzzaman ke barci. Ta dube shi, ta yi salati ta ce. Kai! Tsarki ya tabbata ga Mai aikatawar abin da ya so. Ashe har cikin mutane ana haihuwar aljani? Kai, wannan bari ta cikin mutane, ko cikin aljannu samun kyakkyawa kamarsa babu." Sai ta tashi ta nufi yawo.



Tana cikin yawo sai ta gamu da wani aljani bawan ubanta wai shi Danhash. Ashe shi kuma wajen yawonsa ya ga Badura a Birnin Sin tana barci. Ya yi al'ajibin kyaunta. Saboda haka ko da ya gamu da Maimuna ya gaishe ta, sai ya ce, "Allah ya ba ki nasara, ba ki tambaye ni labarin kome ba. Ni ko ga ni da shi yana cina."

Maimuna ta ce, "Yadda labari ke cinka, haka ni ma ya ke cina. Neman wanda zan gaya wa na ke yi na rasa, sai fa kai yanzu da Allah ya koro mini. Amma faɗa mini naka mu ji."

Danhash ya ce, "Allah ya ɗaukake ki, yau na ga wata 'yar Sarki na barci. Nan duniya duk, na rantse har da girmanki, in kin ɗebe kamar ke, tsakanin mutane da aljannu duk babu irinta don tsananin kyau."

Maimuna ta dube shi, ta yi tsaki, ta ce, "Sakarai, maƙaryaci! Kuna cika baki ba ku san inda ajiyar Allah ta ke ba. Ɗan Sarkin da na gani yau, tun da Allah ya yi ka ma, ka taɓa jin mai kyaunsa ko cikin aljannu? Ni ma da labarinsa zan gaya maka."

Sai gardama ta kaure, kowa na tsammani nasa ne ya fi kyau. Sai suka tashi gaba ɗaya suka tafi ƙasar ḍa Kamaruzzaman ya ke, suka dube shi da kyau yana barci. Danhash ya ce, "I, lalle wannan ba shi da laifi, amma wadda na gani ta shafe shi fat."

Maimuna ta fusata, ta daka masa tsawa, ta ce su tafi Birnin Sin su ga tasa. Nan da nan abin aljannu, suka isa. Maimuna ta dubi Badura, ta ce, "I, kana da 'yar gaskiya, amma in ana maganar yaron can, sai a yi shiru. In dai ka ɗebe shi, nan duniya ba kamar wannan."

Danhash ya ce, "Allah ya ɗaukake ki, ko kuwa kina nufin in dai ka ɗebe wannan, nan duniya ba kamar wancan?"

Sai Maimuna ta harzuƙa, ta buga ƙasa da ƙafarta, sai ga wani aljani wai shi Kashkash ya tsago ƙasa ya fito, ya faɗi gabanta ya yi gaisuwa. Ta sa shi da Dahash su ɗauko Badura su kawo ta

ƙasar Shaharuzzaman, a gwada a ga wanda ya fi kyau.

Aljannun suka yi yadda Maimuna ta ce, suka ɗauko ta suka ajiye gado ɗaya, duk suna barci. Maimuna ta dubi Kashkash, ta ce, "Kai, wa ka ga ya fi kyau? Duba fa da kyau ka gani."

Kashkash ya ce, "Ai ba wanda ya fi wani kyau."

Maimuna ta ce, "Mutumin banza, wanda bai san kyau ba! A ta da su ɗai ɗai, a ga wanda ya fi begen ɗan'uwa, to, shi aka fi kyau."



Suka ta da Kamaruzzaman. Da ya farka ya ji mutum bayansa, ya duba sai ya ga yarinya wadda ba irinta nan duniya, ya ce a ransa, "Da wannan za a aura mini da na yarda." Ya yi kamar ya ta da ita, ya ji tsoron ko an kawo ta ne don ta ɗauke hankalinsa. Saboda haka ya kanne, ya haɗe begensa. Aljannu suka sa ya yi barci. Ka san fa ko da ya ke suna kallonsa, shi ba shi da ikon ganinsu.

Da ya yi barci, suka ta da Badura su ga abin da ita kuma za ta yi. Da farkawarta ta ga Kamaruzzaman, sai ta ce, "A a a a! In dai wannan baba ya ke so ya aurad da ni ga shi, na yarda." Ta fa kafa masa ido ba ta ko ƙiftawa, sai ta zare zoben hannunta ta sa masa, ta zare nasa ta sa hannunta. Sai aljannun suka sa ta yi barci. Suka ɗauke ta, suka mayar da ita Birnin Sin. Sauran aljannun nan suka ce wa Maimuna Kamaruzzaman ya fi kyau, don suna tsoron kada ta yi fushi da su. Kai ji inda wannan ta kwashe.

To, da gari ya waye sai Kamaruzzaman ya ce wa bawan da ke tsaronsa, "Shin yarinyar da Sarki ya sa ta zo nan wurina jiya da dare 'yar wane Sarki ce? In dai ita ce da ma a ke so in aura, to, ka gaya masa na yarda na yi aure."

Bawa ya ce, "Allah ya ba ka nasara, ai ba a kawo wata nan ba jiya da dare."

Kamaruzzaman ya ce, "Kar ka yi zancen banza. Ina wasa da kai ne? Ka tafi ka ce wa Sarki ina sonta."

Bawa ya tsaya cif shi bai ga yarinya ba. Da Kamaruzzaman ya yi fushi sai ya kama gemun bawan nan, ya yi ta dukansa, wai sai ya gaya masa gaskiya. Bawa da ya ji za a halaka shi sai ya ce, "Na san maganar, da ma an kawo ta a gani ne ko ka ce kana so."

Kamaruzzaman ya ce, "Waɗɗare gulya'e! Da da girma da arziki an ce ka faɗi, ka tsaya yi mini waɗansu ƙusurwoyi." Ko da

bawan ya samu ya kuɓuta, da ya garzaya bai zame ba sai gaban Sarki, ya kwashe labarin ɗansa duk ya faɗa masa.

Da Sarki ya ji haka sai ya bushe da dariya, yana tsammani ya kusa biyuwa ne. Ya aike Waziri ya je ya jiwo. Da Waziri ya isa sai Kamaruzzaman ya ce masa, "Yarinyar da kuka kawo mini jiya in ita za a nemam mini, to, na yi aure, amma im ba ita ba ce, ba na yi."

Ka san wannan al'amarin ba wanda ya san an yi shi, daga yaran nan biyu sai fa aljannun nan. Saboda haka Waziri ya ce ba su san wannan magana ba. Kamaruzzaman ya tarrashe shi, Waziri ya yi ta rantse-rantse ba a kawo wata yarinya ba. Sai Kamaruzzaman ya hau masa da duka. Waziri ya ƙwace da ƙyar, ya ruga buza-buza har wajen Sarki, ya kwashe abin da ya auku duka ya faɗdi, ya ce, "Lalle dai aljannu suka taɓa shi jiya."

Sarki ya dube shi, ya ce, "Kai, tsohon banza! Kai ka sa na ɗaure shi can, to, ka tabbata in wani abu ya same shi ka kuka da kanka." Ya tashi ya nufi gidan da kansa, Waziri na biye. Da isarsu yaro ya tashi ya gai da uban da harshe mai daɗi. Sarki ya amsa, sa'an nan ya dube shi, ya ce, "Wace yarinya ka gani ne na ke jin wai ka ce kana sonta?"

Kamaruzzaman ya dukad da kai don kunya, ya ce, "Wadda kuka kawo mini jiya, har kuka sa ta sauya zobenta da nawa, ga shi. Ba na son wata magana a neman mini ita, na aura."

Sarki ya ce, "Wallahi mu ba mu kawo maka wata ba. Ko kuwa aljannu ke son taɓa ka ne? Bari mu gani. Yau wace rana ce?"

Kamaruzzaman ya ce, "Lahadi, gobe Litinin, sai Talata. Laraba, Alhamis. Aljumma'a, Asabar, ko ba su ba ne?"

Uban ya ce, "Hakanan ne fa, ashe kana da sauran hankali, amma ba mu kawo kowa nan ba."

Kamaruzzaman ya ce, "Na ce na aure ta, to, mene ne kuma na ƙin amsa mini? Yaya za ku ce ba ku kawo kowa ba? Ga ko zobe, kowa ya san ba nawa ba ne. An taɓa ganin inda mutum ya yi mafarki yana yaƙi, ya tashi ya gan shi da takobi a hannu?"

Hankalin Sarki fa duk ya dugunzuma da ya ga yaro ya ruɗe. Aka sa malamai da bokaye su yi ta kawo masa maganin aljannu. Duk a banza. Kullum Sarki sai laifin Waziri ya ke gani, ya ce wai shi ya ba da dabarar.

Kamaruzzaman wasa-wasa abu ya koma ka mar ciwo, ba ya ci ba ya sha kwana da kwanaki, sai da kyar a ɗura masa kunu. Ka san soyayya babbar abu ce. Ka ji abin da ya faru ga Kamaruzzaman.

Amma abin da ya faru ga Badura ya ba ku mamaki in kun ji, duk ɗaya ne da abin da ya faru ga yaron nan. Ita kuma ta kwanta

ba ci ba sha, ana nemo malamai da bokaye suna ba ta maganin aljannu.

Na gaya maka inda aka tsare Kamaruzzaman da ma kuṣa da kogi ne. To, tun da yaron nan ya ruɗe haka zaman fadanci ya koma a zauren gidan. Ran nan ana zaune sai aka hango wani mutum kogin nan ya ciwo shi. Aka tashi aka faɗa aka ɗauko shi, aka matsa cikin, ruwa ya yi ta fita. Aka jiyyace shi, bayan kamar kwana uku ya warke.

To, ashe shi falke ne, ba inda ba ya bugawa, har Birnin Sin ya tafi. Yanzu ma daga wajajen can ya fito. Ya ko baro Badura 'yar Sarkin Sin tana ciwon wani yaron da ta gani da dare, har ta musaya zobe da nasa. Ko da kuma ya zo nan ya ji abin da Kamaruzzaman ke ciki, ya ji kuma labarin abin da ya auku gare shi kamar na Badura ne, sai ya ce a ransa, "Watakila yaran nan aljannu suka gama su. Watakila wannan shi ne wanda Badura ke so. Amma bari in gani. In na ga kyaunsa ya dace da Badura ta yi begensa haka, na yi sa'ar fatauci." Aka kai shi ga Kamaruzzaman. Ko da ya gan shi sai ya ce, "Ba shakka wannan shi ne." Ya dubi Sarki, ya ce yana da magani, amma sai a watse a ba su wuri su biyu.

Sarki ya ce, "In ko ka warkad da shi, zan yi maka kyauta wadda za ta ishe ka zaman duniya har 'ya'yanka."

Falke ya ce, "To, madalla." Ya shiga ɗaki ya tarad da Kamaruzzaman, ya ce, "Albishirinka."

Kamaruzzaman ya ce, "Goro."

Falke ya ce, "Bukatarka ta biya." Ya kwashe labarin Badura duk har da siffarta ya gaya wa Kamaruzzaman. Ko da Kamaruzzaman ya ji ya ba da siffarta daidai da yadda ya gan ta da dare, sai ya yi wuf ya tashi, ya rungume falke yana cewa. "To, yaya za mu yi mu sadu da Birnin Sin gobe?

Falke ya ce, "Allah ya ba ka nasara, ai daga nan zuwa Birnin Sin tafiyar wata duniya ce. Abin da dai ya fi yanzu sai ka ce ka warke. Amma kada ka gaya wa kowa abin da mu ke ciki. Im mun yi kamar wata guda sai ka ce mu je kilisa. Ka sami jaka ko biyar ka kai mana wani wuri ka ɓoye don guzuri. Daga wajen shan iska sai mu wuce. Ka san im ba haka ba Sarki ba zai bari ku rabu ba." Kamaruzzaman ya ce, "Hakanan ne."

Falke ya kira Sarki, ya ce, "Kamaruzzaman ya warke, da ma aljannu ne suka taɓa shi, na ko yi masa addu'a."

Batun murna da aka yi a wannan rana sai ya yi ƙurum. Ta ishe ka ma har tambura aka buga, hankalin kowa ya kwanta, tun ba Waziri da da za a ɗaure ba. Alherin kuwa da wannan falke ya samu, ka san wannan ba sai am faɗi ba.

Ana nan ana nan, bayan kamar wata guda sai ƙamaruzzaman ya yi yadda falken nan ya shawarce shi, suka ɗunguma. Da suka shiga daji sai suka sami awakin waɗansu Filani suka saya, suka yanka, suka zubad da jinin ko ina. Kamaruzzaman ya jefa rigarsa cikin jinin, farke kuma ya yi hakanan. Dabararsu don in an zo nemansu aka ga wannan sai hankali ya kwanta, a dangana. Su kuwa suka hau dawaki, suka yi ta yi. Falke shi ne aboki, shi ne bara. Ka ji abin da ya faru ga Kamaruzzaman.

Amma Shahruzzaman da la'asar ta yi ba a ga sun dawo ba sai aka hau dawaki aka bi. Aka yi nema har dare ba a gan su ba, aka komo. Da safe kuma Sarki ya ce a koma, kada kowa kuwa ya sake dawowa sai an ga inda Kamaruzzaman ya ke. In ko ba su gan shi ba, su yi ta bin duniya har su mutu duka can garin nema.

Mutane suka bazu, ana ta nema. Can sai waɗansu suka iske inda rigar Kamaruzzaman ta ke, ga jini faca-faca ko ina. Suka rugo da kuka, suka gaya wa Sarki. Ya hawo ya zo ya gani da idanunsa. Daga nan fa batun baƙin ciki a garin nan da wajen Sharuzzaman, sai in ƙyale ka in gani in kana da ikon ka riya iyakarsa ko da cikin ranka. Ka ji kuma inda wannan tasa ta kwashe.

Bari mu koma kan na Kamaruzzaman. Suna nan suna tafiya, a kwana a tashi suka isa Birnin Sin. Kafin su kai garin suka sai da dawakinsu, suka isa a ƙasa. Da zuwansu suka tarar Sarkin Birnin Sin ya gaji da mutane masu zuwa suna cewa suna da magani na ƙarya, har ya yi alkawari wanda duk ya ga Badura ya ba ta magani ba ta warke ba zai kashe shi. Kadan ko ta warke zai ba shi aurenta, ko tana so ko ba ta so. An kashe mutane da yawa da suka yi ƙoƙari suka kasa.

Da isar Kamaruzzaman sai ya tafi fada, ya ce yana da magani. Sarki ya dube shi, ya ce, "Kai, wannan yaro mutum ko aljan? Abin da ya fi da ma ka rufa wa kanka asiri, ka dangana da wannan baiwa da Allah ya yi maka."

Kamaruzzaman ya ce, "Cewa ka yi duk wanda ya gan ta, bai warkad da ita ba, za ka kashe shi. To, ni maganina ba na ko so in gan ta, a kai ni ƙofar ɗakin in tsaya daga waje in yi ƙoƙari, in na kasa na san tun da dai ban gan ta ba ba a kashe ni sai dai in za a ba ni wani horo a ba ni."

Sarki ya yi murmushi, ya sa aka kai shi kofar ɗakin. Ya ce a kawo masa alkalami da tawwada da takarda, aka kawo masa. Ya rubuta mata takarda, ya bayyana mata siffarsa da yadda suka gamu, ya ɗauki zoben nan nata da ta musaya da nasa, ya ƙunshe cikin takardar ya aika mata da shi. Shi ko yana ƙofar ɗaki. Ko da ta karɓa ta buɗe ta ga zobenta, sai gabanta ya faɗi. Da

karantawar takardar sai ta yiwo wuf ta buɗe ƙofa ta leƙo. Ta ga Kamaruzzaman ta rungume shi.

Nan da nan aka je aka gaya wa Sarki 'yarsa ta warke. Ya shigo da sauri ya gani. Ta ɗauki zobenta na da, ta nuna wa uban. Sarki ya ce, "Haba, ko da ganinsa na san bai dace da kowa ba nan duniya sai ke." Aka tambayi Kamaruzzaman labarinsa duk ya faɗi. Da aka lissafa kwanakin, sai aka ga rana ɗaya ce da safiyar da Badura ta tashi tana haukan sonsa. Aka yi ta mamaki ana cewa aljannu suka gama su, don sun ga ba kamarsu kyau nan duniya.

Sarki ya ce, "Tun da Allah ya nufa haka, ai ba wani abu sai a yi aure. Ga shi kuma abu ya zo daidai, kai ɗan Sarki ita 'yar Sarki." Aka tara mutane aka gaya musu, aka yi ta murna, abin sai a yi shiru.

Da aka yi kamar kwana goma sha biyar ana murna, sa'an nan aka shiga sha'anin biki. Aka yi biki irin wanda ba ka taɓa ko jin labarin kamarsa ba.

Ana nan suna cin duniyarsu a Birnin Sin da abokinsa falken nan, sai wata rana da dare Kamaruzzaman ya yi mafarki da ubansa. Da gari ya waye ya je ya gaya wa Sarki yana so in ya yarda ya tafi ƙasarsu ya ga ubansa, don hankalinsa ya kwanta ya san bai mutu ba.

Sarki ya ce, "Wannan shi ne hankali, sai ka ɗauki matarka ku yi shiri ku tafi, amma kada ku daɗe can, ku dawo da wuri."

Kamaruzzaman ya yi shiri ya kwashi raƙuma, da kaya, da bayi, da kuɗi, abin ba a cewa kome, ya sa matarsa Badura gaba, suka tasam ma ƙasar Shahruzzaman.

Suna nan suna tafiya ba dare ba rana, ran nan da maraice sai suka iske wajen ruwa. Kamaruzzaman ya ce a sauka a ba raƙuma. Aka sauka aka ba su, aka bar su su huta su taɓa kiwo kafin safe. Can da tsakad dare, kowa ya yi barci, sai Kamaruzzaman ya ɗauki buta ya kaikaita wa hanya don ya kewaya, yana kai gindin wata tsamiya sai ya ji an ce, "Yi hankali kada ka taka mini kore, na yi shanya."

Kamaruzzaman ya duba, bai ga kowa ba, sai ya tsorata ya juyo da baya. Ɗaga ƙafan nan da ya ke yi sai ya ji an ce, "Ka ko taka, don tsaurin kai! Wai kai kyakkyawa ko? To, ka san taurin kai na da amfani." Sai ya ji kamar wani mutum ya yi sama da shi, aka yi ta tashi da shi, bai ga mai tafiya da shi ba, har aka kai shi can wani lambu cikin wani tsibiri, aka ajiye. Ya rasa inda ya ke a duniya.

Yana nan kwance har gari ya waye, ya tashi yana kewaya lambu sai ya tarad da wani tsoho, ashe shi ne mai lambun. Kamaruzzaman ya gaya wa tsohon yadda abin ya faru duka.

Tsoho ya ce, "Kayan aljannu ne ka taka, amma ba kome tun da dai ba su halaka ka ba. Akwai jirage masu zuwa nan, amma daga shekara sai shekara. Ga shi kuma ka yi sa'a, yau saura wata guda za su zo. Da sun zo sai in sa su ɗauke ka su mai da kai ƙasarku." Kamaruzzaman ya yi murna, ya zauna nan da mai lambu yana ta yi masa buɗi kullum in ya tashi ban ruwa. Ka ji abin da ya auku ga Kamaruzzaman.

Badura kuwa, ko da ta tashi da asalatun fari ta nemi miji ba ta gani ba, sai al'amarin aljannu ya faɗo mata a rai, don ta tuna abin da ya auku gare su da fari. Ta tashi tana kewaya wurin, sai ta kai gindin tsamiyan nan ta ga buta a yashe, sai ta dawo ta hakikance aljannu suka ɗauke shi. Ta rasa abin da za ta yi. Ita ba abin ta koma ba ta bar shi, ita ba abin ta ci gaba ba, to, ta ce me? Sai ta koma ta sake dabara. Ka san da ma sun yi kama, sai ta yi shiri irin nasa, ta hau raƙuminsa, ta yi wa wata baiwa shiri irin nata, ta sa ta yi lulluɓi yadda ta kan yi, ta hau raƙuminta. Suka yi ta tafiya, ban da su biyu ba wanda ya san abin da ya faru. To, dabarar Aɗura su isa Birnin Ebone inda za ta sa a riƙa duba Kamaruzzaman a ɓoye har ta sami labarinsa.

Da Badura ta sauka garin, sai ta tarar ashe Sarkin garin kuma na da wata 'yarsa wadda a ke kira Hayatunnufusi, ba shi da wani ɗa ba jika, sai wannan yarinyar ita kaɗai. Duk nan ƙasarsu ita kuma ba a taɓa ganin wanda ya kai ta kyau ba.

Na gaya maka Badura fa da shiri irin na maza ta ke, har da naɗi da amawali. Ko da bayin Sarkin Ebone suka kawo wa Badura abinci, suka ga kyaunta, sai suka je suka tsegunta wa Hayatunnufusi, wata tsohuwa ta laɓaɓo da ita ta zo ta ga Badura. Sai yarinya ta ce ita ba ta son kowa sai baƙon ɗan Sarkin nan, watau Badura. Ba su sani ba mace ce.

Da Sarki ya tambayi wani bawa sunan ubangijin nan nasu sai ya ce, "Kamaruzzaman ɗan Sarki Shahruzzaman. Matarsa kuwa, wadda ba ta ko yarda a ga fuskarta don kunya, 'yar Sarkin Birnin Sin ce."

Aka lallaɓi Badura da ta auri Hayatunnufusi, ta ga ba damar ta ce a'a, sai ta yarda. Aka yi aure, aka yi shagali mai yawa. Ba a san mace ce ta auri mace ba.


Da aka natsa, Badura ta lura da Hayatunnufusi ta ga ta kirki ce, sai ta ce mata, "Rantse yanzu, in na gaya miki labarina duka, za ki taimake ni, ba ki tona mini asiri ba."

Hayatunnufusi ta rantse, sa'an nan Badura ta kwashe labarinta kaf ta gaya wa Hayatunnufusi. Da yarinya ta ji haka, sai ta fashe da kuka don tausayi, ta ce, "To, in Allah ya so ba mai jin wannan. In Allah ya nufa ya dawo, ko an sami labarinsa, in ya so

shi ya aure ni mu tafi tare. Ni dai yanzu ba na iya rabuwa da ke, don mun saba, kome munin halin mijinki kuwa na aure shi, ko don ke.'' Suka rufa wa kansu asiri, suka yi ta zama. Badura kullum ta je fada ta harɗe a kan karaga kamar namiji. Da Sarkin Ebone ya ga hankalin Badura ya kwanta da 'yarsa, sai ya yi murabus, aka naɗa Badura sarauta. Mace da mata biyu ga shi kuma tana sarauta, amma ba a sani mace ce ba. Ka ji labarin Badura.

Amma Kamaruzzaman kullum yana nan yana ta aiki a lambun har ya iya jan cakarkara. Bayan kamar wata biyu sai ga jirgi ya zo. Mai lambu ya sami kwando ya cika wa Kamaruzzaman da kayan marmari, su ɓaure da gwanda da sauran irin kayan lambu. Kamaruzzaman ya ɗauki zoben Badura, watau wanda aljannu suka yi masa musaya, ya sa ƙarƙashin kwandon nan, ya mai da kayan lambun nan bisa. Abin da ya sa ba ya sa zoben a hannu yanzu, don ya rame ƙwarai saboda wahala da bege, har zoben ba ya zama a hannunsa, sai ya riƙa sullewa yana faɗuwa. Don gudun kada ya faɗi ya ɓace, shi ya sa ya riƙa ajiye shi cikin kaya.

To, ko da mai lambu ya tafi da Kamaruzzaman aka yi jingar abin da za a biya zuwa babban Birnin Ebone, domin nan ne matsayar jirgin, watau fa inda Badura matarsa ke Sarauta. Mai lambu ya biya kuɗin sufurin Kamaruzzaman, ya sa kayansa cikin jirgi. Ya koma su yi sallama da mai lambu. Ashe masu jirgi sun yi gajin haƙuri. Da suka ga bai dawo ba da wuri, suka tuƙa suka tafi



da kayan Kamaruzzaman cikin jirgi. Ga su nan bayan kwana uku suka isa Birnin Ebone. Ka ji yadda waɗannan tasu ta kwashe.

Kamaruzzaman kuwa da suka gama sallama da tsoho, ya rako shi wajen jirgi yana kuka, sai suka hangi jirgi ya shige teku. Suka yi kuwwar kira. Af! Ba wanda ya ji. Aka bar Kamaruzzaman nan yana baƙin ciki, abin har ba ya faɗuwa. Babban abin da ya sa shi baƙin ciki, rabuwa da zoben nan na Badura. Da shi ya kan gani ya tuna da ita, Hankalinsa ya kwanta. Ka ji aikin ƙaddara.

Mai jirgi kuwa da isa Ebone sai ga bayi, Sarki Badura ta aiko a tambayar mata ko akwai kayan marmari. Da ma wannan jirgi abin da ya kan sa ya je tsibirin nan ke nan don ya ɗauko su.

Da aka tambayi masu jirgi suka ce ai duk an sayar, saura kwando guda na wani da ya sa, amma ya makara sun bar shi. Bayi suka sayi kwandon guda, aka kai wa Badura. Ko da aka je za a sake, sai ga zobenta. Da ƙyalla ido ta gan shi, sai gabanta ya faɗi, ta yi wuf ta ɗauka, ta duba, sai ta sallami bayi. Ta nuna wa matarta Hayatunnufusi ta ce, "Albishirinki!"

Hayatunnufusi ta ce, "Goro."

Badura ta ce, "Kin ga zoben nan na mijina ne." Nan da nan aka aika dogarai suka zo da mai jirgi. Sarki Badura ta tambaye shi mai wannan kaya da ta saya.

Mai jirgi ya kwashe yadda aka yi har ya bar shi a tsibirin nan ya faɗi. Sarki Badura ta ce ya koma yanzu ya zo da shi. Mai jirgi ya tashi jiki na ɓari, ya tuƙa jirgi har ya isa tsibirin nan ya tarad da mai lambu, ya ce masa, "Yaron nan kyakkyawa ashe kyaun banza gare shi, ɓarawo ne. An ce yanzu in tafi da shi."

Nan da nan Kamaruzzaman ya yi sallama da mai lambu, ya kuma sake ba shi waɗansu kayan marmari, suka tuƙo ba ko tsayawa har Ebone. Kamaruzzaman bai san abin da ya sa wannan al'amari ba. Tsammani ya ke yi Badura ta koma garinsu tuni.

Da isarsu suka tafi da Kamaruzzaman wajen Sarki Badura, ta duba ta ga Kamaruzzaman ne. Amma shi bai gane ta ba, don ta sha naɗi, ga amawali da wando mai zina, ga alkyabba ta sa ta kame bisa karaga ana fadanci. Ta yi kamar ba ta san shi ba. Ta sa Sarkin Zagi ya ba shi ɗaki, ya ajiye kayansa.

Dare na yi ta kira shi, ta kai shi wajen Hayatunnufusi ta cire rawani. Ko da ya duba sai ya gane ta. Suka rungume juna, suna kuka don murna. Hayatunnufusi ma da ba ta san shi ba, don tausayi har ta taimaka musu kuka.

Da suka share hawaye, Badura ta kwashe labarin abin da ya auku bayan rabuwarsu duk ta gaya masa. Kamaruzzaman ya dubi Hayatunnufusi, ya ce, "Allah ya yi miki albarka kin ko cika 'ya. Mun ko gode wannan asiri da kika rufa mana." Shi kuma ya kwashe labarinsa duka ya ba su, suka sake fashewa da kuka don tausayi da murna.

Cikin daren nan suka ɗunguma su duka uku, suka tafi wajen tsohon Hayatunnufusi, suka bayyana masa abin da ya faru duk tun farko har ƙarshe. Kamaruzzaman kuma ya gaya masa yadda ya auku har ya auri Badura, da yadda suka rabu. Sarki ya yi mamakin wannan abu.

Gari na wayewa aka tara mutanen gari, aka gaya musu labarin abin nan da ya faru duka, suka yi ta mamakin wannan al'amari.

Kamaruzzaman kuma ya nemi a ba shi Hayatunnufusi, Sarki ya yarda da wannan. Aka yi shagali wanda ba ya bayyanuwa cikin wannan ɗan lokaci. Aka yi wa Kamaruzzaman sarauta maimakon Badura, suka yi ta cin duniyarsu.

Waziri aku ya ce, "To, mu je mana ka iyad da na Asadu da Amjadu."

Haziƙ ya ce, "Wane ne Asadu da Amjadu kuma? Ai ni ban san waɗannan ba."

Waziri ya fashe da dariya ya ce, "Ashe kai hardar banza ka yi in ka tsaya nan. Ina ma'anar wannan labari? Kowa ka tambaya nan, su dai sun ji labari kawai dogo, amma ba abin da ya ƙare su da shi. Da ma iyad da labarin 'ya'yansa su Amjadu da Asadu da abin ya fi armashi. Da ka san ba za ka iya iyad da wannan labari ba, ka haddace na Hasan Mai'igiya mana, ko na Amina Mayya, ko na mai ƙusumbi. Ga labaru nan masu daɗi 'yan gajajjeru, ka kasa ɗaukar ɗaya ciki ka hardace, sai ka faɗa wannan da ba ka iya iyad da shi? Da ma ba ka fara ba, da mugun rawa gwamma ƙin tashi. Bari in iyar muku, jama'a, kada a tashi ya zama yinin nan na yau ba ku ƙaru da kome ba daga wajemmu." Sai ya duƙa aiki:

# Labarin Amjadu Da Asadu

Kamaruzzaman ƙa nan Ebone suna cin duniyarsu da matansa, sai Allah ya ba Badura ciki ta haifi ɗa, aka sa masa suna Amjadu. Badura ba ta yi wata guda ba da haihuwa sai Hayatunnufusi ta haifi ɗa namiji, aka sa masa suna Asadu. Suka tashi gaba ɗaya kamar 'yan tagwaye. Da ka gan su ka ga uban, in kun tuna yadda aka bayyana muku kyaun ubansu ɗazu, ba lalle ba ne sa'an nan im bayyana muku siffar 'ya'yan nan.

Da yaran suka yi shekara goma sha biyu, sai Kamaruzzaman ya fara koya musu sha'anin mulki. In zai kewaya ƙasa sai ya bar su gida su yi sarauta. Aka ce su riƙa rabawa, in wannan ya hau gado yau, gobe ya sauka gudan ya hau. Kome suka aikata kuwa ya zartu.

Ran nan Amjadu na bisa gado, sai wata makira daga cikin saɗakun uban ta rubuto masa takarda. Ta ce ya kamata ya tashi tsaye, Hayatunnufusi na nan na neman magani za ta sa a kashe shi, a kashe Badura, don ɗanta ya yi sarauta. Ta ce, "Saboda haka ya kamata mu kuma mu tashi tsaye, mu riga su. Ni zan nemi guba im ba ka, mu sa cikin abincin Asadu da shi da uwarsa, in sun ci duk su mace mu huta. Kai kuwa in ka yi sarauta ka sa ni babbar jakadiyarka. Ka san fa an ce kashe macucinka kafin ya cuce ka. In kai ba ka iyawa, ka ba ni izni ni na yi kome."

Da yaron nan ya karanta wannan takarda sai ya yi ta kuka, ya sa aka kashe tsohuwar da ta kawo ta, aka nemi dalili aka rasa, ko uwarsa bai gaya mata ba. Ya ɗauki takardar ya sa a aljihu. Gari na wayewa kuma Asadu ya hau gado, shi kuma sai ga takarda daga wata makulliya ta aiko wa Asadu, ya buɗe ya karanta sai ya tarar da daidai abin da waccan makulliya ta aiko wa Amjadu. Wai shi kuma Asadu ya yi hankali da Amjadu, suna nan suna ƙullawa da uwarsa za su kashe shi da Hayatunnufusi.

Shi kuma da ya karanta ya aikata yadda wansa Amjadu ya yi duka, ko junansu ba su gaya wa abin da ya faru ba, balle wani.

Ashe abin da ya sa makullan nan wannan makirci hassada ce don sun ga su ba su da 'ya'ya, kuma Sarki bai kula da su ba

kamar yadda ya kula da Badura da Hayatunnufusi. Su ba bayi ba, amma am mai da su kamar bayi, don ba mai faɗi a ji gidan, daga Badùra sai Hayatunnufusi. Suka gama kai suka aiko da takardun nan haka, wai da su niyyarsu ko wanne ya tasam ma ɗan'uwa. Su kuma su yi ta ƙara iza su, iyayen mata ba su sani ba, har su sa su yi mutuwar kasko, fada ta zama tasu.

Da suka ga abin da yaran nan suka aikata, suka yi tsammani in Kamaruzzaman ya dawo za su nuna masa takardun nan ne, suka ga kuwa lalle in Sarki ya ga takardun nan, ba abin da zai hana su kwana lahira ran nan. Saboda haka suka taru su biyu, suna shawarar abin da za su faɗi in Sarki ya dawo, don su riga yaran nan, ko Allah ya ba su sa'a su kuɓuta. Suna shawara kullum har suka sami dabara.

Ana nan Sarki ya dawo, da saukarsa ba su bari ya ko fito waje ba sai suka iske shi, suka ce suna da magana. Ya ƙaurace, suka tsuguna suka yi ta ƙulla ƙarairayi. Suka kwashe abubuwan nan da suka rubuta, suka ce yaran ne suka aiko musu su taimake su. Suka ce ko wanne bai san ɗan'uwansa ya aiko ba. Suka ce wai bayin nan da ya ji an kashe su ne suka aiko, wai don kada su ƙarar shi ya sa suka kashe su. Kai, makirci dai duk wanda ka sani, har wanda ba ya faɗuwa, matan nan suka ce duk yaran nan sun yi shi, da Sarki ba ya nan. Suka ce sun gaya masa ne, don kada abu ya ruɗe nan gaba, a rasa abin da ya sa shi. "In kuma kana tsammani ƙarya mu ke yi, ka kira su ɗai ɗai ka tambaye su, ko sa iya gaya maka kowa abin da ya sa ɗan'uwansa ya kashe baiwa guda. Ka san in da suna zaman lafiya, lalle kome guda ya aikata gudan ya sani. Ka ji kowa ya ce bai sani ba, ɗan'uwan bai gaya masa ba."

Da Sarki ya ji haka ya kira yara ya tambaye su ɗai ɗai, suka kasa faɗin wani abu, don ba su gaya wa juna ba. Ya tambaye su kuma ɗai ɗai abin da ya sa suka kashe bayinsa, aka rasa maganar kamawa, don ko wannensu na jin tausayin ya bayyana asirin sosai, kada Sarki ya sa a kashe matan nan. Suna ganin in sun yi haka sai a ce don ba iyayensu ba ne.

Da Sarki yaga ba su faɗa masa wani abin kirki ba, sai ya harzuƙa, idandunan nan suka jujuye, ya tashi ba ya ko gani ya sa aka kira tsohon nan, uban Hayatunnufsi, ya kwashe al'amarin nan duk ya gaya masa. Tsohon Sarki ya harzuƙa, shi kuma ya ce, "Tun muna da rai ke nan, ina ga im muka mutu?" Sarki Kamaruzzaman bai tsaya neman shawara ba, sai ya kira hauni da dare, ya ce ya tafi da 'ya'yan nan nasa daji, ya sassare su duka.

Hauni da ya tsaya wani 'yan noƙ-noƙe, Sarki ya buga masa tsawa ya ce, "Don me na ajiye ka, ba sai da ka ɗauki alkawari ba ka saɓa mini ba na naɗa ka. Kome sonsu da ka ke yi, ka san na fi

ka. Tun da ka ji ko na ce a kashe su, ka san kada a tona. Abin da ka ga ya koro ɓera har ya sa ya faɗa wuta, to, ka tabbata hakikan ya fi wutar zafi."

Hauni ya ɗauki gaya-wa-jini-na wuce ya rataya, ya tasa yara gaba da tsakad dare, ba wanda ya san abin da a ke ciki, daga shi hauni sai fa Sarki, ya fita, suka shiga daji, suka yi ta tafiya har gari ya waye da zuwa hauni ya ce musu "Kamaruzzaman ya ce in zo in kashe ku. Amma ni ban san dalili ba. Ni ko lalle na yi alkawari ba na wuce umurni Sarkin. Duniyan nan duk, ko Shahruzzaman ubansa ya ce in sare ina sare shi."

Yara suka ce, "Allah ya daɗe da ran baba, in ka ƙi cika aikinsa, ina amfanin ajiye ka ke nan?"

Ko wanensu ya gane laifinsa wajen kashe baiwan nan ne da ƙwarƙwaran uban ta aiko. Amma har yanzu ba wanda ya faɗa wa ɗan'uwa abin da ya sa ya kashe baiwa guda ran a ya hau gado.

Hauni ya ce, "To, ku raba, wa zam fara kansa?"

Amjadu ya ce, "Sai ka fara kaina, ba ni ne babba ba?"

Asadu ya ce, "A'a, in am fara kanka watakila na ji tsoro in motsa, in ta kawo kaina. A dai fara kaina, don kada in yi fargaba."

Amjadu ya ce, "Ba na iya ganin an sare ka, tun kafin a zo gare ni ma baƙin ciki ya kashe ni."

Suka yi ta gardama, kowa na cewa a fara kansa. Hauni ya ce, "In kun ƙi gaya mini wanda zam fara sarewa, sai ku tsaya ku gama bayanku kuna tsaye, ni ko in ɗaure ku da igiya gaba ɗaya, tun daga hannuwanku har ya zuwa kafaɗu don kada wani ya goce, ku sa ni in sara sau biyu. Na ko yi alkwari da Sarki ran da na sari ƙato, ban ɗauke kansa ba a fid da ni."

Yara suka ce, "I, haka ko ya kamata a yi." Hauni ya sa asalwayi ya ɗaure su tamau.

Amjadu ya ce, "Sai ka komo ta gabana ka fara sarawa, don kada Asadu ya ga sa'ad da za ka sara hankalinsa ya tashi."

Hauni ya juyo gabansa zai sara sai dokinsa ya firgita, ko me ya gani ya barzama dawa da gudu, Allah kaɗai ya sani. Hauni ya yar da takobi, ya bi doki kada ya ɓace. Ya bar yara nan tsaye, tun safe har rana ta yi zafi ba su motsa ba.

Da suka ga bai dawo ba, suka ce, "Ya kamata mu kwance kawunammu in muna iyawa, mu ɗauki takobin mu bi shi ya kashe mu mu huta. Ga yunwa da ƙishirwa na cimmu a banza." Suka yi ta kici-kici har suka kwance kawunansu, suka tafi kowa na gaya wa ɗan'uwansu dalilin da ya sa ya kashe baiwa. Suka ga ashe duk al'amarin ɗaya ne, kowa ya fidda takardar da ƙwarƙwarar Sarki to aiko masa, suka karanta, sai suka gane



makirci ne ɗai matan nan suka ƙulla musu game da Sarki. Suka ƙyale, ba su ce kome ba, har suka kai ga inda ya ke.

Ɗa suka iske shi, ashe dawan da wata zakanya mai 'ya'ya, doki ya sa huni ya haye mata ba sanannen ciki. Zakanya ta durmushe shi za ta kashe, sai ga yaran nan. Amjadu ya sa gaya-wa-jini-na-wuce, ya sare zakanyar Hauni ya kuɓuta yana kaɗuwa.

Asadu ya ce wa Amjadu, "Ba shi takobin maza ya kashe mu, mu kuma mu huta, ni yunwa na ke ji."

Hauni ya dube su jiki ṅa rawa, ga zakanya tim kwance, jini ko ina face-face, ya ce, "Kai, ku rufa mini asiri, im bi ta ina in kashe ku? Ba don ku ba, ni da ko labarina a ji? Ku dai ku san inda kuka nufa. Ni ko in tafi ga Sarki in ce na kashe ku."

Amjadu ya ce, "A'a, ni sai ka kashe mu mu huta, to, ina za mu? Don me Sarki ya ajiye ka?"

Hauni ya ce, "Bari ta ku ma, daga wannan na tuba da sare mutane. Ku ƙyale ni, ni na san abin da na gani. Ku dai ku tafi, in kuna da sauran shan ruwa, to, in ko ba ku da shi, kuma wannan ba da jinina ba."

Da yara suka yi suka yi, ya ƙi kashe su, sai suka fid da takardun matan nan suka ba shi, suka ce, "In ka je ka ba baba waɗannan takardu, ka ce kuma da za ka kashe mu mun ce a gaya masa wanda ya ce zai riƙa kama maganar mata da gaskiya ya ko yi da na sani. Amma mun ce ya yi mana gafara."

Hauni ya karɓi rigunansu ya tsoma cikin jinin zakanya, ya kamo dokinsa ya hau, ya tafi gari da riguna jina-jina, watau shaidar ya cika aikin Sarki.

Da Sarki ya ga haka ya yi murna, amma da hauni ya ba shi



takardu ya karanta su ɗai ɗai, ya kuma gaya masa saƙon da suka yiwo, sai Sarki Kamaruzzaman ya faɗo daga bisa kujera ya some. Aka watsa masa ruwa ya farfaɗe.

Ya ɗauki takardun nan ya kai wa surukinsa, shi kuma ya karanta. Aka ba iyayen yara su kuma suka gani. Aka jawo matan nan aka sa musu ƙiri a wuya, aka kewaya da su gari kowa ya tsine musu. Sarki ya sa aka tsire su, aka barsu nan suna haure-haure, suna buɗe baki har suka mace. Hauni dai bai ce ya saki yaran ba, balle a bi. Amma batun baƙin cikin Sarki Kamaruzzaman da surukinsa da iyayen yaran nan, in an ce za a tona, kai kanka ba ka jin daɗin labarin ba, domin baƙin ciki. Abin da ya fi dai sai mu rufa Ka ji labarin Kamaruzzaman da 'ya'yansa.

Amma su yaran nan da suka ga hauni ya tafi, sai su kuma suka miƙa cikin daji ba su san inda za su ba. Ba su da abinci sai 'ya'yan itatuwa. In dare ya yi su sami ice su haye su kwana bisa, da safe su tashi su miƙa. Suka yi ta yin haka har kwana goma sha biyar, ba su kai ga gari ba.

Ran nan suna cikin tafiya sai suka tarad da wata barewa matacciya, ba su san abin da ya kashe ta ba. Suka yi murna, suka

ɗauka, suka sami kartajiya suka yanyanka barewan nan kamar kilishi suka shanya. Da ya bushe suka ɗauka suka riƙa ci sannu sannu, suna gamawa da 'ya'yan itace. Suka yi ta tafiya kwanaki, sa'an nan suka isa wani gari ƙato. Amjadu ya ce wa Asadu, "Sai ka tsaya nan, ni in shiga in yiwo mana bara, in na ga mutanen garin na kirki ne in zo in kira ka, mu shiga mu nemi wani gida mu yi barantaka.

Asadu ya ce, "A'a, sai dai ni in tafi, ba na iya zama nan daji ni kaɗai." Amjadu ya bar shi ya tafi, ya shiga gari.

Yana shiga sai ya fara isa gidan wani mutum, ya tsaya ƙofar gidan yana cewa, "Masu gida, ku taimake ni da sadaka, domin ƙaunarku da Shugaban talikai. Masu gida, ku ji ƙaina, yadda Allah ya ji ƙanku."

Yana cikin bara sai wani tsoho ya fito, ya ce masa, "Samari, halama kai baƙo ne nan ko?"

Asadu ya ce, "I, yanzu na shigo, ɗan'uwana na nan bayan gari, na zo in samar mana abinci ne."

Tsoho ya nuna alamar yana jin tausayinsa, ya kama hannunsa ya ce, "Shigo ciki in sama maka abin da za ku ci, ka ji?"

Asadu ya ce, "To." Ya bi shi yana cewa, "Allah ya karɓa, Annabi ya gode, Allah ya sa muna cikin cetonsa."

Ya saurara bai ji tsohon ya ce amin ba, sai dai shiga su ke, suka wuce can ƙuryar gida, sai ya kai shi wani ɗaki ya kulle ya sa wata 'yarsa ta riƙa kiwonsa kamar yadda a ke turke rago. Ya ce kullum ta ba shi abinci sau biyu, da safe da dare, ruwa kuma sau biyu ko wace rana.

Ashe mutumin nan wani majusi ne, har Sarkin magiro ma a ke kiransa, watau Sarkin Tsafi. Ko wace shekara ashe abin da ya ke yi ke nan, sai ya kama Musulmi in watan zuwa tsauninsu na tsafi ya tsaya. To, Musulmin nan shi ya ke yankawa ya ba gunkinsa jinin. Sauran Arna masu yanka raguna na yi, masu shanu na yi, har da masu kaji. Amma shi Sarkin tsafin sai mutum ya kan ba gunkin ko wace shekara. To, yanzu watan zuwa bautar gunkin ya kusa, shi ya sa ya sami Asadu ya ajiye don wannan bukata. Ka ji labarin Asadu.

Amma Amjadu da ya yi jira har kusan rana faɗuwa bai ga ɗan'uwansa ya dawo ba, sai shi kuma ya biyo ya duba shi. Yana shigowa sai ya gamu da wani Musulmi, ya tambaye shi ko ya ga ɗanuwansa mai kama kaza a nan inda ya fito

Mutumin ya ce a'a, bai gan shi ba. Ya ce, "Hala ku baƙi ne.!"

Amjadu ya ce, "I."

Mutumin nan ya ce, "O, ai ba ku san cikin garin ba, akwai waɗansu Majusawa masu bauta wa w... . gumaka, in ya faɗa

hannun ɗaya daga cikinsu, kai da ganinsa sai wani ikon Allah. Abin da ya fi, kai ma kanka tun da ya ke magariba ta kusa, sai ka biyo ni mu je gidana ka zauna nan, kullum ka riƙa shiga gari neman ɗan'uwanka, in Allah ya sa kuna da rabon ganawa ku gana."

Amjadu ya ce, "To," Ya bi shi, suka tafi gidansa. Ashe mutumin baduku ne, Amjadu ya zauna nan yana koyon dukanci. Da rana kuma ya shiga gari neman Asadu, kullum sai kuka. Asadu shi kuma can kulle kullum hakanan. Ba wanda ya san inda ɗan'uwansa ya ke.

Ana nan wata rana Amjadu yana yawo sai ya gamu da wata karuwa. Da ta gan shi sai ta ce ya aure ta. Shi ko ya ce a'a, shi yaro ne, ina shi ina auren karuwa? Ga shi ko na fari ma bai yi ba tukun. Karuwa ta bi shi, ta ce ita ko ina ya shiga sai ta ga gidansu. Ba ta ko son kowa sai shi, lalle kuwa ya aure ta. Amjadu ya rasa yadda zai yi da karuwan nan, ko ina ya sa ƙafa sai ta mai da tata nan, shi ba dama ya kai ta gidansu yana jin kunya. Saboda haka ya kwashe ta suka yi ta yawo cikin gari, su bi wannan rariya su ɓulla wannan. Da ma shi dabarasa, in ta gaji da ragaita ta kama gabanta ta rabu da shi, ya je gida. In ta tambaye shi ina gida, sai ya ce, "Mun kusa dai" Ka san abu ga baƙo, yana cikin tafiya sai ya bi wata 'yar hanya ashe ba ta ɓullewa, iyakarta ƙofar wani gida. Suka tarar gidan kulle.

Karuwar ta ce, "Gidan ke nan? Ai ko mai kyau ne, yaran naka duk sun tafi yawo ne? Na ga gida kulle."

Amjadu ya rasa abin da zai ce, shi ba damar ya ce ba gidansa ba ne, tun da hanya ta kawo su, mutum ya taɓa mance hanyar gidansu? Shi ko ba ya son ya ce shi baƙo ne don bai san hannun wanda zai faɗa ba. Saboda haka ya ce, "I' ni na aike su."

Karuwar ta ce, "Im ba su dawo ba sai mu ɓalle marufin ƙofar in ga gidanka, don wata rana in dawo, ni dai im ba kai na aura ba, hankalina ba ya kwantawa."

Amjadu ya ce, "To, mu dakata dai su taho."

Karuwa ta tsaya jim, ba wanda ya zo, sai ta ɗauki dutse ta ɓalle ƙyauren, ta ce, "Ni ba zama na zo ba, daga dai in ga gidanka kawai don gaba." Sai ta kutsa kai ciki. Amjadu ya yi kamar ya ruga, ya dai kanne, ya yi kasada ya shiga, ko da ya ke bai san mai gidan ba.

Suna shiga sai suka tarar ga shimfiɗu nan an yi, ga abinci iri iri an sa bisa wani tebur, ga kujeru biyu an ajiye. Sai karuwar ta haye guda, ta buɗe kwanon abinci ta fara ci, tana cewa, "Ashe yaran naka aiki suka sha. Su suka dafa?"

Amajdu ya ce, "I." Ta sa ya zauna shi ma ya fara ci, duk

gabansa na ɗar ɗar, bai san ko gidan wane ne ba ya faɗa. Da karuwar ta gan shi sukuku, sai ta yi masa magana, ta tambaye shi lafiya?

Ya ce, "Lafiya lau, waɗansu kuɗi ne nawa yara suka zubar."

Suna nan sai suka ji wani tafe, Amjadu ya tashi ya tarye shi. Ashe Sarkin Fadan garin ne, wannan gidansa ne ya sa aka gina nan don shan iska. Abincin da na ce maka Amjadu sun tarar shi ya aiko da shi daga babban gidansa don yau zai zo nan shan iska.

Ko da Amjadu ya gan shi sai ya kwashe labarin karuwar duk ya gaya masa, ya ce in zai kashe shi ya kashe shi, da ma shi tun da ba ya tare da Asadu, bai kula ba ko ya mutu.

Sarkin Fada ya ce, "Ba na kashe ka. Yadda ka ce gidanka ne in na shiga ka ɗauke ni kamar baranka, ka yi mi ni faɗan abin da ya sa na fita, ka yi ta sa ni 'yan aike-aike."

Amjadu ya ce, "To."

Ko da ya koma Sarkin Fada ya bi, sai ya fara masa da faɗa, wai don me ya tafi yawo, an ce ya share gida ya tsaya ya fita.

Sarkin Fada ya durƙusa, yana ta tuba. Karuwar ta ce, "Ya fi kyau a ba shi kashi."

Amjadu ya ce, "Gaskiyarki, amma sai ya ƙara." Suka ci gaba da cin abinci. Sarkin Fada ya ɗebo masu ruwan wanke hannu, ya koma gefe guda, sai barci ya kwashe shi.

Ko da ganin ya yi barci sai karuwan nan ta ce sai Amjadu ya kashe shi, ita dai ta tsane shi, muddin kuwa yana nan gidan ba ta aurensa. Ta ce wai ya faye muni, kamar Amjadu kuwa ko yaron gidansa bai kamata a tarad da mummuna ba.

Amjadu ya ce shi ba ya kashe shi. Karuwa ta ce im bai kashe shi ba ita ta kashe shi. Ta tashi ta ɗauki takobi za ta sare shi, sai Amjadu ya karɓe takobin, ya ce ta bari, ya sare shi da kansa. Ta miƙa masa, sai ya ɗauke kanta. Ya ta da Sarkin Fada ya gaya masa abin da ya faru duka. Sarkin Fada ya yi mamaki, ya ce sai su naɗe ta cikin tabarma, shi da ya ke mutumin gari ya ɗauka cikin daren nan, ya kai ta cikin teku ya jefa. Amjadu ya ce, "To." Ya tashi ya taimake shi, suka naɗe karuwa cikin tabarma, sa'an nan ya sallami Sarkin Fada, shi ko ya koma gidan da ya sauka na baduku.

Da dare ya yi Sarkin Fada ya ɗauki karuwa ya nufi teku. Ashe Alƙalin garin na can, ya je shan iska da dare. Ko da ya ga Sarkin Fada sai ya ce, "A'a, Sarkin Fada! Ina za ka da wannan kaya cikin dare?"

Sarkin Fada ya rasa abin da zai ce. Alƙali ya matsa kusa, ya ce sai ya ga abin da ya ɗauko. Da ya ga mace ce matacciya sai ya ce, "A a a, Sarkin Fada! Ashe har ka fara kashe mutane haka kana

ƙwace dukiyarsu? Da ma na san arzikin nan naka ba banza ba." Da ya tashi bai zame ba sai gidan Sarki, duk ya kwashe labarin Sarkin Fada ya gaya masa. Ko da Sarki ya ji sai ya aika aka kira Sarkin Fada, ya tambaye shi, bai yi ko musun ƙarya ba, don ba dama.

Da gari ya waye sai Sarki ya sa Dogarai suka banƙare Sarkin Fada, aka tafi da shi kasuwa za a sare kansa. Mai yekuwa kuma ya shiga gari titi titi, yana faɗa wa mutane abin da Sarkin Fada ke aikatawa, da kuma yadda aka same shi, da hukuncin da Sarki ya ce a yi masa. Yana cewa ba a ɗauke wa kowa ba ya fito kasuwa ya gan shi don ya zama gargaɗi ga na baya.

Amjadu na gida yana ɗinkin takalmi, ya ji shela, sai ya san abin da ya faru. Ya watsad da kayan ɗinkin, ya rugo kasuwa, ya tarar har Sarki ya fito, an kewaye za a sare Sarkin Fada. Sai Amjadu ya kutsa ya tarad da Sarki ya faɗi ya ce, "Sarkin Fada ba shi da laifi, don ba shi ya kashe ta ba, ni ke da laifi, ni za a kashe!"

Sarki ya tambaye shi labarinsa, ya kwashe duka ya faɗi, har ya kawo inda ya gamu da matan nan, da yadda ya kashe ta. Da Sarki ya ji haka sai ya sa aka saki Sarkin Fada. Ya sa mutane suka watse, ya yi ta mamakin Amjadu, da kuma wannan alkawari da ya cika. Ya ce masa yana jin labarin Sarki Kamaruzzaman tuni, daga nan garin tafiyar wata biyu ne cur zuwa can, ba mugama ba cin zango. Sabo da jaruntakan nan da ya yi, da kuma labarinsu da ya ba shi tausayi, ga shi kuma ɗan Sarki, sai ya yi masa Wazircin garin. Dama dame ya fashe kan kaba, na da ya mutu. Sarkin Fada kuwa aka ƙara masa girma, don 'yancin da ya yi. Suka zauna nan da shi da Sarki da Waziri.

Sarki ya sa mutane kullum suna ta bin gari ko sa ga Asadu, ba su gan shi ba, don yana can kulle ƙuryar gidan Sarkin tsafi ɗakin awaki, ba mai zuwa wurin sai fa shi da 'yar, mai gadin yaron. Ka ji labarin Amjadu.

Amma Asadu kullum im Majusin nan ya kewayo sai ya yi masa bulala hamsin. Suna nan haka har wata uku, sa'an nan lokacin tafiya wajen tsafi ya yi, ya sa Asadu cikin akwati ya kulle, ya ɗauke shi ya kai bakin teku, ya sa cikin jirgi, suna shiri za su tashi sai ga manzannin Waziri, watau Amjadu, sun zo dubawa ko sa ga Asadu, don ko da ya ke shi hankalinsa kwance ne, duk da haka kullum ba ya rabuwa da kuka da aikawa ko ina ko a ga ɗan'uwansa. Aka duba mutane kaf, ba Asadu, suka dawo, jirgi ya miƙa. Yana tafiya cikin teku, sun yi kwana uku sai iska ta tashi, igiyoyin teku suka murɗa, sai aka kwashe jirgi aka tafi da shi can wani babban tsibiri inda ba hanyarsu ba. Suka tarar wata

Sarauniya ce Musulma wai ita Magiyanatu ke mulkin tsibirin.

Arnan nan sun san Sarauniyan nan Musulma ce, sabo da haka da ta tambaye su inda za su sai suka ce su masu sayad da bayi ne, sun sayad da waɗanda suka kawo duka, sai guda ɗaya. Suka fid da Asadu suka nuna, suka ce, "Amma wannan ba mu sayad da shi."

Sarauniya ta dubi Asadu, ta ga hasken musulumci a goshinsa, ta ga kuma lalle ba ɗam banza ba ne. Sabo da haka ta yi ta yi su sayar mata da shi, suka ƙi. Sai ta dubi Asadu, ta ce, "Ka iya rubutu?"

Asadu ya ce, "I, Allah ya ba ki nasara."

Ta sa aka kawo masa alƙalami da tawwada, ya rubuta mata labarinsa duka. Da ta karanta ŝai hawaye suka zubo mata. Ta dubi Arnan nan, ta ce, "Na nufe ku da ku sayar mini da yaron nan, kun ƙi. To, ku je an ƙwace muku." Masu jirgi suka je masaukinsu, suka yi baƙin cikin rabuwa da Asadu. Ba su san abin da za su yi ba, ko su koma, ko su ci gaba.

Sarauniya ta ba shi abinci irin na asali ya ci har ya ƙoshi. Suka zauna, yana ta ba ta labarinsa duka. Da magariba ta yi Sarauniya ta nuna masa ɗakin da zai riƙa kwana, kafin ya huta ta mai da shi garinsu. Ya shiga ya kwanta. Yana nan kwance sai ya ji duk jikinsa ya yi tsami. Ka san wanda ya yi wata shida cikin ɗaki, ya yi kwana uku cikin akwati, ba abin da ya ke so irin miƙe ƙafa. Sabo da haka ya tashi ya fita ƙofar gida, yana miƙe ƙafa sai ya ga wata 'yar rijiya, ya zauna gindinta ya sha iska. Abinka da gajiyayye, sai barci ya share shi. Yana nan yana barci bakin rijiya, ashe kuma Sarkin tsafi ya fito daga masaukinsu yana yawo yana ta baƙin ciki, yana dube-dube ko Allah ya ba shi ko ɗan jariri su sace su gudu da shi, sai ga wani na barci. Bai san ko wane ne ba. Sai ya kira 'yan'uwansa suka ɗauke shi a hankali, suka sa cikin akwatin da suka fidda Asadu daga gare shi, suka kulle, suka haye jirginsu, suka gudu cikin daren nan.

Da Asadu ya farka ya ji shi cikin akwati kuma, sai ya yi salati. Ko da Sarkin tsafi ya ga Asadu ne sai ya yi ihu, ya ce sai shi kafiri ɗan kafiri, jikan kafiri. Wuta ta aure shi, ya aure ta. Ya dubi yan'uwansa, ya nuna musu Asadu ya samo, ya ce ai tun da ya yi niyyar sai ya ba gunkinsa jinin Asadu, ko ina ya shiga sai ya dawo. Ya ce shi tsafi gare shi ba haye bane gado ne. Suka haye jirginsu, suka gudu cikin daren nan.

Amma da gari ya waye sarauniya ta nemi Asadu ba ta gan shi ba. Ta tambayi masu jirgi, aka ce ai tun da dare suka miƙa, sai ranta ya ɓaci, ta san ba makawa su suka sace shi. Sai ta yi salati, ta yi shirin yaƙi ta bi su. Da ya ke jirginta ya fi nasu sauri, can

zuwa rana tsaka suka hange ta tafe. Da ma ko sun koma baya ne can wajen garin da suka fito, watau inda Amjadu ke Wazirci, don su ɗauko hanyar daga inda suka sani. Ko da suka hange ta tafe, sai suka ji tsoron in ta ga Asadu tare da su za ta halaka su ne kaf. Sabo da haka suka kama Asadu suka tura cikin teku, wai don in ta zo ta duba ba ta gan shi ba, ba ta halaka su ba.

Cikin gidi-gidin jefa shi har suka tura duk da akwatin da ya ke ciki. Allah ya ba Asadu sa'a, ya kama akwatin, iska ta yi ta tura shi da sauri. Can zuwa magariba, bai san yadda aka fara ba, sai ga shi garin da ɗan'uwansa Amjadu ke Wazirci. Ka san fa bai san abin da ya faru gare shi ba, balle ya nemi gidan.

Da ya ga magariba ta yi, yana tsoron kada ya shiga garin da magariba ya faɗa hannun wani mugun kuma, ya ruɗe bai san ma ko wane gari ba ne. Yana nan yana shawarwari, sai ya ga ba abin da ya fi sai ya sa akwatinsa cikin wani kabari daga kaburburan da ke ƙusa da shi, ya shige nan ya kwana, in gari ya waye ya isa cikin gari, abin da Allah ya ƙaddara kuma ikonsa ya fi da hakanan. Ya shige ya kwanta. Ka ji labarin Asadu.


Amma Magiyanatu da ta tarad da Arnan nan, sai tà tambaye su Asadu, suka duƙa suka ce, "Allah ya ba ki nasara, ai tun da kika ƙwace shi rabuwarmu da ganinsa ke nan. Ta ina ma za mu bi mu gan shi kuma, kin shiga da shi gidanki?". Ta sa aka bincike kayansu duka, ba a ga kowa ba. Sabo da haka ta koma gida, ta sake shiri, ta ce in aljannu suka ɗauke shi im mutane ne suka sace shi, muddin yana numfashi inda ya ke duka cikin duniyan nan sai fa ƙarfinta ya ƙare garin nemansa. Ta shiga nema ko ina, da kanta ta shiga duniya da mutanenta. Ka ji labarin wannan Sarauniya.

Amma Asadu, da gari ya waye sai ya fito daga cikin kabarin. Yana fitowa sai ga wani dogari ya dawo daga gadi a matsayar jirgi, don Waziri Amjadu ya sa kullum a yi ta gadi, ko wane jirgi zai wuce a yi cajinsa ko a ga Asadu.

Ko da dogari ya ga Asadu, duk ya yi baƙi, kamarsa ta sake da yadda Waziri ya bayyana musu, sai ya yi tsammani ɓarawo ne. Ya buga masa tsawa, ya tambaye shi inda ya fito, tsoro ya kama shi, ya kasa iya ba da ko jawabi. Dogari bai tsaya wata-wata ba sai ya buga masa ankwa, ya aza masa akwatin nan da ya biyo shi cikin teku, yana tsammani sato shi ya yi. Ya yi macinsa zuwa gidan Sarki yaran gari suka bi suna "Biri, biri!"

Da Sarki ya fito, dogari ya nuna masa Asadu, sai ya ce a tafi da shi ofishin Waziri, ya rubuta sunansa, ya aika da shi wajen Alƙali a tuhunce shi, a ji inda ya samo akwatin nan, da kuma abin da ya sa shi kwana cikin kabari da ransa.

Ko da aƙa shiga da shi wajen Waziri, suka yi arba da juna, ko wannensu sai ya faɗi ya some, mutane ba su san abin da ya faru ba. Aka zuba musu ruwa suka farfaɗe. Ko da dogari ya ga haka sai ya yi wuf ya kwance ankwa.



To, yanzu fa yaya ka ke tsammani labarin farin ciki tsakanin Amjadu da Asadu? In na bar ka ma da abin da ranka ya ƙulla, iyakar farin cikin nan ya ma isa, ba sai na faɗa maka ba. Ta ishe ka ma saboda murna Sarki ma da bai gama kome da su ba sai da ya sa aka yafe wa duk 'yan sarƙan garin, aka sake su. Dogarin ko ma da ya gan shi, alherin da aka yi masa, kai, abin dai sai a yi shiru!

Ana nan ana cikin wannan murna, ana goce tambura, sai aka ga ƙura ta taso ta toshe sararin sama, Sarki ya ce Waziri Amjadu ya je ya dubo, in yaƙi ne a shirya. Ko da ya isa, aka kai shi ga sarki, sai ya tarar ashe ma ba Sarki ba ne, wata Sarauniya ce wai ita Magiyanatu, watau waccan da ta kuɓutad da Asadu daga hannun Sarkin tsafi.

Da Waziri ya tambaye ta abin da ke tafe da su, Magiyanatu ta ce ta zo neman wani saurayi ne, mai kama kaza mai kama kaza, ana ce masa Asadu. In yana nan a ba ta shi ta koma, in ko kun ƙi, yanzu na lahira na fin ku jin daɗi.

Waziri ya tambaye ta abin da ya sa ta ke nemansa, ta gaya masa labarin da ya gaya mata sa'ad da ta kuɓutad da shi. Ta ce shi ya sa ta ke so ta mai da shi garinsu. Ta dubi Waziri, ta ce, "Kai, ai ko kun yi kama. Ba don ka fi shi ƙiba ba ma sai in ce shi ne."

Waziri ya yi murmushi ya ce, "Ai ni ne wansa da ya gaya miki. Shi ko yana nan gari, yau ya iso." Sai ya wuce gaba, ɗimbin yaƙin Magiyanatu na biye, har gari wajen Sarki. Aka gaya masa abin da ke tafe da ita. Asadu ya zo, suka rungume juna suna murna. Al'amari ya komo sabo.

Ana nan ana ta shagali kuma, can zuwa rana tsaka sai aka hangi ƙura ta danno gabas da yamma, sai ganguna ke tashi. Sarki ya sa Waziri Amjadu ya je ya dubo. Magiyanatu ta ce, "A dubo me? Ku bari ko wane Sarki ne ya iso. Ko da wacce ya zo ya gamu da gamonsa."

Sarki ya ce, "A'a, a je dai a dubo." Waziri ya koma da hammadanci. Da isa aka kai shi ga Sarki, ya faɗi ya yi gaisuwa. Dawaki ga su nan bilahaddin, sai ka ce fari. Da ya tambayi Sarkin nan abin da ke tafe da shi, sai Sarki ya ce, "Ni ne Sarkin Birnin Sin, na taho neman 'yata ce wadda a ke kira Badura, tana aure da Kamaruzzaman ɗan Sarki Shahruzzaman. In tana nan ku ba ni ita ku huta. In kuwa kun ƙi, yanzu garin nan da abin da ke cikinsa duka su koma turɓaya. Yau na yi shekaru da yawa ina nemanta, ban gan ta ba."

Waziri ko da ya ji haka sai ya fashe da kuka, don ka san fa kakansa ne. Ya gaya masa shi jikansa ne, ya kwashe labari duka ya gaya masa. Suka yi ta al'ajibi, Sarki ya ce, "Na yi tsammanin haka, ko da na gan ka sai na ga kun yi kama da Kamaruzzaman." Suka shiga gari. Da mutane suka ji labarin Sarkin Sin ne, farin ciki kuma me za mu kamanta shi? Ai babu.

Ana nan gari ya cika da dawaki, na Sarkin Birnin Sin ma har a tafukka a ke ɗaure su. Sai aka hangi wata ƙura daga arewa. Sarki ya ce wa Waziri, "Koma, Allah ya sa yau ranar sa'a ce." Waziri ya tafi, aka kai shi ga Sarki. Ko da suka yi arba, sai su duka suka kasa magana. Ashe ubansa ne Kamaruzzaman da tsohon Sarkin Ebone, watau uban Hayatunnufusi uwar Asadu. Da hauni ya gaya musu bai kashe su ba, shi ne suka fito nemansu. Waziri ya tashi Sarki Kamaruzzaman ya nuna masa raƙumin da iyayensu mata, watau Badura da Hayatunnufusi, su ke bisa. Ba a cewa murna wannan wuri. Ya wuce gaba, suka isa gari Asadu ya ga Kamaruzzaman, ya ga Hayatunnufusi uwarsa da Badura. Sarkin Birnin Sin shi kuma ya ga 'yarsa Badura. Wayyo Allah! Murna a wannan wuri, faɗi ƙauyanci.

Ana nan, gari ko ina ƙaɗe-ƙaɗe da waƙe-waƙe da tambura abin

ba mai jin na wani, sai aka hangi ƙura ta toshe sama, duk har ta rufe rana. Aka aiki Waziri Amjadu ya dubo kuma mene ne. Sai aka tarar Sarki Shahruzzaman ne, watau kakansu Uban Kamaruzzaman, ya sami labari bai mutu ba, sun bar rigunansu cikin jini don a daina nemansu ne, shi ya sa ya biyo nemansa cikin duniya.

Da ya ga Amjadu sai ya ce, "Kai ko samari, ko ina ka fito na ƙi, jinina ne."

Waziri Amjadu ya bayyana masa ko shi wane ne. Ɗan tsofo ya some don murna. Suka isa gari. Kamaruzzaman ya ga ubansa Shahruzzaman. Badura da Hayantunnunfusi suka ga surukinsu. Amjadu da Asadu suka ga kakanninu. Wayyo Allah! Wohoho! Wani al'amarin ya fi gaban a bayyana, sai a yi kurum. Garin da Sarakunan duniya biyar suka taru, duk ko taron farin ciki. To, wurin mutun ya ce zai bayyana wani abu, ai ka san kifin rijiya, wanda bai san abin da a ke kira duniya ba, sai ye ce zai ƙaryata mutum a wofi. Ba abin da ya fi sai dai a bar kaza cikin gashinta.

Da aka yi kwana bakwai ba barci garin, ko kana son yi ma ba dama, don tambura da kaɗe-kaɗe da bushe-bushe. Kowa ya ga taron nan sai ya ce iyakar duniya ke nan, ba wani mahalukin da ya rage a wani wuri, duk sa taru nan.

Da ranan nan ta dawo, watau kwana bakwai ke nan yadda na faɗi yanzu, sai suka taru, Shahruzzaman ya ba su labarin wahalar da ya sha wajen neman Kamaruzzaman. Sarkin Birnin Sin ya ba da labarin shi kuma abin da ya sha wurin neman Badura. Kamaruzzaman kuma da shi da surukinsa Sarkin Ebone, uban Hayatunnufusi, suka ba da labarin wahalar da su kuma suka sha gun neman Amjadu da Asadu. Sarauniya Magiyanatu ta ba da'yar wadda ta sha kan Asadu. Amjadu kuma ya ba da wadda suka sha da Asadu, da kuma abin da suka yi da karuwa, har ya yisarauta. Kowa ya yi zugudun don tausayin wahalar da suka sha. Asadu kuma da ya fara faɗin abin da ya sha na wajen uƙuba tun daga ran da ya rabu da Amjadu har ran da ya sake gamuwa da shi makon jiya, sai kowa cikin Sarakunan nan ya fashe da kuka don tausayi.

Sarkin garin nan ya sa Dogarawa suka kamo Sarkin Tsafi, za a tsire shi, ya yi Kalmar Shahada ya ce ya musulunta, nan take ya ƙone kayan tsafi, aka ƙyale shi, ya kama tafarkin Fiyayyen talikkai.

Da aka yi kwana bakwai ana ba da labarun aka ƙare, aka ƙara hutawa waɗansu kwana bakwai, watau ashirin da ɗaya ke nan, sai duk Sarakunan nan biyar suka nufi garin da Sarauniyan nan Magiyanatu ke mulki. Aka tara Sarakunan ƙasar aka yi biki, ta

auri Asadu. Ta sa wani wakilin ƙasar, ita ko ta bi shi suka sake ɗungumawa ƙasar Shahruzzaman, aka naɗa Ƙamaruzzaman Sarki maimakon ubansa da ya tsufa. Suka zauna nan da Badura da Hayatunnufusi.

Aka kuma tafi Birnin Sin, aka naɗa Amjadu Sarki, don ka san shi ne ɗan Badura, watau jika ya ke ga Sarkin Birnin Sin. Aka koma Ebone, aka naɗa Asadu Sarki don ka ga shi kuma fa ne ɗan Hayatunnufusi, watau 'yar Sarkin garin. Ya zauna nan da shi da matarsa Sarauniya Magiyanatu. In sun yi wata uku nan su je can su yi wata uku. Sarkin nan da Amjadu ya yi wa Wazirci shi kuma ya ba shi 'yarsa aure. Suka yi zamansu nan, duniya ta komo hannunsu. In wannan ya yi nishaɗi, ya shirya ya tafi garin wannan yawo.

Allahu Akbar! Duniya na inda ta ke, masu cinta kuwana can na murtsukarta. Ya Allah, domin alfarmar Annai binka, ka sa ni cikin waɗanda ba za su mutu ba sai sun ce duniya, im bar wa na baya abin labari.

Waziri ya dubi Sarkin Sirika, ya ce, "Allah ya ba ka nasara, ka ji labarin Amjadu da Asadu. Naka maganin a kwaɓe ka. Manya masu duniya, Sarakai masu yin abin don kansu daga gare ki, sarauta, burin duniya ya ƙare."

Mutane suka yi tafi, suka ce, "Tun da ka ke ba da labari ba ka taɓa ba da mai daɗi irin wannan ba. Kai, duniyan nan ma ba wanda ya taɓa jin labari mai daɗi irin wannan. Da ashe ga labari mai daɗi za mu watse ba mu ji ba."

Sarkin Sirika ya ce, "Ga labari har labari, amma ya so ya rage wuri guda. Ka tara mini Sarakuna biyar gari ɗaya, ka ce an yi kaɗe-kaɗe da waƙe-waƙe, ga kuma Ƙamaruzzaman ya gaji gidansu, Amjadu ya yi sarauta, Asadu shi kuma ya yi, amma duk ban ji waƙar ko Sarki ɗaya ba daga cikinsu. To, ina zan san fasahar waɗansu ƙasashe, kana ko yi da mu a kaikaice kana ce mana kifayen rijiya? Na ko gaya maka ba abin da ke ba ni raha illa ka ƙare labari da waƙa don daɗin muryarka."

Sai Waziri Aku ya kaɗa fiffike, ya ce, "Yanzu ka shata. Zan gaya maka waƙar Amjadu da Asadu su kaɗai, in na ce zan ƙara waɗansu sai abin ya ƙi daɗi." Da ma abin da Sarkin Sirika ke so ke nan, don ya san muryar Waziri Aku ko kare ba ya ci ba don rashin daɗi, ya kan so ya takale shi don ya yi dariya.

Waziri Aku ya gyara murya, ya ce, "Ta Amjadu, Sarkin Birnin Sin zan fara, daga nan kuma in ci gaba da ta Asadu ƙanensa." Ya yi tari ya zubad da yawu, ya karkace kai, ya fara:

"Bismillahi na fara,
Za ni yabon gwarzo,
Wa zai fushi da yin Allah?
Annabi, kai ya so.
Birnin Sin ku zo wurin caffa,
Mai abu ya dawo.
Na Hayatunnufusi wan Asadu,
Alheri ya danno.
Mai hassada ya je ya mace,
Hannummu a romo.
Tattake mu ɗau shirin yaƙi,
Ba mu barin sanƙo.
Turai, Faransi, har Jamus,
Kowa sai ya zo.
Mutanan Masar ku bar kawa,
Nan ma ma raɓo.
Sudan ku tsoràci mai nasara,
In kun ƙi ya taso.
Amjad, dangane ka ɗau himma,
Kome ka yi sabo.
Babba, dogare wajen Allah,
Kome bunƙaso.
Saura guda mu je mu haji,
Daɗa ka zama gwarzo.
Ya Allah, ka dubi Sarkimmu,
Ka ba shi halin tsoho.
Alo, alo, alo Amjad,
Alo, gwarzon gwarzo!

Allah ya ba ka nasara, ka ji ɗaya daga cikin waƙoƙin Amjadu Sarkin Birnin Sin. Karkaɗe kunne kuma ka ji ta Asadu, Sarkin Ebone."

Sarkin Sirika ya ce, "Zaune ma na ke, amma na rantse har da rawanin Sarki Abdurrahman ɗan Alhaji, tun da ka ke ba ka taɓa rera mai daɗi irin wannan ba. Ga murya, ko mu mutane ma shafa maka lafiya!"

Waziri Aku ya ji daɗi an yabe shi, ya karkata kai kuma ya fara waƙar Asadu. Kaji suka watse, suna tsammani korarsu ya ke yi.

"Ku saurara, ni zam fara ambaton Sarki,
Duk mai so ya ji.
Ka ɗau himma, babba, ɗan'uwan su Amjad,
Kwab biɗi wasa ka ƙi.

Ka miƙe ƙafarka, ka muskaki duniya,
  Yau kai ɗai ke agaji.
Haba Asadummu, ina ba ka shawara dai,
  Wadda ta ka fid da ni.
Akwai wani gaula nan yamma-yamma,
  Kar ka sake ka yi wasa da shi.
Tun ba ka zo ba ya ke so a ba shi mulki,
  Mu ko sai mun ka ƙi.
Gaya masa mulki ba jaura ce ba,
  Gadon sauna, balle ya ci.
Ga ka talakka tiɓis ɗan talakka,
  Ban da kiɗa me ya dace ka yi?
Haba sauna, don Allah ku dubi wandonai,
  Ho ɗa ja'iri!
Ka saurara, babba ɗam Badura,
  San da sani mu ba mui da shi.
Ciki ya sani in dai ya cika shi,
  Ba saura daɗa sai izgili.
Aduwu'llahi, Aduwu'rrasuli! Ho gaula,
  Babban zalumi!
Ya Allah, ka yi jin ƙai gare mu,
Ya Allah ka yi jin ƙai gare mu,
Ya Allah ka yi jin ƙai gare mu,
  Don alfarmar Aɗɗahiri."

Waziri Aku ya dubi Sarkin Sirika, ya ce, "Allah ya ba ka nasara, shi kuma ka ji tasa."

Sarakuna suka ce, "Kai, wannan ita ma ba baya ba. Amma wane ne a ke zagi a kaikaice, ba a faɗin sunan mu ji?"

Waziri Aku ya ce,s "Madawakin garin, da ai shi ya so a ba shi sarautar da aka bar shi wakilci sa'ad da aka je neman yaran."

Sarkin Sirika ya ce, "Wannan labari ya fi kome daɗi. Amma yana ba ni mamaki yadda Sarakunan nan biyar suka taru gari guda duk a rana ɗaya, ba ko da sun ƙulla za su yi haka ba."

Waziri Aku ya ce, "Madawakin garin, da ai shi ya so a ba shi mutum ya ba da labarinsa, sai ka yi binciken abinda za ka kawo ka soki wani abu a ciki. Labari ne na ba ka, ba tarihi ba, balle a ce ana neman gaskiya ciki. Kuma ma mene ne nawa? Na gaya muku tun da fari cikin Alfu laila ya ke, Haziƙ shi ya fara."

Sarki Abdurrahman ya ce, "Allah ya huci zuciyarka, aku kuturu."

Aku ya ce, "Allah ya ba ka nasara, ni fa ba na son 'aku kuturun' nan. Yaya mutum lafiyarsa ƙalau a riƙa kira masa cuta?

Dubi yatsuna. Abin da na tabbata yanzu ko cikin mutane samun mai kyau kamarmu, sai an tona. Mu ƙananan kyau gare mu sai an daɗe ana kallommu za a ga ba wajen kushewa. Mun dai gode wa Allah, ko Haziƙ, da ya halicce mu kyawawa. Tubarkalla, bismilla!"

Mutane suka fashe da dariya, aka watse.

Kashegari yau kuma da aka taru sai Waziri ya dubi Haziƙ, ya ce, "Bismilla."

Haziƙ, ya ce, "Tun jiya na gaya muku ni labaruna sun ƙare, to, mene ne kuma za a dame ni?"

Waziri Aku ya ce, "Ai, Allah ya ba ka haƙuri. To, saurara ka ƙaru." Sai ya ci gaba:

# Kyale Maƙetaci Ya Yi Ta Halinsa, Kome Ta Jima Zamani Na-Nan

A arewa akwai waɗansu mutane su biyu suna zaune a ƙauye guda, ɗaya ana kiransa Sidi, ɗaya kuma Tanko. Ko da ya ke suna maƙwabtaka da juna ba ta inda halinsu ya gamu, domin Sidi dai Allah ya yi shi mai haƙuri ne kamar ƙasa, sa'an nan ga kyauta da tausayi, abin ba a magana. Amma Tanko duk inda ja'iri ya kai ya wuce nan, ga dai ƙeta sai ka ce dogari, rowa kuwa ko Zumbuli ya san da shi.

Suna nan zaune dai da daɗi ba daɗi, sai wanda ke kusa da su kaɗai ya sani. Iyakar cunkusawa ba irin wadda Tanko ba ya yi wa ɗan talikin nan, amma duk da haka Sidi ba ya kula, sai in abin ya damė shi ya nisa ya ce, "Mahaƙurci mawadaci."

Sidi yana da wani ingarman akawali wanda duk garin ba kamarsa. Tanko kuwa ban da wani gurgun jaki na matarsa ba shi da ko fiffike. Ba abin da ya tsone wa Tanko ido irin ya ga Sidi ya hawo dokin nan yana tafe yana cinsa, sai ya yi ta riya yadda zai yi ya sace dokin nan ya haye ƙasa, ya kai cikin Faransi ya sayar.


Ana nan, ran nan da Tanko ya ga Sidi ya hau dokinsa za shi wani ɗan ƙauye ya gai da wata goggonsa da ba ta lafiya sai ya shirya ya bi shi baya. Ya yi shawarar ya kashe shi ya ɗauke dokin ya gudu, ya ga watakila a gane. Ko kuma ma ba a ganewa, in dai na a gwada ƙarfin tuwo ne ba abin da zai ɗiba a gun Sidi. Saboda haka ya sake dabara, ya sami'yan tsummokara ya sa, ya shafe fuskarsa da shuni, ya ɗaure ƙafarsa da tsumma kamar tana ciwo, ya tsinto wata tsohuwar malfa da doguwar sanda ya ajiye, ya kwashe kayayyakinsa masu kyau ya kai can gaba nesa ya ɓoye. Shi kuwa ya dawo baya, yana doddogara sanda kamar ba ya iya takawa sosai.

Can sai ga Sidi ya dawo kararaf kararaf. Da Tanko ya gan shi, ya yi masa magana a mararaice ya ce, "Bawan Allah ka ji ƙaina ka sa ni a kuturi, amosani na ke yi. Tun da asalatu na fito Hamis, amma ka ga har yanzu ban isa gari ba. Na nemi inda zan yi barar abinci na rasa, rabona da sa hatsi baka tun jiya da magariba."

Da Sidi ya ji haka sai ya ji tausayinsa, ya sauka, ya sa hannu a

aljihu ya kawo taro, ya ce, "Ga sadaka saboda Allah im mun je gari ka sayiabinci." Ya kuma ciccibe shi ya ɗora bisa doki, shi kuma zai taka ya hau sai Tanko ya buga wa doki ƙaimi ya zabura da gudu. Da ya ga ya yi wa Sidi tazara, ba yadda zai yi ya kama shi, sai ya zame doki ƙu ƙu, ya waiwayo ya ce, "Ni ɓarawo ne, da ma lafiyata lau, dokinka dai na ke so in sace, na kuwa ci nasara, ka ga kuwa tafiyata!"

Sidi ya ce, "Don Allah tsaya ka ji magana ɗaya, in ka tafi kada ka gaya wa mutane wannan dabarar ce ka yi ka same shi."



Tanko ya ce, "Me zai hana im faɗa wa 'yan'uwana, su yaba hi bisa ga wannan wayo da na yi maka?"

Sidi ya ce, "A'a, ba wani abu na ke gudu ba sai idan ka faɗi, mutane suka ji, nan gaba ko sun ga gajiyayye na gaskiya a hanya, ya nemi taimako gare su, ba za su taimake shi ba, don za su yi tsammani kowa irinka ne. Ka ga hanyan nan taka za ta kashe wa gajiyayyu kasuwa, har a rika barinsu suna halaka sabo da tsoro."

Tanko ya ce, "Zancen banza! Ina ruwanka da wannan?" Ya zabura ya tafi. Ya kwashe kayansa masu kyau ya sa ya watsad da

tsummokaran. Kafin magariba ta yi ya ƙetare ƙasa. Da ma garin kusa da kan iyaka ya ke. Ya sayad da doki, ya sayo shanu goma sha ɗaya ya koro. Bayan kwana biyar ya iso gida, ya ɗaure shanunsa, ya yi ta kiwo. Mutane suka yi ta mamakin yadda ya yi arziki gaba ɗaya haka. Amma Sidi, tun da ya ji muryarsa ran da ya sace masa doki, ya san shi ne. Da ya dawo gida ya iske ba ya nan, ya ƙara tabbatarwa, amma duk da haka bai ce wa kowa kome ba.

Ana nan, ran nan kuma sai wani kawun Sidi ya kawo shanunsa guda goma, ya ce Sidi ya yi masa kiwo kafin ya dawo daga wani biki da aka gayyace su. Sidi ya ɗaure shanun nan gidansa.

Da Tanko ya ga Sidi da shanu sai ya fara ganin ƙyashi. Ya tafi gidansa, ya ce, "Don ka ga ina da shanu, kai kuma don son gasa ka sayo. To, sai ka yi hankali kada ka kuskura ka bari ɗaya daga cikinsu ya shiga gonata ya ci ko ganye ɗaya daga tstasen gambar da na bari don nawa su ci nan gaba. Ka san da sani fa, in na ga sanka cikin gonata lalle in kashe shi."

Sidi ya ce, "Na ji, Allah dai ya kyauta." A kwana a tashi ka san yau da gobe sai Allah, ran nan da dare sai sa guda daga cikin shanun Sidi ya kucce, ya shiga gonar Tanko ya fara cin tsatsen gamba. Da matar Tanko ta ji motsi a gona ta tashi ta duba, ta hangi ashe sa ne, sai ta zo ta ta da mijinta, ta ce, "Ka san dai Sidi ya raina ka. Ga abin da ka ke masa kandako kansa ya faru. Ka ce kada ya bar shanunsa su ci gambarka, ga shi can ya saki ɗaya da gangan, duk ya cinye gamba sarai."

Ko da Tanko ya ji haka, sai ya tashi da fushi, ya ɗauki baka da kwari ya fito gona, ya dubi san ya ɗirka masa kibiya, ya faɗi ya mutu. Da safe ya zo ba kunya ba tsoro, ya gaya wa Sidi abin da ya aikata.

Sidi ya ce, "Kash, Allah ya tsayar nan!" Ya sa aka ja sa, aka kai daji aka yar.

Mutane fa da matarsa suka dame shi lalle sai ya yi ƙara. Ya ce ba ya yi, mahaƙurci ai mawadaci.

Matarsa ta fusata, ta ce, "Ni ko kai ka ƙyale, sai na san yadda na yi na rama mana. In kai kana taƙamar haƙuri ne, ai ni ba na iya jure wa maganganummu na mata, a ce mun ƙyale don muna jin tsoro."

Sai da matan nan ta Sidi ta bari an yi kamar kwana goma duk am manta da wannan, sai ta tashi ran nan da dare ta laɓaɓa garken Tanko, duk ta sako shanun ta kora su cikin gonarsa, suka yi ta cin gambar da ya ke faɗa. Da matarsa ta ji motsi sai ta tashi ta duba, ta hangi shanu fari fat cikin gona suna cin gamba, tana tsammani na Sidi ne. Sai ta ta da mijin, ta ce masa, "Ahayye,

ayyururui! Ashe gobe ana shirin yin danja."

Tanko ya ce mata, "Mene ne? Lafiya? Wace irin danja?"

Matar ta ce, "Wai don ka kashe wa Sidi ɗam maraƙi kwanan baya, shi ya sa yau ya yi hushi ya sake su duka su cinye gambar, in ya so abin da za a yi duka a yi. Ka san wannan raini da ke tsakaninku da Sidi ba shi da iyaka."

Sa'ad da mijin ya ji haka sai ya fusata, ya ɗauki kwari da baka ya shiga gonar, duk ya harbe shanun suka mutu. Ya koma gida ya ce wa matar, "Na kashe su duka, gobe ko kome ta tafasa ta ƙone. Na san dai ba a kashe ni don na kashe sa."

Matar ta ce, "Bari ta maganar kisa ai ko wata ƙatuwar harara ba a yi maka ba. Da fa ba ka yi masa kandako ba ne tun da fari."

Gari na wayewa sai Tanko ya tafi wajen Sidi, ya ce, "Na kashe shanunka duka da ka bari suka shiga mini gona. In da za ka kai ni kuwa, duk je ka ka kai ni."

Sidi ya ce, "Assha! Amma ni nawa shanun duka suna nan ɗaure. Yanzu na fito can, hala na wani ne. Mutanen duniya ba su jin magana."

Tanko ya dawo gida, ya tafi garkensa ya tarar ba sa ko ɗaya. Ya dafe kai, ya yi salati. Matar Sidi ta fito, ta ce, "Ni na sake su, je ka kai kuma, duk inda za ka kai ƙara ka kai."

Tanko ya rasa abin da zai ce, sai ya faɗa matarsa da tsina, yana cewa ita ta sa ya kashe su. Ya hau mata da bugu. Abin ƙarar kwana, ya shure ta a ƙahon zuci, ta faɗi ta mace. Dogarawa suka kama shi aka je da shi gidan Sarki, aka tambaye shi ya faɗi dalilin da ya sa ya kashe matarsa, duk ya kwashe ya faɗi.

Waziri ya ce, "Unguwarmu fa ya ke." Ya dube shi, ya ce, "Kai da na sani ba ka da ko kaza ina ka sami shanu goma sha ɗaya?"

Tanko ya ce, "Iye, na'am, Allah ya gafarta malam, ni Wallahi ba ni su aka yi."

Da Sarki ya ga alamar ba gaskiya cikin maganarsa, ya sa dogarawa su tambaye shi. Suka fa same shi, sai sakam masa bulala su ke kamar ruwa, har ya faɗi gaskiyar yadda ya ƙwace dokin daga wurin Sidi, da kuma abin da Sidi ya ce masa duka da za su rabu.

Sarki ya sa aka kira Sidi, ya tambaye shi inda ya yi da dokinsa. Sidi ya kwashe labari duka ya faɗa wa Sarki. Aka sami abin da ya faɗi ya yi daidai da na Tanko. Sarki ya sa masa albarka. Nan take Sarki ya naɗa shi ma'ajin Garin, da ma na da ya mutu, ana neman wani mara cin amana a ba shi, an rasa. Aka kai Tanko kurkuku, aka shiga hidimar naɗin Sarauta. Da aka gama, zuwa azahar Sarki ya sa aka zo da Tanko. Sarki ya tashi da kansa, aka ɗunguma zuwa kasuwa har da Ma'aji Sidi, aka yi gangami,

mutane suka taru. Sarki ya ce wa Tanko ya faɗi abin da ya yi wa Sidi tun daga farko har ƙarshe, ya kwashe ya faɗi. Da ya game, duk mutanen da ke kasuwa suka ce, "Allah kuwa ya tsine maka, Tanko!"

Sarki ya ce a tsire shi. Da suka gama ido da Sidi sai hawaye ya zubo wa Sidi, ya durƙusa gaban Sarki, ya ce yana roƙon arziki a yafe wa Tanko, in dai don shi ne.

Sarki ya ce, "Ai ba dama, kowa ya kashe wani lalle a kashe shi. In kai ka yarda, iyayen matarsa sun yarda ne? Ai ba sabo da laifin da ya yi maka ba ne zan kashe shi, don matarsa ce da ya kashe. Amma tun da ka roƙam masa sulhu, na yi maka. Maimakon in sa a tsire shi, zan sa a sare shi da takobi." Sarki ya dubi hauni, ya ce, "A ba ni kan wannan azzalumi."

Kafin ƙiftawa da bismilla hauni ya gama masa aiki, sai ga kai ƙasa, baki na ɗuntsar ƙasa. Allah ya kiyashe mu da cin amana, da ƙeta, da zalunci, amin!

Yara fa suka sami wani ɗa da Tanko ya bari da shakiyanci, in ya yi wata magana sai su ce masa, "Kai ar! Har kai kana da wani abin cewa? Manyan azzalumai biyu ne Allah ya halitta a duniya, daga ubanka sai kura. Mun ga iyakar ubanka, ba abin da mu ke jira kuwa yanzu sai mu ga iyakar kura. Eho, eho, eho!"

Mutane suka yi ta al'ajibin wannan haƙuri na Sidi. Za a watse sai ga Dogarawan Sirika sun zo da Dogon Yaro. Da aka gaisa da su, aka ba su abinci suka ci. Sarkin Sirika ya juya ga Dogon Yaro, ya tambaye shi ya faɗi gaskiyar abin da ya kawo shi Sirika, da sunansa na sosai, da garin da ya fito.

Dogon Yaro ya dubi Sarki, ya ce, "Tuni na gaya maka sunana Dogon Yaro, na kuma gaya maka garimmu Tsa nan gabas. Ko da na fito daga garimmu ko ban saci kayan kowa ba. To, in ka gaji da zama da ni, ba ka aika mini in yi gaba, sai ka aika a ɗauro ni? Ɗaga na zo ziyara in sami albarkacinka, ban sami albarkacinka ba, sai a ɗaure ni?"

Waziri Aku ya dube shi, ya ce, "Kai, ba surutu mu ke so ba, ka gaya mana gaskiya. Da ka fito Sarai, Sarkin Sarai ya yi maka alkawarin jaka biyar, wane umurni nasa ka yi niyya za ka cika?"

Mutane duk sai suka dubi aku, ba su san abin da ya ke nufi ba. Sai suka ga Dogon Yaro na gyara zama yana "Iye, iye, na'am, Allah ya ba ka nasara, Wallahi ƙarya ya ke yi mini."

Waziri Aku ya ce, "Ai duk asirinka a tone ya ke, da ma ka faɗi gaskiya in kana kwaɗayin ranka."

Dogon Yaro ya ce, "Wallahi tallahi ƙarya ne."

Waziri Aku ya dubi hauni, ya ce, "Fita da shi waje, ka kawo mana kansa, tun da ya ƙi faɗin gaskiya." Hauni, ya zabura ya yi sama da shi.



Dogon Yaro da ya ga na bagara sun cafe shi, sai ya ce, "Ku tsaya, ku tsaya! Wallahi zam faɗi gaskiya, tun da aka ce in na faɗi na kuɓuta. Sarkin Sarai ya ce in zo in yi ƙoƙarin kashe Sarkin Sirika, zai ba ni jaka biyar."

Waziri Aku ya ce, "Mu je mana, ba kai kaɗai ba ne. Ban da Shamakin Sirika da wa kuma aka gama kai?" Shamaki na nan zaune gaban Sarkin Sirika, ko da ya ji an ambaci sunansa sai ya miƙe tsaye da faɗa, "Ina ruwana, ina ruwana? Kai fa, ɗan akun nan, haka ka ke da gamin husuma!"

Dogon Yaro ya ce, "Wane irin gamin husuma? Da kai ciki mana, da Magatakarda tsoho, da Sarkin Zagi da aka fitar, da Hakimin Basawa."

Waziri Aku ya ce, "Mun daɗe da sanin haka. Yaya kuka ƙulla da za ku yi ku kashe shi wajen kadarkon Kogin Maikatanga?" Mutane duk suka yi zugudun suna kallo.

Dogon Yaro ya dubi aku, ya ce, "Mutane na nan, mun ajiye a bakin kadarkon da muka ji Sarki na dawowa jibi. Da ma niyyarmu, gobe da daddare su sassare ginshiƙan kadarkon su bar shi ɗagu-ɗagu, don in ya zo da mota ya rusa, in sun ga ya mutu a lokacin nan kome ya yi, sai su je su karɓi jakunkunansu wurin Sarkin Sarai, in ko sun ga bai mutu ba, su zabura kamar za su yi taimako, su iyad da shi. Abin nan da na faɗi kuwa, ko Alƙur'ani aka ba ni na saɓa, gaskiya ne."

Shamaki ya tashi da rantse-rantsen ƙarya, wai shi ba ruwansa. Nan da nan Dogarawa suka buge shi, suka ɗaure, aka fita da shi waje yana ta rantse rantsensa. Aka aika da Dogarawa maza maza a zo da Magatakarda tsoho, da Sarkin Zagi da aka fitar, da Hakimin Basawa.

Za su wuce, Waziri Aku ya ce wa Dogarai. "In kuma kun kawo kusa da kadarko Mai-katanga ku kashe wuta, ku, laɓaɓa cikin sarƙaƙiyan nan ta yamma da hanya, duk wanda kuka gani ciki ku ɗauro." Mota ta wuce, mutane suka yi kurum suna duban Waziri Aku. Sarkin Siriki ya rasa abin da zai ce wa Waziri, sai ya ƙura masa ido kawai. Can kowa ya tashi ya koma gida. Mutanen Sirika da suka fara mamakin Aku, abin sai a yi shiru.

Da gari ya waye aka sake taruwa a Majalisar Sarki Abdurrahman. Sarkin Sirika ya ce wa Waziri Aku, "Ban da gobe, jibi zan tafi gida in ga abinda ke ciki. Amma ba zam fi wata uku ba zan dawo garin nan naku."

Waziri Aku ya ce "Allah ya nufa. Amma bari im ba ka 'yan labaruruka da za su ƙayatad da kai kafin waɗannan mutane su dawo, na ga duk ħankalinka ya tashi."

Sarkin Sirika ya ce, "Hankalina ya tash mana. Don Allah ba ni labarin ko na ji dama."

Waziri Aku ya ce "T[illegible] Allah ya kyauta."

# In Maye Na Da Hankali Ba Ya Fid Da Maitarsa A Fili

A wani gari cikin ƙasar Kano an yi waɗansu mutane guda biyu, guda ana kiransa Jatau, guda ana kiransa Ɗansanda mai-ambambanta, ba su da wata sana'a sai su yiwo ice su sayar. Da ya ke sana'arsu ta zama ɗaya haka, sai suka yi abuta da juna, dare kaɗai ke raba su. Ka san mutum ba shi da wata magana sai ta sana'arsa. Saboda haka kullum ba su da wani taɗi sai na inda za su su samo itace mai ƙwari.

Suna nan haka sai ran nan matar Ɗansanda ta ce masa kada ya jira Jatau yau, ya tafi shi kaɗai ya yiwo itace wai don kullum in ya je da Jatau ba su samo abin kirki, ko sun samo ma ba su sayarwa da wuri. Ta ce Jatau ke da gashin tsiya, shi ya sa ta ke son raba su da mijinta, don kada ya goga masa.

Da safiya ta yi, Jatau ya biyo ta gidan Ɗansanda don su tafi, matar ta ce, "Ai ya yi gaba." Ya yi mamakin abin da ya sa ya wuce shi, ya rasa. Ya nufi nasa wuri. Yana cikin tafiya har ya isa daji, can ya miƙa cikin daji sai ya ga akwati a wani kogon itace, ya jawo shi ya buɗa, sai ga kuɗi cunkus, ɓarayi sun sato sun ɓoye. Ya tsaya, ya yi godiya ga Allah, ya ɗauka ya rufe da 'yan ƙirare, ya komo gida.

Da isarsa gari sai ya tasam ma gidan abokinsa Ɗansanda ya iske har ya komo, ya ba shi ajiyar kayan, don shi gidansa babu wurin ajiya. Ɗansanda ya karɓi kaya ya ajiye. Da dare matar ta ce, "Sai mu buɗa, mu ga abin da ke da nauyi a ciki haka."

Suka buɗa, sai suka ga kuɗi ƙuru-ƙuru. Da ganin haka ta ce wa mijinta, "In ya tambaye ka ka ce bai ba ka ba, ƙarya ya ke yi, duk inda za a tafi, kome wuyar da masu tuhuma suka ba ka kada ka tona, ka san bayan wuya sai daɗi. Namiji kamarka ma ai ka san ka fi ƙarfin raki."

Ya ce, "Allah ya sawwaƙa kamata ya yi raki, kin san kuwa im mun sami wannan mun warke."

Ta ce, "Mhm, kai dai yi kuruminka kawai." Suka ɓoye kaya.

Bayan kamar kwana uku sai Jatau ya zo ya ce, "Ɗansanda ina son kayan."

Ɗansanda ya ce, "Waɗanne kaya naka ka ba ni?"

Jatau ya ce, "Kai dai ƙa ka rabuwa da wasanni, don Allah ka kawo mini, sauri na ke yi."

Ɗansanda ya ce, "Wallahi ni ba ka da kaya wurina."

Jatau ya ce, "Har da Wallahinka!"

Ɗansanda ya ce, "Allah, ni ba wargi na ke yi ba. Yaya haka? Wasa-wasa abu har gaban Alƙali."

Bayan sun mai da jawabi, Alƙali ya yi binciken maganar iyakar iyawa tasa, ya ga babu wurin dafawa. Sai ya sallame su har kafin gobe.

Da gari ya waye, suka koma gidan Alƙali. Alƙali ya yi juyin duniyan nan, Ɗansanda ya ƙi faɗin gaskiya. Zai rantsad da shi, Jatau ya ce, "A ƙyale shi. Allah ya isa."

Alƙali ya ce, "To, ku tafi."

Da komowar Jatau gida sai ya yi ta ƙoƙari har ya ɗaɗɗaura wani mutummutumi na kara, ya yi masa ɗan kai da 'yan hannuwa.

Da ya gama sai ya kai shi cikin bukkarsa ya ajiye. Da ma akwai wata tsohuwar riga ta Ɗansanda a gidansa, don kun san abinsu ɗaya ne. Sai ya ɗauke ta ya sa wa mutummutumin. Ya tafi ƙauye ya nemo 'ya'yan karnuka gudu biyu, ya kawo su bukka nan ya rufe. Kullum in zai ba su abinci sai ya zuba musu bisa hannun rigar mutummutumin nan, har suka saba da shaƙar warinta, ba su da wajen wasa ma sai bisanta.

A kwana a tashi ran nan sai 'ya'yan Ɗansanda su biyu suka zo gai da Jatau abokin ubansu, yaran nan kuwa duk ba su wuce shekara biyar biyar ba. Da Jatau ya gan su sai ya kama su ya kai su wani ɗan ƙauye ya ce a tsare su, a riƙa ba su sukar in za su yi kuka. Ya dawo ya ɗauki kuyakuyan nan guda biyu, ya ruga zuwa gidan Ɗansanda, yana kuka.

Ɗansanda ya tambaye shi ya ce, "Lafiya?"

Jatau ya ce, "Ina fa lafiya, yara daga zuwa gaishe ni sai suka zama karnuka!"

Ɗansanda da matarsa suka buga ƙirji, suka ce, "Allambaran, ƙarya ya ke yi. Yaya za a yi haka, a ce mutum ya zama kare?"

Da tashin Ɗasnsanda bai zame ba sai gidan Alƙali, ya gaya masa duk abin da ya auku. Da fari Alƙali ya tasar wa musu. Nan da nan ya aika aka kira Jatau. Aka tambaye shi ya mai da jawabi.

Alƙali ya ce, "Faɗa mana gaskiya dai."

Jatau ya ce, "Gafarta malam, har wannan abin mamaki ne cikin ikon Allah, wanda ke da iko bisa kan kome, mai raya matattu, ya kashe rayayyu, mai arzutta matsiyata, ya tsiyata ma'azurta?"



Da Alƙali ya ji haka ya ce, "Hakanan ne."

Jatau ya ce, "To, in kuma kuna tsammani ƙarya na ke yi bari in kwaso 'ya'yan karnukan nan in kawo su nan.

Nan da nan ya ruga ya kwaso ya zuba su a nan tsakar mutane. Kun san halin karnuka wajen iya shaɗar wari. Da ajiye su sai suka shaƙi warin Ɗansanda, su ka koma gabansa suka ji daidai da ƙanshin mutum-mutumin nan da a ke zuba musu abinci bisa rigarsa. To, da ma suna jin yunwa, sai suka faɗa wa Ɗansanda da sunsune-sunsune, wai ko sa sami abinci yadda suka saba.

Da ganin haka sai duk Majalisa suka yi salati, kowa ya ce "Sun gane ubansu! Tsakanin ɗa da mahaifi lalle abin yana da girma."

Alƙali ya dubi Ɗansanda, ya ce, "Sai ka je ka sa malamai su yi ta yi maka roƙo, ko Allah ya sa su koma mutane." Suka sallami Alƙali. Ɗansanda ya ya kwashi karnuka a hannun riga.

Da isarsa gida sai ya gaya wa matar duk yadda aka yi, ta yi ta kuka ba ci ba sha. Mijin ya ce, "Lalle Allah-ya-isan da Jatau ya yi mana ne ya fara kama mu. Ke dai kika ce kada inba shi kuɗinsa. Ga shi abin da kika jawo mana, lalatacciyar wofi, azzaluma! Ina tare da abokina kika sa na ci amanarsa, im ba zuwa muka yi

muka mai da masa da dukiyarsa ba, muka tuba, lalle har mu ma da ƙyar im ba mu koma karnuka ba!"

Suka tashi suka ɗauki kayan Jatau duka suka ɗunguma zuwa gidansa. Suka faɗi gabansa suna ta afi, suna tuba. Ya karɓi kayansa, ya tafi ya kawo musu 'ya'yansu, ya ce. "Ga 'ya'yanku nan, mutanen wofi, masu cin amana! Da ma dabara ce na yi don in sami nawa kaya. Allah wadan ku!

Suka tashi zabu-zabu duk kunya ta rufe su, suka yi ta mamakin wannan fasaha ta Jatau. Da labari ya bazu cikin gari, duk aka tasam musu da dariya da shakiyanci, har suka kwashe kayansu, suka bar garin.

Mutane suka ce, "Kai, lalle mun saki, duk al'amarin duniya kome abin da mutum dai ke ciki lalle wani ya fi shi. Gaba da gabanta Maibaggu ya ga haƙorin Uwarzana."

Waziri na ƙare wannan labari sai ga motar Sirika ta dawo da mutanen nan da aka ce, har da waɗanda aka samu maƙe su shida ƙatta mutanen Sarai.

Da aka tambaye su da fari suka tashi yin 'yam mutsu mutsu. Da suka ga Sarkin Sirika ya fito musu ta bayan gida zai sa a yanke su, sai ɗaya daga cikinsu ya tona duk abin da aka yi. Aka zo da Dogon Yaro da Shamaki, aka sami dai duk abin da Dogon Yaro ya faɗi ya tabbata hakanan ne. Sarki Sirika ya sa aka sake ɗaure su duka, ya ce a mai da su Sirika, sai ya zo ya san abin da zai yi musu duk da ɓarayin nan. Aka ɗunguma da su.

Mutane suka dubi Waziri Aku suka yi tafi, suka durƙusa gaba ɗaya suka gaishe shi. Sarkin Sirika ya dubi Sarki Abdurrahman, ya ce, "Ni dai yanzu, Waziri kome na yi masa nan duniya na wajen godiya ban biya shi ba. Wani al'amarin ma dai ya fi gaban a yi godiya."

Labarin Waziri Aku kuma ya ƙara watsuwa cikin ƙasashe. Sarakuna suka yi haramar komawa masaukinsu. Sarkin Sirika ya ce, "Ban da gobe dai, in Allah ya so, yadda na gaya muku ɗazun, jibi fa zan tafi gida in ga abin da a ke ciki."

Kashegari yau da aka dawo Sarkin Sirika ya ce wa Waziri Aku, "Ka ce fa za ka ba mu labarai masu faranta zuciya. Ka fara wani mai daɗi jiya, don Allah ci gab kuma yau da mai daɗi irin wancan."

Waziri Aku ya ce, "Har waɗanda suka fi shi ma in kana so ka sha." Sai ya fara:

# Iya Gani Iya Kyalewa

Wata rana wani maharbi yana yawo, sai ya tarad da wani maciji dutse ya danne shi, ya yi ya yi ya ƙuɓuta, ya kasa. Da macijin nan ya ga maharbi sai ya dube shi, ya ce, "In kana ƙaunar ka gana da Ma'aikin Allah, wannan mutun, ka tsarshe ni daga halaka. Kai kuwa Allah ya saka maka da alheri."

Maharbi ya ce, "Ba fisshe ka ba na ke gudu, halinku na halittar duniya na ke jin tsoro, a yi muku rana ku kuwa ku yi wa mutum dare."

Maciji ya lanƙwasad da kai ya ce, "Subuhana lillahi, bawan Allah yaya za a fara wannan aiki? Haba, Allah ya sawaƙa!"

Maharbi ya ce, "Tun da ka yi alkawari ba ka cutata, bari in taimake ka. Ai kowa da ranarsa. Ban san inda Allah zai nufa kai kuma ka rama mini ba." Ya sa hannu ya ɗauke masa dutse. Cire dutsen nan ke da wuya, sai ya nuho shi fuu zai sare shi. Ya sa wani tsumman gwadonsa ya tsare shi, ya kai wa gwadon sara kaf. Maharbi ya ce, "Da gaske ka ke yi ko wasa? In wasa ka ke yi da ni don Allah bari, irin wannan wasa ban gane masa ba."

Maciji ya ce, "A'a' wasa fa ina? To, bari ka gani in wasa na ke yi. Kiyayyar da ke tsakanimmu da ku 'yan Adam har ɓoye ta ke? Ai ni idona idon mutum sai sara." Ya sake kai masa sari kaf, ya tare da zane.

Maharbi ya ce, "Tuna fa yadda muka yi, ka yi alkawari ba za ka cuce ni ba. Ashe haka halin 'yan duniya ya ke yanzu?"

Maciji ya ce, "A to, ko da ya ke na yi maka wannan alkawari, ai ka san da mai hankali ya ji haka daga gare ni ya san ba ta kai ciki ba, ko cikin littattafanku na mutane kuwa ma ai an yarda idan mutum ya ga macucinsa ya hallaka shi tun bai cuce shi ba. Ka san kuwa tsakanimmu da ku kamar wuta da saɓi ne, in akwai aminci.

Maharbi ya ce, "Duka abin nan da ka faɗi bisa hanya ya ke, amma ina roƙonka abu guda."

Maciji ya ce, "Mene ne? Faɗi maza in ji in na iya."

Maharbi ya ce, "Yadda ka gama ni da Allah har na yarda na

tserad da kai, ni kuma ina son kai kuma don Allah ka yarda mu shiga daji mu sami Alƙalai uku su yi mana shari'a. In sun ce shari'a ta bayar a kashe ni, ka kashe ni. In sun ce shari'a ba ta bayar a kashe ni ba, ka ƙyale ni."

Maciji ya ce ya yarda, a tafi. Ya shiga gaba, maharbi na biye. Duk abin nan maharbi ba shi da ko sanda balle baka, duk ya ajiye su cikin bukkar gonarsa. Ba shi kuma da damar ya karya, don kada maciji ya gane abin da zai ya ya riga shi.

Suna cikin tafiya sai suka gamu da wani tsohon doki. Maharbi ya bayyana masa yadda suka yi da maciji, ya kuma tambaye shi abin da ya gani a cikin wannan al'amari.

Doki ya ce, "Af, ba wani abin da na gani sai maciji ya cinye ka. Ai ku mutanen yanzu ba ku kula da a yi muku rana ku yi wa mutum dare ba. Ni da sa'an nan ina tsakar ƙarfina wajen wani Bature na ke, ya sa ni cikin sukuwa. A lokacin nan daga in ciwo masa fam hamsin sai in ciwo masa ɗari. Im mun tafi filin sukuwan nan, in na dubi nisan wurin sai in yi kamar in ƙi zuwa, sai in tuna da azabar ƙaimi da bulala. Ka san filin nan kome ƙarfin mutum, in ya yi kuwwa, na wancan gefen ba ya ji. Duk da haka sai dai in jure in yi ta gudu kamar raina zai fita, Baturen yana bisa dafa'an, sai buguna ya ke yi, yana suka kamar bawansa. In dai tattake sai na wuce saura.


"A lokacin nan fa ba ya son abin da ya taɓa ni ko kaɗan, ko ɗan haki ya gani ya liƙe mini a gashi sai ya cire mini, in na yi dauɗa ya sayi sabulu ya sa wani baƙin mutum maƙetaci ya je rafi ya yi mini wanka. Yana fita da ni sai ya haye ya je cikin daji ya yi ta sukuwa da ni a banza, wai yana more wahalarsa, don Baturen ba ya biyansa kuɗin aikinsa sosai, bayan ya gaji ya wanke ni im fita fes. Abinci kuwa sai irin wanda na ke so a ke ba ni. Ka ga duk kuɗin nan da na ke ci masa wajen sukuwa bai ishe shi ba, sai da ya sa ni cikin wani irin aikin banza, sai su hau mu, su ɗauki sanduna su riƙa bin wani makoɗi suna bugu. Im ma makoɗin nan ya sami ƙafarka sai ka yi kamar ka ce wayyo Allah don zafi. Da yawa ana cikin yi sai wani ya rauka maka sanda. Ka ga yanzu don ya ga na tsufa, ya kuwa bubbuge mini ƙwauri, ya suɗe ni sarai har ba na iya ci wajen sukuwa sai nema ya ke ya kashe ni, wai in huta ko an taɓa hutu da mutuwa? Da na ga ran nan ya jawo bindiga sai na sheƙo. Ka ji butulcin 'yan Adam."

Maciji ya ce wa mutumin, "Ka ga wannan Alƙali wajena ya ke. Mu ci gaba, mu ji na sauran biyun."

Za su wuce, doki ya ce wa maciji, "Me ka ke jira da shi? Kai dai ba ka san halin jemammen nan ba. Tsaya kaɗan in gaya maka tarihinsu. Ka san kunne ya girmi kaka." Maciji ya tsaya.

Doki ya ce, "Da sa'ad da mutane ba su gane dabarar yin gari su gina gidaje su yi benaye su shiga ciki ba, cikin dawa su ke zaune tare da kakannimmu. Abin da namun daji ke ci, shi su ke ci. Ran nan da kirinkinsu na mutane, ba sai ɗaya ya sami wani ƙaton dutse ba ya jefi ɗan manyan dawa, har ya fasa masa ido? Da manyan dawa ya ga haka ya ce namun daji su bazu, duk inda aka gan shi a kashe shi. Da kakannimmu suka ji haka, sai suka neme shi suka tsegunta masa abin da a ke ciki, don in zai ɓoye ya ɓoye. Ka san mutum ba wanda ya fi shi tsoro, sa'an nan kuma ga mugum aiki, duk sai maganan nan ta ruɗa shi, ya durƙusa kamar da lalama, ya roƙi kakannimmu su ɓoye shi, ya ɗauki alkawarin kome su ke so ya yi musu. Suka kai shi gida suka ɓoye.

"Suna nan, da ya ga kamar za a gane shi, ya rarrashe su su gudu su koma wani wuri. Suka yarda suka tashi. Ya ɗauki 'yan kayansu suka koma wani dawa, suka sami wani fili, ya nemi ganyaye ya yi musu bukkoki. Shi kuwa da sauran 'yan danginsa suka tsaya daga waje suna gadinsu. Ka ga yanzu don tsananin butulcinsu na 'yan Adam, da suka ga sun yi ƙarfi, sun kuma fi kakannimmu yawa, sai suka kore su daga cikin bukkokin nan, su suka maye. Ƙakannimmu suka so su koma su gaya wa manyan dawa, suka ga ko sun koma ba za a yarda da su ba, don kurarsu ta rigaya ta yi kuka a kan munafunci. Sabo da haka suka dangana bisa ga wannan hukuncin Allah, na gaba ya koma baya. Dubi don Allah yanzu, im ba don butulcin 'yan Adam ba, bawammu na gado ya ce wai shi zai tona mini asiri haka, har ya ɗauko bindiga wai zai harbe ni? Ka san yanzu in da abin shari'a ne, muna da iko mu sayad da 'yan Adam mu ci abinci."



Maciji ya kama hanya za su wuce, doki ya waiwayo ya ce, "Ba ka san wani abin haushi ba kuma."

Maciji ya ce, "Me?"

Doki ya ce, "Wai ashe duk ƙyale su da muka yi suna wahalshe mu, tsammani su ke tsoro ne. Ba su san mun ƙyale su don mu more su ba ne. Ka ga yanzu dole ko ana ruwa sai su fita su yiwo mana ciyawa, su yi noma su ba mu hatsin mu ci. In sun ƙi kuma mu kama su ɗai ɗai mu sayar, halal dai ne." Ya dubi mutumin nan, ya ce, "Don Allah dube shi ya yi saƙo sai ka ce mummuni, amma butulcinsa ya fi shi." Ya juya ya kama hanyarsa, yana cewa, "Ku ƙare can, an dai gaya maka gaskiya ka ƙi, wai kai son shari'a. Ka san dai kowa ya bar naman kura, ba zai sa kura ta bar nasa ba."

Maciji ya shige gabe mutum na biye, har suka tarad da wani biri kan itace. Da ganinsa maciji ya sa baki ya kira shi. Da ya zo ya kwashe duk abin da ya gudana tsakaninsa da maharbi ya gaya masa.

Biri ya ce, "Af, cikin wannan har sai ka tsaya neman Alƙali? Hala ba ka sa mutum ba. Dube shi fa da kyau ka gani. Duk duniyan nan akwai wanda ya fi mutum butulci? Ɗan'uwammu ne fa, an halicce shi da ƙafa huɗu kamarmu, don tsananin rigima ka ga yadda ya ɗage biyun na gaba, ya riƙa yawo bisa na baya. In ka dubi fuskarsa tsai, ka dubi tawa, ka ga lalle akwai dangantaka a tsakanimmu. Duk cikin dabbobi ba mai kai irin namu sai mutum. Dubi hancina da hannuwana, ka kuma dubi nasa. Amma yanzu fa tsakanimmu ba ko gaisuwa. Da manyan dawa zai yarda mu gama kammu mu faɗa wa mutane duk mu halaka su, mu shige benayen nan nasu, mu yi ta cin duniyarmu a huce." Biri ya sake duban mutum, ya ce, "Allah wadan naka ya lalace! Don Allah yaya ka ƙona gashinka haka? Ina wutsiyarka? A! Wannan akwai kirinki. Dubi fa da sunammu ɗaya biri, amma ka ga shi sai ya ce a riƙa kiransa wani abu wai shi mutum." Ya harari mutum ya ce, "Ho ɗan nema, mummunin kare mai cizo! M, kada in tsai da ku, in kana kashe shi ka kashe shi, da wani son a sani, yaji da kwarin miji. Ka ji dai an ce kashe macucinka tun bai cuce ka ba." Ya faɗa cin 'ya'yan itace abinsa.

Maciji ya dubi mutumin, ya ce, "To, yanzu fa Alƙalai biyu ke nan wajena, saurammu ɗaya a zartad da hukunci."

Idanun maharbi suka cika da ƙwalla, ya ce, "I, mu tafi gaba, Allah ya kyauta."

Suna tafe, maharbi na kirfa abin da zai yi wa maciji ya rasa. Sun ƙara gaba kaɗan sai suka gamu da kare. Da hango shi maharbi ya ce, "Ya kai, wannan kare, don Allah ka zo ka ji

wannan al'amari. Ina yawona sai na tarad da wannan maciji dutse ya danne shi, ya yi ya yi ya fita, ya kasa. Ya gama ni da Allah in taimake shi, na duƙa na cire dutse, ya fito. Ka ga da ya fito sai ya ce wai ba wanda zai sara sai ni. Don Allah fa ka ga an tasam ma gaskiya wurin nan?"

Da kare ya ji sai ya ce, "In kuna so in yi muku shari'a, sai mu koma in ga yadda ka same shi. Don bai kamata ba Alƙali ya yi shari'a sai bisa ga abin da ya kyauta ganinsa, ko kuwa ya sami adalai da suka shaida."

Mutum ya ce, "Gaskiya ne." Suka ɗunguma su duka uku zuwa wurin dutsen nan.

Da suka isa, kare ya ce wa maciji, "Kwanta yadda ya tarad da kai." Maciji ya kwanta. Ya kuma dubi mutum, ya ce, "Kai kuma mai da dutsen yadda ka tarad da shi bisansa." Maharbi ya ciccibi dutse ya jiɓa bisa maciji.

Kare ya dubi maciji, ya ce, "Haka ya same ka?"

Maciji ya ce, "I."

Kare ya ce, "To, zauna nan har Allah ya kawo maka wani wanda karambani ya yi masa yawa ya fid da kai."

Suka watse suka bar shi nan ya mutu. Maharbi ya yi ta murna bisa ga wannan hukunci na kare. Shi ya sa yanzu maharbi bai gama kowa ba da karensa, da ka bugam masa kare gwamma ka bugam masa ɗa.

Da Waziri ya ƙare wannan labari, don daɗinsa sai Sarkin Sirika ya ɗauko jaka guda ya ba shi. Da Haziƙ ya ga haka sai ya ce, "Au! Ni ma abin da ya sa aka ka da ni ai don ba a koma wajen almara ba ne."

Waziri ya ce, "Ita ka iya?"

Haziƙ ya ce, "I mana."

Waziri ya dubi Sarakunan nan ya ce, "Gobe in Allah ya so da almara za mu cika labarimmu, Allah ya ba ku nasara. Kai ko, Sarkin Sirika, in kana son labarai ka je gida ka huta ka aiko in zo har can garinka, im mun ƙare sha'anin haraji in gaya maka labarai sai ka gaji, ka ga dai su na ke, Ubangiji kuwa bai hana mini ƙwaƙwalwar tunawa ba."

Mutane suka watse, suna "Allah ya kai mu gobe."

Da aka koma gida Haziƙ ya ce wa Sarkin Sirika, "Gobe, Allah ya ba ka nasara, kana shirin ganin inda gwanin rawa zai fadi."

Sarkin Sirika ya ce, "Haziƙ, don Allah raba kanka da wuya."

Haziƙ ya ce, "In kana tsammani ba'a na ke, Allah ya kai mu goben, ai ka gani da idanunka."

Sarkin Sirika ya ce, "To, amin."

# Rana Ta Karshe

Kashegari duk mutane suka yi ta ɗokin azahar ta yi su taru a ƙofar gidan Sarki, su ga abin da zai auku ga wannan rana ta ƙarshe. Tun da rana tsaka suka taru, Sarakunan nan kuma da azahar ta yi suka zo suka ƙume bisa karagu, ana ta yi musu figini.

Da kowa ya kintsa, Sarkin Sirika ya dubi Waziri Aku, ya ce, "Bismillanku."

Waziri Aku ya dubi Haziƙ ya ce, "Kai ka san irin almarar da ka ke son yi, sai ka fara mu ji."

Haziƙ ya ce, "To, ka saurara: Bisa rai, ƙasa rai, tsaka dabara, me ke nan?"

'Mutane suka ɗauka gaba ɗaya, "Ko mu ai mun san wannan tun muna yara. Doki da sirki."

Waziri Aku ya amshe ya ce, "Da mai dokin ba?"

Haziƙ ya ce, "Da ma na fara da wannan don in ga irin kamun ludayinku ne. Amma ga wani: Wane abu ne, ga shi da rai, amma ba ya cin abinci. Im babu shi mutane sai su ga wabai, in ya yi yawa su tsane shi. Ga shi wajen faɗa yana iyaƙar ƙoƙarinsa wajen taimakon mutane, amma su ba su ƙaunarsa, kullum sai nema su ke su kashe shi."

Sauran mutane suka yi shiru, suka rasa yadda za su amsa masa. Sai Waziri Aku ya yi farat da baka ya ce, "Allah Sarki! Karamin sani ƙuƙumi. Ita ƙumbar kana tsammani ba ta cin abinci?"

Haziƙ ya fusata, ya ce, "Ka fara irin maganar taka ba? To, ina ka taɓa ganin ƙumba na cin abinci?"

Aku ya ce, "In ka ce ba ta cin abinci, to, me ya sa in mutum ya mutu ita ba ta ci gaba da girma? Jinin mutum ai shi ne abincinta."

Haziƙ ya ce, "Ka fara ba? Ina ka taɓa ganin an tone matacce, balle ka lura da ƙumbarsa?"

Waziri Aku zai ƙara ba shi misalai, sai ya tuna an ce inda jahilci ya yi kauci, sakarci ne wani ya zo ya ce zai nuna ilmi. Saboda haka ya ce, "O, gaskiyarka, na so ne in raukana. Amma na ce ko dai an amsa maka tambayar?"

Hazik ya ce, "I, tambaya dai ka karɓa."

Waziri ya ce, "To, madalla, ci gaba mu je."

Hazik ya ce, "To ga wata: Wata rana wani mutum wai shi Mainalanga ya je wajen wani malami, ya ce, "Allah ya gafarta malam, ina zaune cikin garin nan, amma duk kowa ya tsane ni saboda mugun halina. Na rasa yadda zan yi in ji dama-dama. Saboda haka ina so ka zaɓam mini ɗaya wanda ya fi im bari, don ba na iya barin biyu."

Malami ya ce, "Faɗe su mu ji."

"Mainalanga ya ce wa malamin, na faro dai yana da kwadayi, kuma ko na goye bai fi shi rowa ba. Yana sata, in kuma ana neman gwanin iya haɗa husuma tsakanin jama a, ka same shi ka huta. Ya ce makirci kuwa ko mata sa ba shi lafiya. Ga shi makaryaci. Kai, karewa ma ya ce har tsafi ya ke yi. To, cikin waɗannan wane hali ya kamata malamin nan ya ce ya bari?"

Wazirin Sirika ya ce, "Makirci." Galadiman gari ya ce, "Sata." Sarkin Sirika da Sarki Abdurrahman da alkalansu suka ce, "Tsafi.'

Waziri Aku ya yi murmushi ya ce, "Wannan ma sai an tsaya Suka tsaya, kowa ya ce shi lalle gaskiyarsa. Suka yi ta ba da 'yan dalilai.

Hazik ya dubi Waziri Aku, yana kaɗa kai wai shi ya yi abin kirki. Waziri Aku ya ce, "Ina mamakin wannan irin tambaya da ka yi yanzu mara kangado. Na ga ka fita daga cikin almara ka koma wa hadisi. Mu ko ba ka gaya mana hadisi za ka yi mana ba, balle mu zo maka da sadaka." Mutane suka fashe da dariya.

Hazik ya ce, "Je ka, an ji hadisin ne. Faɗi amsar mu ji."

Wqaziri Aku ya yi murmushi ya ce, "Wannan ma sai an tsaya wani tunani? Su ma da ka ji sun kuskure ga ba ka amsa, don ba su yi tsammani ga hadisi ka koma ba ne. Mu dai iyakar sanimmu ba abin da ya fi kyau a ce ya bari sai karya, don im ba a gama da karya ba, duk abubuwan nan da aka faɗi ba sa yiwuwa."

Hazik ya yi kus, Sarki Abdurrahman ya ce, "Ina misali? Ka tsaya da cewa ba ya yiwuwa. 'Ba ya yiwuwa' ai ba misali ba ne."

Waziri Aku ya ce, "In ji ya ce yana da rowa? To, idan an roke shi wani abu, ya ce yana da shi, kun ga alamar ya hana?"

Mutane suka ce, "A'a, ba safai ba ne zai yiwu ya hana."

Waziri Aku ya ce, "Kun ga barin karya ta sa ya bar rowa ke nan. To, kuma idan ya je sata, da isarsa zai faɗi gaskiyar abin da ya kawo shi, kun ga alamar a bari ya yi sata?"

Mutane suka ce, "A'a, lalle dai gaskiyarka."

"Kuma da matsafa suna da gaskiya, mutum ya tashi kawai yana yawo cikin daji, daga ya ga wani tsohon kwaure sai ya ɗaura

masa fari ko saƙi, ya share ƙarƙashinsa ya zuba rairaiyi ya ce shi zai bauta wa? Har ka ga wata rana in ya zo wajen kwauren nan ya koma, sai ya ce wa mutane kwaure ya ce a yi kaza a bar kaza. Gaskiya ya wannan?"

Mutane suka tafa, "Wallahi, a'a."

Waziri Aku ya dubi Haziƙ, ya ce, "Ko kuwa na yi kuskure ne?"

Haziƙ ya ce, "Ka yi daidai."

Waziri Aku ya ce, "To, sake wata tambayar."

Haziƙ ya ce, "Wallahi da ma ni iyakar tawa ka nan masu wuyar, tun da ko ka gane su duk sauran ka gane. Kai kuma tambaya mu ji." Mutane suka ɓingire da dariya.

Waziri Aku ya gyara fiffike, ya ce, "To, madalla. Ga tawa. Akwai wani azzalumin Sarki wanda shi ko yaushe wani ya yi masa laifi, in yana so ya kashe shi sai ya ba shi wani abu da ba ya yiwuwa, ya ce ya yi, in ya kasa sa'an nan sai ya sami hujjar kashe shi. Ana nan haka, ran nan sai Wazirinsa ya yi wata suɓul da baka, ya ko yi katoɓara. Aka zo aka gaya wa Sarki. Wannan Sarki kuwa ba a taɓa yi masa laifi ba ya kira mutumin da ya yi laifin ya ce "Na yafe maka' ko kuwa, "Je ka, sai ka ƙara'. Shi ba abin da ya tsare sai dai kullum da gamo da kasawa."

Haziƙ ya ce, "A'aha! Ba almara ka ce za ka gaya mana ba ne? Na ga ka tsunke a kan ba da wani labarin da ba kai ba gindi."

Dogarawa suka harari Haziƙ suka daka masa tsawa, "Yi ladab! Ba da tsaranka ka ke magana ba, da Waziri ka ke magana."

Waziri Aku ya ce, "Ku ƙyale shi, ai wasa ya ke yi." Ya dube shi ya ce, "Gajin haƙuri shi ya kawo me aka shuka."

Sarki Abdurrahman ya ce, "A'a, ai gaskiyar Haziƙ, im ba haka aka ce maka ba, har la'asar ta yi ba ka faɗi abin da za ka faɗi ba, kai kuwa ba ka bar mu mun yi tafiyarmu ba. To, don Allah faɗi abin da za ka faɗi. In kuwa labari za mu yi, mu san abin da mu ke ciki."

Waziri Aku ya ce, "Da aka tsegunta wa Sarkin nan abin da Wazirinsa ya ce, sai ya sa aka kira shi ya gaya masa ya ji abin da ya ke faɗi. Ya ce masa kuma gobe in ya fito Majalisa yana son ya tarad da Waziri ga shi tsaye, ga shi zaune, ga shi yana kuka, ga shi yana dariya, ga shi da tufa, ga shi tsirara, duk gaba ɗaya. Ya ce in kuwa ya tardad da shi cikin wani hali ba wannan da ya faɗi ba, zai kashe shi. To, wa zai iya gaya mini abin da Wazirin nan zai yi ya kuɓuta daga halaka?

Haziƙ ya ce, "Kai Waziri, ko Dujal ya zo ba ya fid da Wazirin nan daga halaka, in dai sai ya yi waɗannan zai kuɓuta. Ba wani abin da zai yi sai ya dangana ga Allah, abin da ya nufa da bawansa shi ne mai kyau."

Mutane suka ce, "Wallahi gaskiyarka, Haziƙ, ba shi da wata hanya da ta fi wannan."

Waziri Aku ya sa baki ya gyara gashinsa, ya ce, "Abin da kuka ce ba makawa gaskiya ne. Amma ku ba ni gari dai ku ji."

Sarkin Sirika ya ce, "Am ba ka."

Waziri Aku ya ce, "Abin da zai yi ya kuɓuta, sai ya yi rigar harsa ya sa ta ita kaɗai, ya sami albasa mai yaji, ya kifa turmi ya hau ya zauna, sa'an nan ya yi ta cin albasan nan yana dariya."

Haziƙ ya ce, "To, me ke nan ya yi? Ban ga hanyar kuɓuta ba ta wannan dabara."

Alƙalin Sirika ya ce, "Af, ba ku gane ba? Ai kun ga in ya zauna bisa turmi, kowa ya hango shi zai yi tsammani tsaye ya ke."

Haziƙ ya ce, "E, gaskiyarsa a wannan, amma to, mene ne kuma na cin albasa? Sarki bai ce yana son ya ji warin baki ba."

Alƙalin Sirika ya ce,s "Af, ashe kai dai ba ka da lura. In yana cin albasan nan mai yaji, ai ka san lalle ya yi hawaye. Idan kuwa an kai ga fid da hawaye, ai maganar kuka ta ƙare. Da ma mene ne kuka, in ba hawaye ba?"

Haziƙ ya yi farat ya ce, "Harsa kuwa mutum ba ya iya yin rigarta ya je kasuwa da ita kaɗai, ba wando ba bante. Ka san ko don mutum na sanye da ita kaɗai lalle tsirara ya ke."

Sauran mutane suka bushe da dariya, suka ce, "Ai ko ba ka faɗi ba wannan kowa ya sani."

Waziri Aku ya dubi Haziƙ ya ce, "Kana ɗaya. Kuma ga wata: Wata rana waɗansu mata su uku suna ɗiban ruwa, sai ga wata tsohuwa ta zo bakin rafin. Ta tsaya ta roƙe su su sam mata ruwa kaɗan ta sha. Suka ƙi ba ta. Ta yi ta yi, suka ƙi. Biyu daga cikinsu da suka ga ta dame su da roƙo sai suka hau mata da zagi. Gudar ta ce, 'Ku bar zaginta, ruwa dai ne ba mu ba ta. Im mutuwa za ta yi ta je ta mutu.'"

"Tsohuwan nan ashe tana rikiɗa, sai ta dubi matan nan ta ce, 'Duk ku rikiɗa ku zama tsiron taba.'" Ba ta rufe baki ba sai ga su duk uku sun rikiɗe, sun zama tsiron taba masu kama ɗaya a jere. Tsohuwa ta sa kai za ta wuce, sai ta tuna ɗaya daga cikinsu ta hana a zage ta. Saboda haka ta waigo ta ce wa tsiro ɗayan nan, "Ke waccan da kika hana su zage ni, na yi miki nasiha guda. Da magariba ta yi za ki zama mutum, ki je ɗakinki ki kwana. Da an yi kiran asalatu ba za ki san yadda aka yi ba, sai ki ga kin zama tsiro kin koma nan bakin rafi tare da 'yan'uwanki." Dodanniya ta tafi.

"Magariba na yi sai wannan matar ta ga ta koma mace, ta tashi ta nufi gida. Ta gaya wa mijinta duk abin da ya faru. Mijin ya yi baƙin ciki matuƙa, suka zauna kan haka. Da dare ta zama mutum, asalatu na yi ta koma tsiro kwana da kwanaki.

"Ana nan ran nan sai ta yi mafarki an ce, 'In kina so ki zama mutum ko yaushe, sai ki gaya wa mijinki da hudowar rana gobe, ɗaya ga Rajab, ya tafi bakin rafin nan ya tuge tsiron da ki ke rikiɗa. In kuwa aka kuskure wannan rana, kuma sai baɗi ta kewayo." Ko da ta gama wannan mafarki sai ta farka, ta ta da mijin ta gaya masa.

"Asalàtu na yi ta zama hure ta koma, shi kuwa mijin ko da ya ga rana ta kunno sai ya tafi bakin rafin wajen da ta yi masa kwatanci, ya tarad da tsiron taba uku yadda ta gaya masa, ga su duk kamarsu ɗaya. To, yaya zai yi ya gane matarsa?"

Sarkin Sirika ya ce, "Matarsa dai, tun da ya kuskure wannan, ai kuma sai ya haƙura sai baɗi."

Haziƙ ya ce, "Wannan magana dahir ce."

Waziri ya fashe da dariya ya ce, "To, ku ban gari in kun kasa."

Sarki Abdurrahman ya ce, "Am ba ka."

Waziri ya ce, "Sai ya shafa tsiron ya ji wanda ba shi da raɓa a gare shi, to, matarsa ke nan, sai ya tumɓuke ta." Haziƙ ya fashe da dariya, ya ce, "Me ka ke nufi da ya ji mara raɓa?"

Waziri ya ce, "Ba yanzu da asalatu suka rabu da tasa matar ba? To, ko da ya ke ta koma tsiro, ai ka san raɓa ba ta saukam mata ba, don ta gama sauka ta dawo."

Mutane suka ɗauka gaba ɗaya, "Gaskiyarka, Wazirin Wazirai!"

Waziri Aku ya dube su, ya ce "To, kuna biyu. Wace dabba ce kuma ga ta da rai, amma ba ta motsi?"

Sarki Abdurrahman ya ce, "Iyakar sanimmu ba wannan dabba nan duniya. Don dai gari mun ba ka. Faɗi mu ji."

Waziri Aku ya ce, "Kwai da aka kusa ƙyanƙyashewa."

Haziƙ ya ce, "I, hakanan ne fa. Don in ka fasa shi ɗan tsako za ka gani da rai ko? Amma duk da haka ba a taɓa ganin ƙwai na ɓingira ba." Mutane suka rasa ta cewa.

Waziri Aku ya ce, "Kuna uku. Wata rana kuma wani Sarki ya tsani mutanen wani ɗan ƙauye, sai ya kira su, yana so ya kashe su, amma ya rasa dalilin da zai bayar. Sabo da haka ya ce musu kafin wata guda su gina masa gida cikin hawa, ba da ko sun sa wani abu sun kare shi ba. So ya ke gidan dai ya yi ta lilo kamar tsuntsu. In kuwa sun kasa duk zai kashe su. To, jama'a, ko wani ya san hanyar da za su bi su kuɓuta daga wannan halaka?"

Sarkin Sirika ya ce, "Wace hanya kuma a ke nema ga waɗannan, Waziri? Da ma su halakakku ne, tun da aka ce musu haka."

Waziri aku ya ce, "To, ku ba ni gari, mu gani ko ma iya sama musu mafita."

Sarki Abdurrahman ya ce, "Am ba ka."

Waziri ya ce, "Sai su cẹ masa ya shata musu su ga yadda za su sa harsashin, mu gani in ya shata."

Mutane suka ɓarke da dariya, "Ha!" Suka ce, "Wallahi, Waziri, ba maganin Sarkin nan sai haka, in dai ya iya shatawa, su kuwa sa gina."

Waziri ya ce, "To, kuna huɗu. Ga na biyar: Da aka fara daga ɗaya, aka yi biyu, aka yi uku, aka yi huɗu, aka yi biyar, aka yi shida, sai aka yi me?"

Haziƙ ya yi farat ya ce, "Sai aka yi bakwai."

Waziri Aku ya ɓingire da dariya har yana hawaye don wannan amsar Haziƙ.

Sarkin Sirika ya ce, "To, mun ba ka gari."

Waziri Aku ya ce, "Allah ya ba ku nasara, ku yafe ni. Wannan na sa mala. Daga nan ko har iyakar raina wanda duk ya gano amsar wannan tambaya ya kawo gare ni, na ga daidai ne, zam ba shi jaka guda."

Mutane suka yi ta tafi gaba ɗaya raf raf raf, suna cire wa Waziri Aku hula ya yi fas. Sarkin Sirika ya ce, "Yanzu sai a daina haka, mu je mu kinkintsa don gobe mu tashi da wuri." Ya kawo jaka biyar na kuɗi ya ba Waziri Aku, shi kuma Waziri ya cire guda ya ba Haziƙ. Ya ɗauki kuma guda, ya bayar a rarraba wa gajiyayyu cikin gari sadaka.

Za a watse, sai Sarkin Sirika don ya yi dariya ya ce wa Waziri, "Waɗannan labarai da aka bayar, ni dai da ka ƙare mini su da waƙa da abin ya fi shero ni. Ni dai na kan sọ in ji muryan nan taka mai zaƙi."

Waziri Aku ya ce, "Kash, ina ko mura yau. Amma duk da haka yanzu ka sha ta." Ya karkace kai, ya shiga gonarsa:

Bismillah zan yabe ka Allah!
Haliƙu Allah muna yabonka,
Ka ba mu ilmin tsirar tsara.
Haba mutane, ku daina ruba,
Bin ga Allah ya ƙaddare shi,
Kowa saɓa ya sama gaula.
Haba shakiyai, ku bar butulci,
Ku daina wargi ku kama hanya.
Nai gaba, ba kwa mai mai son baya.
Haziƙu, kunya ta bar biyarka,
Abin ga Allah ya ƙaddare shi,
Ikon Allah kowa yaj ja.
Ina da kyawun gani da tsari,

Ga ni da wayo har da fasaha,
   Ga ni da ilmi tsintsa-tsintsa.
Abin da na ce ba fahari ba,
Yabo na ke yi gunka Muhamman,
   Mu sami hanyar neman girma.
Sirika, Wallahi na yabe ka,
Idan da fari ka yi fushi ne,
   Ga ni a durƙushe na zo tube.
Tabara ƙai ne ka ɗaukake ni,
In wani sauna yai mini sharri.
   Ka mai da niyyatai can baya.
Akwai sharari, akwai bahili,
Akwai shakiyi, akwai namimi,
   Allah kai ne ka san kowa.
Tabara Allah ka taimake mu,
Ka shafe laifin da munka aika,
   Ka ba mu ikon neman tsira!

NNPC